# MUSULUNCI

## TAQAITACCEN BAYANI GAME DA MUSULUNCI KAMAR YADDA YA ZO A CIKIN QUR'ANI DA SUNNAR MANZON ALLAH



نبذة موجزة عن الإسلام (مشتملة على الأدلة) هوسا

بيان الإسلام
Bayan AL-Islam

ⓒجمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات ، ١٤٤٦هـ

جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات
الإسلام - نبذة موجزة عن الإسلام (مشتملة على الأدلة) - هوسا.
/ جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات ؛ جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات - ط١. .- الرياض ، ١٤٤٦هـ

١٦٠ ص ؛ ..سم

رقم الإيداع: ١٤٤٦/٢٥٨٦
ردمك: ٩٧٨-٦٠٣-٨٤٧٤-٠٦-٨

Partners in Implementation

Content Association

Rowad Translation

Rabwah Association

IslamHouse

This publication may be printed and disseminated by any means provided that the source is mentioned and no change is made to the text.

Tel: +966 50 244 7000
info@islamiccontent.org
Riyadh 13245- 2836
www.islamhouse.com

# MUSULUNCI

TAQAITACCEN BAYANI GAME DA MUSULUNCI KAMAR YADDA YA ZO A CIKIN QUR'ANI DA SUNNAR MANZON ALLAH

Littafi ne mai muhimmanci wanda ya qunshi bayani game da Musulunci da yake bayanin mafi muhimmancin tushensa da koyarwarsa da kyawawunsa wanda aka samo su daga tushe na asali shi ne Al-Kur'ani mai girma da kuma Sunnar Annabi da kuma saqon da aka turashi zuwa ga baki dayan baligai na musulmai da yarukansu a kowane lokaci da kuma ko ina suke duk da sabanin yanayi da kuma hali
(Kwafi ne da yake qunshe da dalilai daga cikin Al-qur'ani mai girma da kuma Sunnar Annabi)

## 1-Musulunci shi Saqon Allah zuwa ga mutane baki dayan su shi ne saqon Allah wanzajje

Musulunci shi ne saqon Allah ga mutane baki dayan su Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا كَآفَّةٗ لِّلنَّاسِ بَشِيرٗا وَنَذِيرٗا وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ ٢٨﴾[سبأ: 28]

{Kuma ba Mu aika ka ba fãce zuwa ga mutãne gabã ɗaya, kanã mai bãyar da bushãra kuma mai gargaɗi, kuma amma mafi yawan mutãne ba su sani ba} (Saba'i: 28) Allah Madaukakin Sarki ya ce:

﴿قُلۡ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنِّي رَسُولُ ٱللَّهِ إِلَيۡكُمۡ جَمِيعًا ...١٥٨﴾[الأعراف: 158]

{Ya ku mutane ni manzon Allah ne zuwa gare ku baki daya} [Al-a'araf: 158] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدۡ جَآءَكُمُ ٱلرَّسُولُ بِٱلۡحَقِّ مِن رَّبِّكُمۡ فَـَٔامِنُواْ خَيۡرٗا لَّكُمۡۚ وَإِن تَكۡفُرُواْ فَإِنَّ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ١٧٠﴾[النساء: 170]

{Yã kũ mutãne! Haƙĩƙa, Manzo yã je muku da gaskiya daga Ubangijinku. Sabõda haka ku yi ĩmãni yã fi zama alhẽri a gare ku. Kuma idan kun kãfirta, to, Allah Yanã da abin da ke cikin sammai da ƙasa. Kuma Allah Yã kasance Masani, Mai hikima} [al-Nisa'a: 170] Musulunci shi ne Saqon Allah dawwamamme kuma shi ne cika makin Saqon Ubangiji, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٖ مِّن رِّجَالِكُمۡ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٗا ٤٠﴾[الأحزاب: 40]

{Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance Manzon Allah kuma cikon Annabãwa. Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme} [al-ahzab: 40].

**2. Kuma Musulunci ba Addinin wasu kebantattun mutane ba ne ko jinsi a'a Addinin Allah ne ga mutane baki dayansu**

Kuma Musulunci ba Addinin wasu kebantattun mutane bane a'a Addinin Allah na mutane baki dayansu, kuma farkon umarni a cikin Al-Qur'ani mai girma shi ne fadin Allah - Madaukakin sarki -:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٢١﴾﴾[البقرة: 21]

{Yã ku mutãne! Ku bauta wa Ubangjinku, Wanda Ya halicce ku, kũ da waɗanda suke daga gabãninku, tsammãninku ku kãre kanku!} [al-Baqara:21] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱتَّقُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُم مِّن نَّفْسٍ وَٰحِدَةٍ وَخَلَقَ مِنْهَا زَوْجَهَا وَبَثَّ مِنْهُمَا رِجَالًا كَثِيرًا وَنِسَآءً ۚ وَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ ٱلَّذِى تَسَآءَلُونَ بِهِۦ وَٱلْأَرْحَامَ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ كَانَ عَلَيْكُمْ رَقِيبًا ﴿١﴾﴾

{Ya ku Mutane kuji tsoron Ubangijinku wanda Ya halicce ku daga rai kwara daya kuma Ya halitta masa rai kuma ya waatsa daga cikinsu maza da mata} [al-nisa'a: 1] Kuma an rawaito daga Ibn Umar - Allah Ya yarda da su - cewa Manzon Allah - SAW - ya yi huduba ga mutane ranar bude Makka sai ya ce: "Ya ku mutane lallai Allah Ya kawar muku da haukan Jahilci da jiji da kai da iyaye saboda haka mutane sun kasu biyu: Mai biyayya ga Allah kuma mai tsoronSa mai girma a wajen Allah, da kuma fajiri tababbe wulakance a wajen Allah, dukkan 'Yan Adam kuma Allah Ya halicci Annabi Adam daga tabo, Allah Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقۡنَٰكُم مِّن ذَكَرٖ وَأُنثَىٰ وَجَعَلۡنَٰكُمۡ شُعُوبٗا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْۚ إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٞ ١٣﴾[الحجرات: 13]

{Ya ku Mutane lallai mun halicce ku daga Namiji fa Mace kuma muka sanya ku Jama'a da Qabilu don ku san juna lallai mafi tsoron Allah a cikin ku shi ne mafi tsoron Allah, lallai Allah Masani ne kuma mai bada labara} [al-hujrat: 13] Tirmizi ne ya rawaito shi (3270) Kuma ba zaku samu ba a cikin umarnin Al-Qurani mai girma da umarnin manzon Allah - SAW - wani hukunci da ya kebe wasu mutane ko kungiya saboda kawai Jininsu ko don kabilar su ko jinsinsu.

**3-Musulunci shi ne Saqon Allah wanda ya zo don cika Saqonnin Annabawa da Manzanni wadanda suka gabata -amincin Allah ya tabbata a gare su- zuwa ga al-ummansu**

Musulunci shi ne Saqon Allah wanda ya zo don cika saqonnin Annabawa da Manzanni wadanda suka gabata - amincin Allah ya tabbata a gare su - zuwa ga al’ummansu, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞ إِنَّآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ كَمَآ أَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ نُوحٖ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ مِنۢ بَعۡدِهِۦۚ وَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَعِيسَىٰ وَأَيُّوبَ وَيُونُسَ وَهَٰرُونَ وَسُلَيۡمَٰنَۚ وَءَاتَيۡنَا دَاوُۥدَ زَبُورٗا ١٦٣﴾[النساء: 163]

{Lalle ne Mu, Mun yi wahayi zuwa gare ka, kamar yadda Muka yi wahayi zuwa ga Nũhu da annabãwa daga bãyansa. Kuma Mun yi wahayi zuwa ga Ibrãhĩma da Ismã'ĩla da Is'hãƙa da Yaƙũbu da jĩkõki da ĩsa da Ayũba da Yũnusa da Hãruna da Sulaimãn. Kuma Mun bai wa Dãwũda zabũra} [Al-Nisaa: 163] Kuma wannan Addinin wanda Allah Allah Yayi wahayinsa ga Manzon Allah - SAW - shi ne Addini wanda Allah Ya shar'anta

ga Annabawa da suka gabata kuma yayi musu wasiyya da shi, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿۞ شَرَعَ لَكُم مِّنَ ٱلدِّينِ مَا وَصَّىٰ بِهِۦ نُوحًا وَٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ وَمَا وَصَّيۡنَا بِهِۦٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَمُوسَىٰ وَعِيسَىٰٓۖ أَنۡ أَقِيمُواْ ٱلدِّينَ وَلَا تَتَفَرَّقُواْ فِيهِۚ كَبُرَ عَلَى ٱلۡمُشۡرِكِينَ مَا تَدۡعُوهُمۡ إِلَيۡهِۚ ٱللَّهُ يَجۡتَبِيٓ إِلَيۡهِ مَن يَشَآءُ وَيَهۡدِيٓ إِلَيۡهِ مَن يُنِيبُ ١٣﴾[الشورى: 13]

{Ya shar'anta muku, game da addini, abin da Ya yi wasiyya da shi ga Nũhu da abin da Muka yi wahayi da shi zuwa gare ka, da abin da Muka yi wasiyya da shi ga Ibrãhĩm da Mũsã da Ĩsã, cẽwa ku tsayar da addini sõsai kuma kada ku rarrabu a cikinsa. Abin da kuke kira zuwa gare shi, ya yi nauyi a kan mãsu shirki. Allah na zãɓen wanda Yake so zuwa gare Shi, kuma Yanã shiryar da wanda ke tawakkali gare Shi, ga hanyarSa} [al-shura:13] Kuma wannan Addinin wanda Allah Yayi wahayinsa ga Manzon Allah - SAW - shine Addini wanda Allah Ya shar'anta ga Annabawan da suka gabata kuma Yayi musu wasiyya da shi, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَٱلَّذِيٓ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ هُوَ ٱلۡحَقُّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِۗ إِنَّ ٱللَّهَ بِعِبَادِهِۦ لَخَبِيرُۢ بَصِيرٞ ٣١﴾[فاطر: 31]

{Kuma abin da Muka yi wahayi zuwa gare ka, daga Littãfi, shi ne gaskiya mai gasgata abunda ya gabace shi lallai Allah mai bada labari ne ga Bayinsa kuma mai hani} [Fadir: 31].

### 4. Annabawa Amincin Allah a gare su Addininsu daya ne kuma shari'unsu sun sha banban

Addinin Annabwa - amincin Allah a garesu - daya ne sai dai shari'unsu ne suka sassaba, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَمُهَيۡمِنًا عَلَيۡهِۖ فَٱحۡكُم بَيۡنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُۖ وَلَا تَتَّبِعۡ أَهۡوَآءَهُمۡ عَمَّا جَآءَكَ مِنَ ٱلۡحَقِّۚ لِكُلّٖ جَعَلۡنَا مِنكُمۡ شِرۡعَةٗ وَمِنۡهَاجٗاۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن لِّيَبۡلُوَكُمۡ فِي مَآ ءَاتَىٰكُمۡۖ فَٱسۡتَبِقُواْ ٱلۡخَيۡرَٰتِۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرۡجِعُكُمۡ جَمِيعٗا فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ٤٨﴾[المائدة: 48]

{Kuma Mun saukar da Littãfi zuwa gare ka da gaskiya yanã mai gaskatãwa ga abin da yake a gaba gare shi daga Littãfi (Attaura da Injĩla), kuma mai halartãwa a kansa sai ka yi hukunci a tsakãninsu da abin da Allah Ya saukar kuma kada ka bĩbiyi son zũciyõyiniu daga abin da ya zo maka daga gaskiya Ga kõwanne daga gare ku Mun sanya sharĩa da hanya (ta bin ta) Kuma dã Allah Yã so, dã Yã sanya ku al'umma guda, kuma amma dõmin Ya jarraba ku a cikin abin da Ya bã ku Sai ku yi tsere ga ayyukan alheri Zuwa ga Allah makõmarku take gabã ɗaya Sa'an nan Ya bã ku lãbãri ga abin da kuka kasance kunã sãɓãwa a cikin sa} [al-Ma'ida: 48] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ni ne mafi cancantar mutane da Isa dan Maryam a duniya da lahira, kuma Annabawa ‘yan uwan juna ne ‘yan uba, sai dai iyayensu maza daban daban Amma Addinisu daya ne". Bukhari ne ya rawaito shi (3443)

**5,Musulunci yana kira -Kamar yadda kowane Annabi yayi: Nuhu da Ibrahim da Musa, da Sulaiman, da Daud, da Isa - amincin Allah a gare su- zuwa ga imani cewa Ubangiji kadai Shi ne Allah wanda Yayi halitta kuma Mai rayawa Mai kashewa Mai Mulki Mamallaki, kuma Shine wanda Yake gudanar da al’amura, kuma Shine Mai jin kai Mai tausasasawa**

Musulunci yana kira -kamar yadda kowane Annabi yayi: Nuhu, da Ibrahim, da Musa, da Sulaiman, da Daud, da Isa - amincin Allah a gare su- zuwa ga imani cewa Ubangiji kadai

Shine Allah wanda Yayi halitta kuma Mai rayawa Mai kashewa Mai Mulki Mamallaki, kuma Shine wanda Yake gudanar da al'amura, kuma Shine Mai jin kai Mai tausasasawa, Yã kũ mutãne! Ku tuna ni'imar Allah a kanku.

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱذۡكُرُواْ نِعۡمَتَ ٱللَّهِ عَلَيۡكُمۡۚ هَلۡ مِنۡ خَٰلِقٍ غَيۡرُ ٱللَّهِ يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۖ فَأَنَّىٰ تُؤۡفَكُونَ ٣﴾[فاطر: 3]

{Shin, akwai wani mai halitta wanin Allah da zai azurta ku daga sama da, ƙasã? Bãbu wani abin bautãwa, fãce Shi. To, yãya ake karkatar da ku?} [Fadir: 3] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce: Ka ce:

﴿قُلۡ مَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ أَمَّن يَمۡلِكُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَمَن يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَۚ فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُۚ فَقُلۡ أَفَلَا تَتَّقُونَ ٣١﴾[يونس: 31]

{Wãne ne Yake azurtã ku daga sama da ƙasa? Shin kõ kuma Wãne ne Yake mallakar jĩ da ganĩ, kuma Wãne ne Yake fitar da mai rai daga mamaci, kuma Ya fitar da mamaci daga mai rai, Kuma Wãne ne Yake shirya al'amari?" To, zã su ce: "Allah ne." To, ka ce: "Shin fa, bã zã ku yi taƙawa ba?} [Yunus: 31] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce: {Kõ wãne ne yake fã ra halitta sa'an nan kuma ya mayar da ita, kuma Wãne ne Ya azurta ku daga sama da ƙasa? Ashe, akwai wani abin bautãwa tãre da Allah?} Ka ce:

﴿أَمَّن يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَمَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِۗ أَءِلَٰهٌ مَّعَ ٱللَّهِۚ قُلۡ هَاتُواْ بُرۡهَٰنَكُمۡ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٦٤﴾[النمل: 64]

{Ku kãwo dalĩlinku idan kun kasance mãsu gaskiya} al-Naml: 64] Kuma baki dayan Annabawa da Manzanni - amincin Allah a

gare su- an aiko su ne da da'awa zuwa ga bautar Allah Shi kadai, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ هَدَى ٱللَّهُ وَمِنۡهُم مَّنۡ حَقَّتۡ عَلَيۡهِ ٱلضَّلَٰلَةُۚ فَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٣٦﴾[النحل: 36]

{Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun aika a cikin kõwace al'umma da wani Manzo (ya ce): "Ku bauta wa Allah, kuma ku nĩsanci ¦ãgũtu." To, daga gare su akwai wanda Allah Ya shiryar, kuma daga cikinsu akwai wanda ɓata ta wajaba a kansa. Sai ku yi tafiya a cikin ƙasa, sa'an nan ku dũba yadda ãƙibar mãsu ƙaryatãwa ta kasance} [al-Nahl: 36] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ٢٥﴾[الأنبياء: 25]

{Kuma ba Mu aiki wani Manzo ba a gabãninka fãce Munã yin wahayi zuwa gare shi, cẽwa "Lalle ne Shi, bãbu abin bautãwa fãce Nĩ, sai ku bauta Mini} [al-Anbiyaa: 25] Sai Allah Ya bada labari game da Annabi Nuhu -Amincin Allah a gare shi- da cewa:

﴿لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا نُوحًا إِلَىٰ قَوۡمِهِۦ فَقَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥٓ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ٥٩﴾[الأعراف: 59]

{Mutãnẽna! Ku bauta waAllah! Bã ku da wani abin bautãwa waninSa. Lalle ne nĩ, inã yimuku tsõron azãbar wani Yini mai girma} [al-A'araf: 59] Kuma badadayiin Allah Annabi Ibrahim - amincin Allah a gare shi- cewa shi ya ce:

﴿وَإِبۡرَٰهِيمَ إِذۡ قَالَ لِقَوۡمِهِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱتَّقُوهُۖ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ١٦﴾

{Da Ibrãhĩm a lõkacin da ya ce wa mutãnensa, "Ku bautã wa Allah ku bĩ Shi da taƙawa. Wannan Shĩ ne alhẽri a gare ku idan kun kasance kunã sani} [al-Ankabut: 16] Kuma Annabi Salihu - amincin Allah a gareshi - ya ce:

﴿وَإِلَىٰ ثَمُودَ أَخَاهُمْ صَٰلِحًاۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥۖ قَدْ جَآءَتْكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْۖ هَٰذِهِۦ نَاقَةُ ٱللَّهِ لَكُمْ ءَايَةًۖ فَذَرُوهَا تَأْكُلْ فِيٓ أَرْضِ ٱللَّهِۖ وَلَا تَمَسُّوهَا بِسُوٓءٍ فَيَأْخُذَكُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٧٣﴾[الأعراف: 73]

Kamar yadda Allah ya bada labarinsa Ya ce: {Yã mutãnena! Ku bauta wa Allah; bã ku da wani abin bauta wa wanninSa. Haƙĩƙa hujja bayyananniya tã zo muku daga Ubangijinku! wannan rãƙumar Allah ce, a gare ku, wata ãyã ce. Sai ku bar ta ta ci, a cikin ƙasar Allah, kuma kada ku shãfe ta da wata cũta har azãba mai raɗaɗi ta kãmã ku} [al-Aaraf: 73] Kuma Annabi Shuaibu - amincin Allah a gareshi- ya ce:

﴿وَإِلَىٰ مَدْيَنَ أَخَاهُمْ شُعَيْبًاۚ قَالَ يَٰقَوْمِ ٱعْبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنْ إِلَٰهٍ غَيْرُهُۥۖ قَدْ جَآءَتْكُم بَيِّنَةٌ مِّن رَّبِّكُمْۖ فَأَوْفُواْ ٱلْكَيْلَ وَٱلْمِيزَانَ وَلَا تَبْخَسُواْ ٱلنَّاسَ أَشْيَآءَهُمْ وَلَا تُفْسِدُواْ فِي ٱلْأَرْضِ بَعْدَ إِصْلَٰحِهَاۚ ذَٰلِكُمْ خَيْرٌ لَّكُمْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ٨٥﴾[الأعراف: 85]

{Kamar yadda Allah ya bada labarin sa "Ya mutãnena! Ku bauta wa Allah; bã ku da wani abin bauta wa waninSa. Lalle ne, wata hujja bayyananniya daga Ubangijinku tã zõ muku! Sai ku cika mũdu da sikeli kumakada ku nakasa wa mutãne kãyansu, kuma kada ku yi fasãdi a cikin ƙasa a bãyan gyaranta. Wannan ne mafi alhẽri a gare ku, idan kun kasance mũminai} [al-A'araf: 85] Kuma farkon wanda Allah Yayi magana da shi shi ne Annabi Musa - amincin Allah a gare shi- Allah - Madakaki - Ya ce:

﴿وَأَنَا ٱخۡتَرۡتُكَ فَٱسۡتَمِعۡ لِمَا يُوحَىٰٓ ١٣ إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدۡنِي وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ ١٤﴾[طه: 13-14]

{Kuma Nĩ Nã zãɓe ka. Sai ka saurãra ga abin da ake yin wahayi.(13) "Lalle, Nĩ Ni ne Allah. Bãbu abin bautawa fãce Ni. Sai ka bauta Mini, kuma ka tsayar da salla dõmin tuna Ni(14)} [Daha: 13-14] Kuma Allah Ya ce Yana bada labarin Annabi Musa - amincin Allah a gareshi-cewa shi ya nemi tsari da Allah sai ya ce:

﴿وَقَالَ مُوسَىٰٓ إِنِّي عُذۡتُ بِرَبِّي وَرَبِّكُم مِّن كُلِّ مُتَكَبِّرٖ لَّا يُؤۡمِنُ بِيَوۡمِ ٱلۡحِسَابِ ٢٧﴾ [غافر: 27]

{Kuma Mũsã ya ce: "Lalle nĩ, nã nẽmi tsari da Ubangijĩna kuma Ubangijinku, daga dukan makangari, wanda bã ya ĩmani da rãnar Hisãbi} [Ghafir: 27] Sai Allah Ya bada labari game da Annabi Isa-amincin Allah a gare shi- da cewa:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ ٥١﴾[آل عمران: 51]

{Lallai Allah ne Ubangijina kuma Ubangijinku, sai ku bauta Masa. Wannan shi ne tafarki madaidaici} [Aal Imran: 51] Sai Allah Ya bada labari game da Annabi Annabi Isa- amincin Allah a gare shi- har wa yau da cewa:

﴿لَقَدۡ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ مَرۡيَمَۖ وَقَالَ ٱلۡمَسِيحُ يَٰبَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمۡۖ إِنَّهُۥ مَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ ٱلۡجَنَّةَ وَمَأۡوَىٰهُ ٱلنَّارُۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ ٧٢﴾[المائدة: 72]

{Ya ku Banu Isra'ila ku bautawa Allah Ubangiji na kuma Ubangijinku hakika duk wanda ya hada shi da abokin tarayya haqiqa Allah ya haramta masa Aljannah sannan mokomarsa wuta kuma Azzalumai basu da Mai taimako} [al-Ma'ida: 72] Kai

har a Al-taura da linjila qarfafawa ta zo a cikinsu kan bautar Allah shi kadai saboda ya zo cikin Sifr Al-Tathniya fadin Annabi Musa - amincin Allah a gare shi- fadinsa (Ka ji ya kai Isra'il Ubangiji Shi ne Ubangijinmu ubangiji qwara daya) Kuma karfafawa kan Tauhidi ta zo a cikin Linjila cewa Marqus lokacin da yake cewa da Annabi Isa - amncin Allah a gareshi- (Lallai farkon abunda wasiyya ta qunsa su ne: Ka ji ya kai Isra'il Ubangiji shi ne Ubangijinmu ubangiji qwara daya) Kuma Allah Yana bayyanawa cewa baki dayan Annabawa an aikosune da wannan Sako mai girma shi ne kira zuwa ga kadaita Allah, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce: {Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun aika a cikin kõwace al'umma da wani Manzo (ya ce):

﴿وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ فَمِنۡهُم مَّنۡ هَدَى ٱللَّهُ وَمِنۡهُم مَّنۡ حَقَّتۡ عَلَيۡهِ ٱلضَّلَٰلَةُۚ فَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَٱنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلۡمُكَذِّبِينَ ٣٦﴾[النحل: 36]

{Ku bauta wa Allah, kuma ku nĩsanci ¦ãgũtu." To, daga gare su akwai wanda Allah Ya shiryar, kuma daga cikinsu akwai wanda ɓata ta wajaba a kansa} [al-Nahl: 36] kuma Allah - Madaukaki - Ya ce Ka ce:

﴿قُلۡ أَرَءَيۡتُم مَّا تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِي مَاذَا خَلَقُواْ مِنَ ٱلۡأَرۡضِ أَمۡ لَهُمۡ شِرۡكٞ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِۖ ٱئۡتُونِي بِكِتَٰبٖ مِّن قَبۡلِ هَٰذَآ أَوۡ أَثَٰرَةٖ مِّنۡ عِلۡمٍ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٤﴾[الأحقاف: 4]

{Shin, kun gani, abin da kuke kira, wanda yake baicin Allah? Ku nũna mini, menene suka halitta daga ƙasa? Kõ kuwa sunã da tãrayya a cikin sammai? Ku zo mini da wani littãfi na gabãnin wannan (Alƙur'ãni) kõ wata alãma daga wani ilmi, idan kun

kasance mãsu gaskiya} [al-Ahqaf: 4] Shiekh Al-si'ady -Allah Yayi masa rahama ya ce: (saboda an sani cewa jayayyar mushirikai a cikin shirkarsu bai dogara kan wasu hujjoji ba ko dalili, kadai ya dogara ne kan zato na karya, da batattun tunanuka da hankula gurbatattu abunda zai nuna maka gurbatarsu bibiyar halayensu da ilimansu da ayyukansu da duba halin wadanda suka karar da rayuwarsu a bautarSa shin ya anfane su (ai abubuwan da suke bautawa koma bayan Allah) da wani abu a duniya ko a lahira? ) [Taisiru Karimu Al-mannan: 779]

**6: Allah - Madaukakin Sarki - Shi ne wanda Yayi halitta kuma Shi ne wanda Ya cancanci ibada shi kadai, kuma ba'a bautawa kowa waninsa tare da shi**

Allah shi ne wanda Ya cancanci a bauta masa shi kadai, kuma ba'a bauta maSa tare da wani, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعْبُدُوا۟ رَبَّكُمُ ٱلَّذِى خَلَقَكُمْ وَٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ﴿٢١﴾ ٱلَّذِى جَعَلَ لَكُمُ ٱلْأَرْضَ فِرَٰشًا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءً وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءً فَأَخْرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزْقًا لَّكُمْ ۖ فَلَا تَجْعَلُوا۟ لِلَّهِ أَندَادًا وَأَنتُمْ تَعْلَمُونَ ﴿٢٢﴾﴾[البقرة: 22-21]

{Yã ku mutãne! Ku bauta wa Ubangjinku, Wanda Ya halicce ku, kũ da waɗanda suke daga gabãninku, tsammãninku ku kãre kanku! (21) Wanda Ya sanya muku ƙasa shimfiɗa, kuma sama gini, kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sa'an nan Ya fitar da abinci daga 'ya'yan itãce game da shi, sabõda ku. Sabõda haka kada ku sanya wa Allah wasu kĩshiyõyi, alhãli kuwa kuna sane (22)} [al-Baqara: 21-22] Saboda wanda Ya halicce mu kuma Ya halicci tsaraikun da suka gabace mu kuma Ya sanya kasa shinfida a gare mu kuma Ya saukar mana da ruwa daga sama sai Ya futar

mana da 'ya'yan itatuwa arziqi a garemu; to shi ne wanda Ya cancanci da bauta shi kadai, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱذْكُرُوا۟ نِعْمَتَ ٱللَّهِ عَلَيْكُمْ ۚ هَلْ مِنْ خَـٰلِقٍ غَيْرُ ٱللَّهِ يَرْزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلْأَرْضِ ۚ لَآ إِلَـٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ فَأَنَّىٰ تُؤْفَكُونَ ۝٣﴾ [فاطر: 3]

{Yã kũ mutãne! Ku tuna ni'imar Allah a kanku. Shin, akwai wani mai halitta wanin Allah da zai azurta ku daga sama da, ƙasã? Bãbu wani abin bautãwa, fãce Shi. To, yãya ake karkatar da ku?} [Fadir: 3] Saboda wanda Yayi halitta kuma Yake azurtata Shine wanda Ya cancanci Ibada shi kadai kuma Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمْ ۖ لَآ إِلَـٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ خَـٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ فَٱعْبُدُوهُ ۚ وَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ وَكِيلٌ ۝١٠٢﴾ [الأنعام: 102]

{Wancan ne Allah Ubangijinku. Bãbu wani abin bautãwa fãce Shĩ, Mahaliccin dukan kõme. Sabõda haka ku bauta Masa kuma Shi ne wakĩli a kan dukan, kõme} [al-An'am: 102] Kuma duk abunda aka bautawa koma bayan Allah to bai cancanci bauta ba; saboda bai iya mallakar kwayar zarra ba a sammai ko a kasa kuma shi ba abokin tarayya ba ne a cikin wani abu ko kuma mai taimako ko mai agazawa Allah saboda me to za'a kirawo tare da Allah ko a sanya masa abokin tarayya, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قُلِ ٱدْعُوا۟ ٱلَّذِينَ زَعَمْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ ۖ لَا يَمْلِكُونَ مِثْقَالَ ذَرَّةٍ فِى ٱلسَّمَـٰوَٰتِ وَلَا فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا لَهُمْ فِيهِمَا مِن شِرْكٍ وَمَا لَهُۥ مِنْهُم مِّن ظَهِيرٍ ۝٢٢﴾ [سبأ: 22]

{Ka ce: "Ku kirãyi waɗanda kuka riya (cẽwa abũbuwan bautãwa ne) baicin Allah, bã su Mallakar ma'aunin zarra a cikin sammai, kuma bã su Mallakarsa a cikin ƙasa kuma bã su da wani rabon tãrẽwa a cikinsu (sammai da ƙasa), kuma bã Shi da

wani mataimaki daga gare su} [Saba'i: 22] Kuma Allah - SWT - Shine wanda Ya halicci wadan nan Halittun kuma Ya samar da su daga babu kuma samuwarsu yana nuna samuwarSa da AllantakarSa, Allah - Madaukaki Ya ce:

﴿وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنۡ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ إِذَآ أَنتُم بَشَرٞ تَنتَشِرُونَ ٢٠ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنۡ خَلَقَ
لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ أَزۡوَٰجٗا لِّتَسۡكُنُوٓاْ إِلَيۡهَا وَجَعَلَ بَيۡنَكُم مَّوَدَّةٗ وَرَحۡمَةًۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ
يَتَفَكَّرُونَ ٢١ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ خَلۡقُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَٱخۡتِلَٰفُ أَلۡسِنَتِكُمۡ وَأَلۡوَٰنِكُمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَٰتٖ لِّلۡعَٰلِمِينَ ٢٢ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ مَنَامُكُم بِٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ وَٱبۡتِغَآؤُكُم مِّن فَضۡلِهِۦٓۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ
لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَسۡمَعُونَ ٢٣ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦ يُرِيكُمُ ٱلۡبَرۡقَ خَوۡفٗا وَطَمَعٗا وَيُنَزِّلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ
فَيُحۡيِۦ بِهِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَآۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَٰتٖ لِّقَوۡمٖ يَعۡقِلُونَ ٢٤ وَمِنۡ ءَايَٰتِهِۦٓ أَن تَقُومَ ٱلسَّمَآءُ
وَٱلۡأَرۡضُ بِأَمۡرِهِۦۚ ثُمَّ إِذَا دَعَاكُمۡ دَعۡوَةٗ مِّنَ ٱلۡأَرۡضِ إِذَآ أَنتُمۡ تَخۡرُجُونَ ٢٥ وَلَهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۖ كُلّٞ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ٢٦ وَهُوَ ٱلَّذِي يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهۡوَنُ عَلَيۡهِۚ وَلَهُ ٱلۡمَثَلُ
ٱلۡأَعۡلَىٰ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٢٧﴾ [الروم: 20-27]

{Kuma akwai daga ãyõyinSa, Ya halitta ku daga turɓãya, sai gã ku kun zama mutum, kunã wãtsuwa. (20) Kuma akwai daga ãyõyinsa, Ya halitta muku mãtan aure daga kanku, dõmin ku natsu zuwa gare ta, kuma Ya sanya sõyayya da rahama a tsakãninku. Lalle a cikin wancan akwai ãyõyi ga mutãne mãsu yin tunãni.(21). Kuma akwai daga ãyõyinSa halittar sammai da ƙasã da sãɓã, war harsunanku, da launukanku. Lalle a cikin wannan akwai ãyõyi ga mãsu ilmi. (22) Kuma akwai daga cikin ãyõyinSa, barcinku a cikin dare da rãna, da nẽmanku ga falalarsa. Lalle a cikin wannan akwai ãyõyi ga mutãne mãsu saurãrãwa.(23) Kuma akwai daga cikin ãyõyinSa, Ya nũna muku walƙiya a kan tsõro da ɗammãni kuma Ya dinga saukar da ruwa

daga sama Sa'an nan Ya rãyar da ƙasã game da shi a bãyan mutuwarta. Lalle a cikin wannan akwai ãyõyi ga mutãne mãsu hankaltawa.(24) Kuma akwai daga ãyõyinsa, tsayuwar sama da asƙã bisa umurninsa, sa'an nan idan Ya kira ku, kira ɗaya, daga ƙasã, sai gã ku kunã fita.(25) Kuma wanda ke cikin sammai da ƙasã Nãsa ne shi kaɗai. Dukansu mãsu tawãli'u ne a gare Shi.(26) Kuma shine ke fara yin halitta ,sa'annan ya sake ta kuma sakewar tafi sauki a gare shi] [al-rum: 20-27] Namarudu ya musanta samuwar Ubangijinsa sai Annabi Ibrahin ya ce da shi kamar yadda Allah Ya bada labarinsa:

﴿أَلَمۡ تَرَ إِلَى ٱلَّذِي حَآجَّ إِبۡرَٰهِـۧمَ فِي رَبِّهِۦٓ أَنۡ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُ ٱلۡمُلۡكَ إِذۡ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ رَبِّيَ ٱلَّذِي يُحۡيِۦ وَيُمِيتُ قَالَ أَنَا۠ أُحۡيِۦ وَأُمِيتُۖ قَالَ إِبۡرَٰهِـۧمُ فَإِنَّ ٱللَّهَ يَأۡتِي بِٱلشَّمۡسِ مِنَ ٱلۡمَشۡرِقِ فَأۡتِ بِهَا مِنَ ٱلۡمَغۡرِبِ فَبُهِتَ ٱلَّذِي كَفَرَۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٢٥٨﴾[البقرة: 258]

{Ibrahin ya ce to lallai Allah Yana futo da rana daga gabas to kai ka zo da ita daga yamma sai aka rinjayi wanda ya kafirta kuma Allah baYa shiryar da mutane azzalumai} [al-Baqara: 258] Kuma haka ne Annabi Ibrahim - amincin Allah a gare shi - ya kafa dalili ga mutanensa cewa Allah Shine wanda Ya shiryar da shi kuma Ya ciyar da shi kuma Ya shayar da shi kuma idan yayi rashin lafiya Yake warkar da shi kuma Shine wanda Yake kashe shi kuma Ya raya shi sai Ya ce:

﴿ٱلَّذِي خَلَقَنِي فَهُوَ يَهۡدِينِ ٧٨ وَٱلَّذِي هُوَ يُطۡعِمُنِي وَيَسۡقِينِ ٧٩ وَإِذَا مَرِضۡتُ فَهُوَ يَشۡفِينِ ٨٠ وَٱلَّذِي يُمِيتُنِي ثُمَّ يُحۡيِينِ ٨١﴾[الشعراء: 78-81]

kamar yadda Allah Ya bada labari game da shi {Wanda Ya halitta ni, sa'an nan Yanã shiryar da ni."(78) "Kuma Wanda Yake Shĩ ne Yake ciyar da ni, kuma Yanã shãyar da ni."(79) "Kuma idan na yi jiyya, to, Shĩ ne Yake warkar da ni."(80)

"Kuma wanda Yake matar da ni, sa'an nan Ya rãyar da ni(81)} [al-Shu'ara'a: 78-81], Kuma Allah - Madaukakin sarki - Ya bada labarin Annabi Musa cewa shi yayi jayayya da Fir'auna yana mai cewa: Ubangijinsa shi ne:

﴿قَالَ رَبُّنَا ٱلَّذِيٓ أَعۡطَىٰ كُلَّ شَيۡءٍ خَلۡقَهُۥ ثُمَّ هَدَىٰ ٥٠﴾[طه: 50]

{Shi ne wanda ya bawa kowane abu halittarAa sannan kuma Ya shiryar} [Daha: 50] Kuma Allah Ya horewa baki dayan abunda ke cikin sammai da kasa ga mutum, kuma Ya kewa shi da ni'amomi; don ya bautawa Allah kuma kada ya kafirce masa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿أَلَمۡ تَرَوۡاْ أَنَّ ٱللَّهَ سَخَّرَ لَكُم مَّا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ وَأَسۡبَغَ عَلَيۡكُمۡ نِعَمَهُۥ ظَٰهِرَةٗ وَبَاطِنَةٗۗ وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يُجَٰدِلُ فِي ٱللَّهِ بِغَيۡرِ عِلۡمٖ وَلَا هُدٗى وَلَا كِتَٰبٖ مُّنِيرٖ ٢٠﴾[لقمان: 20]

{Ashe, ba ku gani ba, cẽwa Allah Yã hõre muku abin da ke a cikin sammai da abin da ke a cikin ƙasã, kuma Ya zuba ni'imõminsa a kanku, bayyanannu da ɓõyayyu? Kuma akwai daga mutãne wanda ke yin jidãli ga al'amarin Allah, bã da wani ilmi ba, kuma bã da wata shiriya ba, kumã ba da wani littãfi mai haskakãwa ba} [Luqman: 20] Kuma kamar yadda Allah Ya sauwake duk abunda ke sammai da kasa to haqiqa shi Ya halicce su kuma shi Ya tanadar musu da duk abunda suke buqata naji da kuma gani da zuciya don su koyi Ilimin da zai musu anfani kuma ya nuna musu Ubangijinsu da Mahaliccinsu, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَٱللَّهُ أَخۡرَجَكُم مِّنۢ بُطُونِ أُمَّهَٰتِكُمۡ لَا تَعۡلَمُونَ شَيۡـٔٗا وَجَعَلَ لَكُمُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَٱلۡأَفۡـِٔدَةَ لَعَلَّكُمۡ تَشۡكُرُونَ ٧٨﴾[النحل: 78]

{Kuma Allah ne Ya fitar da ku daga cikunan iyãyenku, ba da kunã sanin kõme ba, kuma Ya sanya muku ji da gannai da zukãta, tsammãninku zã ku gõde} [al-nahl: 78]

Saboda Allah - SWT - haqiqa Ya halicci baki dayan wadan nan duniyoyi kuma Ya halicci dan Adam kuma Ya tanadar masa baki dayan abunda yake buqata na gabbai sannan kuma Ya qare shi da duk abunda zai taimaka masa kan tsayuwa da bautar Allah da raya kasa sannan Ya hore masa dukkan abunda ka sammai da kasa.

Kuma Allah Ya kafa dalili ga halittarSa da wadan nan halittu masu girma, kan AllantakarSa wacce take ta wajibi daga AllantakarSa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿قُلۡ مَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ أَمَّن يَمۡلِكُ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡأَبۡصَٰرَ وَمَن يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَمَن يُدَبِّرُ ٱلۡأَمۡرَۚ فَسَيَقُولُونَ ٱللَّهُۚ فَقُلۡ أَفَلَا تَتَّقُونَ ٣١﴾[يونس: 31]

{Ka ce: "Wãne ne Yake azurtã ku daga sama da ƙasa? Shin kõ kuma Wãne ne Yake mallakar jĩ da ganĩ, kuma Wãne ne Yake fitar da mai rai daga mamaci, kuma Ya fitar da mamaci daga mai rai, Kuma Wãne ne Yake shirya al'amari?" To, zã su ce: "Allah ne." To, ka ce: "Shin fa, bã zã ku yi taƙawa ba?} [Yunus: 31] Kuma Allah - Madaukaki - Ya ce: Ka ce:

﴿قُلۡ أَرَءَيۡتُم مَّا تَدۡعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِي مَاذَا خَلَقُواْ مِنَ ٱلۡأَرۡضِ أَمۡ لَهُمۡ شِرۡكٞ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِۖ ٱئۡتُونِي بِكِتَٰبٖ مِّن قَبۡلِ هَٰذَآ أَوۡ أَثَٰرَةٖ مِّنۡ عِلۡمٍ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ٤﴾[الأحقاف: 4]

{Shin, kun gani, abin da kuke kira, wanda yake baicin Allah? Ku nũna mini, menene suka halitta daga ƙasa? Kõ kuwa sunã

da tãrayya a cikin sammai? Ku zo mini da wani littãfi na gabãnin wannan (Alƙur'ãni) kõ wata alãma daga wani ilmi, idan kun kasance mãsu gaskiya} [al-ahqaf: 4] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ بِغَيۡرِ عَمَدٖ تَرَوۡنَهَاۖ وَأَلۡقَىٰ فِي ٱلۡأَرۡضِ رَوَٰسِيَ أَن تَمِيدَ بِكُمۡ وَبَثَّ فِيهَا مِن كُلِّ دَآبَّةٖۚ وَأَنزَلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجٖ كَرِيمٍ ١٠ هَٰذَا خَلۡقُ ٱللَّهِ فَأَرُونِي مَاذَا خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦۚ بَلِ ٱلظَّٰلِمُونَ فِي ضَلَٰلٖ مُّبِينٖ ١١﴾[لقمان: 10-11]

{Ya halicci sammai ba tare da turaku ba da kuke iya ganinsu kuma Ya jefa Duwatsu a bayan kasa saboda kada ta raurawa da ku kuma ya yada kowace irin dabba a cikinta kuma Ya saukar da ruwa daga sama sai muka futar a cikinta kowane abu mace da namiji masu daraja, kuma wannan ita ce halittar Allah to kununa mun abunda wadan da suke koma bayanSa suka halitta ba haka bane azzalumai dai suna bata bayyananne} [Luqman: 10-11] Kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿أَمۡ خُلِقُواْ مِنۡ غَيۡرِ شَيۡءٍ أَمۡ هُمُ ٱلۡخَٰلِقُونَ ٣٥ أَمۡ خَلَقُواْ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۚ بَل لَّا يُوقِنُونَ ٣٦ أَمۡ عِندَهُمۡ خَزَآئِنُ رَبِّكَ أَمۡ هُمُ ٱلۡمُصَيۡطِرُونَ ٣٧﴾[الطور: 35-37]

{Shin, an halitta su ne bã daga kõme ba, kõ kuwa sũ ne mãsu yin halitta?(35) Shin, sun halitta sammai da ƙasa ne? Ã'a ba su dai yi ĩmãnin yaƙĩni ba.(36). Shin, taskõkin Ubangijinka, sunã a wurinsu ne? Kõ kuwa sũ ne mãsu rinjãya? (37)} [al-Dur: 35-37] Shiek Al-Si'adi ya ce: (Kuma wannan kafa dalilin akan su da umarni da ba zai yi musu ba sai mika wuya ga gaskiya ko kuma futa daga abunda zai tabbatar da hankali da addini) Tafsir Ibn Al-Si'adi:816.

**7: Allah shi ne Mahalicci ga baki dayan halitta abunda muke iya gani da wadan da bama iya gani, kuma duk wani abu da ba shi ba to shi abun halitta ne da cikin halittunSa, kuma shi Ya halicci sammai da kasa cikin kwana shidda**

Allah Shine Mahalicci ga baki dayan halitta abunda muke iya gani da wadan da bama iya gani, kuma duk wani abu da ba Shi ba to shi abun halitta ne da cikin halittunSa, kuma Shine Ya halicci sammai da kasa cikin kwana shida ka ce:

﴿قُلْ مَن رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ قُلِ ٱللَّهُ ۚ قُلْ أَفَٱتَّخَذْتُم مِّن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءَ لَا يَمْلِكُونَ لِأَنفُسِهِمْ نَفْعًا وَلَا ضَرًّا ۚ قُلْ هَلْ يَسْتَوِى ٱلْأَعْمَىٰ وَٱلْبَصِيرُ أَمْ هَلْ تَسْتَوِى ٱلظُّلُمَٰتُ وَٱلنُّورُ ۗ أَمْ جَعَلُوا۟ لِلَّهِ شُرَكَآءَ خَلَقُوا۟ كَخَلْقِهِۦ فَتَشَٰبَهَ ٱلْخَلْقُ عَلَيْهِمْ ۚ قُلِ ٱللَّهُ خَٰلِقُ كُلِّ شَىْءٍ وَهُوَ ٱلْوَٰحِدُ ٱلْقَهَّٰرُ ١٦﴾[الرعد: 16]

{Wãne ne Ubangijin sammai da ƙasa?" Ka ce: "Allah". Ka ce: "Ashe fa, kun riƙi waɗansu masõya baicin Shi, waɗanda ba su mallaka wa kansu wani amfãni ba kuma haka bã su tũre wata cũta?" Ka ce: "Shin makãho da mai gani sunã daidaita? Kõ shin duhu da haske sunã daidaita? ko sun sanya ga Allah waɗansu abõkan tãrayya waɗanda suka yi halitta kamar halittarSa sa'an nan halittar ta yi kama da jũna a gare su?" Ka ce: "Allah ne Mai halitta kõme kuma Shĩ ne Maɗaukaki, Marinjãyi} [al-ra'ad: 16] Kuma Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿...وَيَخْلُقُ مَا لَا تَعْلَمُونَ ٨﴾[النحل: 8]

{Kuma yana halittar abunda baku sani ba} [al-Nahl: 8] Kuma Ya halicci sammai da kasa cikin kwanaki shida, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿هُوَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ ثُمَّ ٱسْتَوَىٰ عَلَى ٱلْعَرْشِ ۚ يَعْلَمُ مَا يَلِجُ فِى ٱلْأَرْضِ وَمَا يَخْرُجُ مِنْهَا وَمَا يَنزِلُ مِنَ ٱلسَّمَآءِ وَمَا يَعْرُجُ فِيهَا ۖ وَهُوَ مَعَكُمْ أَيْنَ مَا كُنتُمْ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ بَصِيرٌ ٤﴾[الحديد: 4]

{Shĩ ne wanda Ya halitta sammai da ƙasa a cikin wasu kwãnuka shida, sa'an nan Ya daidaitu a kan Al'arshi, Yanã sanin abin da ke shiga cikin ƙasa da abin da ke fita daga gare ta, da abin da ke sauka daga sama da abin da ke hawa cikinta, kuma Shĩ yanã tareda ku duk inda kuka kasance. Kuma Allah Mai gani ne ga abin da kuke aikatãwa} [al-hadid: 4] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَلَقَدْ خَلَقْنَا ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا فِى سِتَّةِ أَيَّامٍ وَمَا مَسَّنَا مِن لُّغُوبٍ ٣٨﴾[ق: 38]

{Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun halitta sammai da ƙasã da abin da ke a tsakãninsu, a cikin kwãnaki shida, alhãli wata'yar wahala ba ta shãfe Mu ba} [Q: 38]

**8-Kuma Allah - Madaukakin sarki - baShi da abokin tarayya a cikin mulkinSa da halittunSa ko bayinSa**

Kuma Allah - Madaukakin sarki - Shine Mamallaki wanda baShi da abokin tarayya a cikin halittarSa ko mulkinSa ko gudanarwarSa, Ka ce:

﴿قُلْ أَرَءَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَرُونِى مَاذَا خَلَقُوا۟ مِنَ ٱلْأَرْضِ أَمْ لَهُمْ شِرْكٌ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ ۖ ٱئْتُونِى بِكِتَٰبٍ مِّن قَبْلِ هَٰذَآ أَوْ أَثَٰرَةٍ مِّنْ عِلْمٍ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ٤﴾[الأحقاف: 4]

{Shin, kun gani, abin da kuke kira, wanda yake baicin Allah? Ku nũna mini, menene suka halitta daga ƙasa? Kõ kuwa sunã da tãrayya a cikin sammai? Ku zo mini da wani littãfi na gabãnin wannan (Alƙur'ãni) kõ wata alãma daga wani ilmi, idan kun kasance mãsu gaskiya} [al-ahqaf: 4] Shiekh Al-si'ady -Allah

Ya yi masa rahama - Ya ce: Ai ka ce da wadan nann da suke shirka da Allah wasu gumaka da kishiyoyi wadanda ba su Mallaki wani anfani ko cutarwa a gare su ba ko mutuwa ko rayuwa ko kuma tashi daga kabari to ka ce musu kana mai bayyana musu gajiyawar gumakan na su kuma cewa su basu cancanci da a bauta musu ba (ka nunamun abunda suka halitta a bayan kasa ko kuma suna da abokan tarayya a cikin sammai) ko sun halicci wasu daga cikin burujan sama da kasa? ko kuma sun halicci koramai? ko sun samar da dabbobi? ko sun tsirar da bishiyoyi? ko kuma suna da masu taimaka musu a tare da su akan wani abu na halitta da cikin hakan? babu wani abu daga cikin wancan da iqirarin su akan su, ga kuma na wasun su to wannan shi ne dalilin hankali mai yankan hanzari kan cewa kowane abu koma bayan Allah bautarsa batacciya ce. Sannan ya fadi koruwar dalili na nassi sai ya ce: (To kuzo mun da wani littafi kafin wannan) littafin da yake kira kan shirka (Ko kuma wani abunda aka gada na Ilimi) wanda aka gada daga manzanni da suke umarni da hakan kuma abu ne sananne cewa su gajiyayyu ne kan cewa su zo da wani abu daya daga manzanni da dalilin da yake nuna wancan 'A'a dai muna yankewa kuma munsakankace cewa baki dayan manzanni sunyi kira ne zuwa kadaita Ubangijin su kuma ya hane su ga barin shirka da Shi kuma Shine mafi girman abunda aka samo daga gare su na Ilimi) Tafsir Ibn Al-Si'adi:779. Kuma Allah - Madaukakin sarki - Shine Mamallakin mulki ba shi da abokin tarayya a cikin mulkinSa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce: Ka ce:

﴿قُلِ ٱللَّهُمَّ مَٰلِكَ ٱلۡمُلۡكِ تُؤۡتِي ٱلۡمُلۡكَ مَن تَشَآءُ وَتَنزِعُ ٱلۡمُلۡكَ مِمَّن تَشَآءُ وَتُعِزُّ مَن تَشَآءُ وَتُذِلُّ مَن تَشَآءُۖ بِيَدِكَ ٱلۡخَيۡرُۖ إِنَّكَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٢٦﴾[آل عمران: 26]

{Yã Allah Mamallakin mulki, Kanã bayar da mulki ga wanda Kake so, Kanã zãre mulki daga wanda Kake so, kuma Kanã buwãyar da wanda Kake so, kuma Kanã ƙasƙantar da wanda Kake so, ga hannunKa alhẽri yake. Lalle ne Kai, a kan kõwane abu, Mai ĩkon yi ne} [Aal Imran: 26] Kuma Allah - Madaukakin Sarki - Ya bayyana cewa cikakken mulki naSa ne a ranar Al-qiyama

﴿يَوۡمَ هُم بَٰرِزُونَۖ لَا يَخۡفَىٰ عَلَى ٱللَّهِ مِنۡهُمۡ شَيۡءٞۚ لِّمَنِ ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَۖ لِلَّهِ ٱلۡوَٰحِدِ ٱلۡقَهَّارِ ١٦﴾[غافر: 16]

{ Rãnar da suke bayyanannu, bãbu wani abu daga gare su wanda yake iya bõyuwa ga Allah, Mulki ga wa ya ke a yau?" Yana ga Allah, Makaɗaici, Mai tĩlastãwa} [Ghafir: 16] Kuma Allah - Madaukakin Sarki - baShi da abikin tarayya a cikin mulkinSa da halittunSa ko bayinSa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَقُلِ ٱلۡحَمۡدُ لِلَّهِ ٱلَّذِي لَمۡ يَتَّخِذۡ وَلَدٗا وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٞ فِي ٱلۡمُلۡكِ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ وَلِيّٞ مِّنَ ٱلذُّلِّۖ وَكَبِّرۡهُ تَكۡبِيرَۢا ١١١﴾[الإسراء: 111]

{Kuma ka ce: Gõdiyã ta tabbata ga Allah wanda bai riƙi ɗã ba kuma abõkin tãrayya bai kasance a gare Shi ba a cikin mulkinSa, kuma wani masõyi sabõda wulãkancin bai kasance a gare Shi ba." Kuma ka girmama Shi, girmamãwa} [al-Isra'a: 111] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ٱلَّذِي لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَمۡ يَتَّخِذۡ وَلَدٗاوَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٞ فِي ٱلۡمُلۡكِ وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖ فَقَدَّرَهُۥ تَقۡدِيرٗا ٢﴾[الفرقان: 2]

{wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa kuma bai riƙi abin haihuwa ba, kuma abõkin tãrayya bai kasance a gare Shi ba a cikin mulkinSa kuma Ya halitta dukan kowane abu, sa'an nan Ya ƙaddara shi ƙaddarãwa} (al-Furqan: 2) To shi ne Mai mulki kuma

duk abunda yake ba Shi ba to abun mallaka ne a gare shi - SWT - kuma Shine Mai halitta kuma duk abnda yake ba Shi ba to shi halitta ne a gare Shi, kuma Shine mai gudanar da al'amari kuma duk wanda ya kasance wannan ne sha'aninsa to ya wajaba a bauta masa kuma bautar waninsa tawaya ce a cikin hankali da kuma shirka duniya da lahira Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَقَالُواْ كُونُواْ هُودًا أَوۡ نَصَٰرَىٰ تَهۡتَدُواْۗ قُلۡ بَلۡ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِـۧمَ حَنِيفٗاۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٣٥﴾[البقرة: 135]

{Kuma suka ce: "Ku kasance Yahũdãwa ko Nasãra, kwã shiryu."Ka ce: "A'a aƙidar Ibrãhĩm dai, maikarkata, zuwa ga gaskiya, kuma bai kasance cikin mãsu shirki ba} [al-Baqara: 135] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَنۡ أَحۡسَنُ دِينٗا مِّمَّنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ وَٱتَّبَعَ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۗ وَٱتَّخَذَ ٱللَّهُ إِبۡرَٰهِيمَ خَلِيلٗا ١٢٥﴾[النساء: 125]

{Kuma wãne ne ya fi kyau ga addini daga wanda ya sallama fuskarsa ga Allah, alhãli kuwa yanã mai kyautatawa kuma ya bi aƙidar Ibrãhĩm, Yanã mai karkata zuwa ga gaskiya? Allah Yã riƙi Ibrãhĩm badãɗayi} [al-Nisa'a: 125] Kuma Allah - Madaukakin sarki - Ya bayyana cewa duk wanda yabi wanin tafarkin Annabi Ibrahin ba dadayin Allah - amincin Allah a gare shi- to haqiqa ya wawaitar da kansa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَن يَرۡغَبُ عَن مِّلَّةِ إِبۡرَٰهِـۧمَ إِلَّا مَن سَفِهَ نَفۡسَهُۥۚ وَلَقَدِ ٱصۡطَفَيۡنَٰهُ فِي ٱلدُّنۡيَاۖ وَإِنَّهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٣٠﴾[البقرة: 130]

{Kuma wãne ne yake gudu daga aƙĩdar Ibrãhĩm, fãce wanda ya jãhilta ga ransa? Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun zãɓe shi, a cikin

dũniya, kuma lalle ne shi, a cikin Lãhira, haƙĩƙa, yana daga sãlihai} [al-Baqara: 130].

**9. Allah - Madaukakin Sarki - bai haifa ba kuma ba'a haifeShi ba kuma baShi wani kini ko mai kamanceceniya da Shi**

Allah - Madaukakin Sarki - bai haifa ba kuma ba'a haifeShi ba kuma baShi wani kini ko mai kamanceceniya da Shi, Allah - Madauakaki - Ya ce:

﴿قُلۡ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ١ ٱللَّهُ ٱلصَّمَدُ ٢ لَمۡ يَلِدۡ وَلَمۡ يُولَدۡ ٣ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدُۢ ٤﴾[الإخلاص: 1-4]

{Ka ce: Shi ne Allah Makaɗaĩci."(1) Alla shi ne abun nufi da Buqata (2) "Bai haifa ba, kuma ba a haife Shi ba."(3) "Kuma babu ɗaya da ya kasance kini a gare Shi(4)} [al-Ikhlas: 1-4] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿رَّبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَا فَٱعۡبُدۡهُ وَٱصۡطَبِرۡ لِعِبَٰدَتِهِۦۚ هَلۡ تَعۡلَمُ لَهُۥ سَمِيًّا ٦٥﴾[مريم: 65]

{Shi ne Ubangijin sammai da ƙasa da abin da yake a tsakãninsu. sai ka bauta Masa, kuma ka yi haƙuri ga bautarsa. Shin kã san wani takwara a gare shi?} [Maryam: 65] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿فَاطِرُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ جَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ أَزۡوَٰجًا وَمِنَ ٱلۡأَنۡعَٰمِ أَزۡوَٰجًا يَذۡرَؤُكُمۡ فِيهِۚ لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٌۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ ١١﴾[الشورى: 11]

{(Shĩ ne) Mai ƙãga halittar sammai da ƙasa, Ya sanya muku ma'aura daga jinsinku, kuma (Ya sanya) daga dabbõbi maza da mãtã, Yanã halitta ku a cikinsu, wani abu bai zama kamar tamkarSa ba, kuma Shĩ ne Mai ji, Mai gani} [al-shura:11].

## 10. Allah - Madaukakin Sarki - baYa sauka a cikin wani abu, ko kuma Ya saje da jikin wani abu daga cikin halittunSa

Kuma Shi Allah - SWT - baYa sauka cikin wani jiki kuma baYa kamanceceniya da wani daga cikin halittarSa kuma baya hadewa da komai, wancan saboda Allah Shine Mahalicci kuma duk abunda yake ba Shi ba abin halitta ne, kuma Shine wanzajje kuma duk wanda yake koma bayansa makomarsa shi ne qarewa, kuma kowane abu mulkinSa ne kuma Shine mamallakinSa saboda haka babu wani abu da Allah Yake sauka a cikinsa daga cikin halittarSa kuma babu wani daga cikin halittarSa da yake sauka cikin zatinSa Madauakaki, Kuma Allah - SWT - Shine mafi girman komai kuma mafi girma daga komai Allah - Madaukaki - Yana cewa Yana mai musantawa wadanda suka riya cewa Allah Ya sauka cikin Annabi Isa:

﴿لَّقَدْ كَفَرَ ٱلَّذِينَ قَالُوٓاْ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلْمَسِيحُ ٱبْنُ مَرْيَمَۚ قُلْ فَمَن يَمْلِكُ مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا إِنْ أَرَادَ أَن يُهْلِكَ ٱلْمَسِيحَ ٱبْنَ مَرْيَمَ وَأُمَّهُۥ وَمَن فِى ٱلْأَرْضِ جَمِيعًاۗ وَلِلَّهِ مُلْكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَاۚ يَخْلُقُ مَا يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ١٧﴾[المائدة: 17]

{ Lalle haƙĩka waɗanda suka ce:Lalle Allah Shĩ ne Masĩhu ɗan Maryama," sun kãfirta. Ka ce: "To, wane ne ke iya mallakar wani abu daga Allah, idan Yã nufi Ya halakar da Masĩhu ɗanMaryama da uwarsa da wanda yake a cikin ƙasa gabã ɗaya?" Kuma Allah ne da mallakar sammai da ƙasa da abin da ke a tsakãninsu, Yanã halitta abin da Yake so. Kuma Allah a kan dukkan kõme, Mai ĩkon yi ne} [al-Ma'ida:17] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَلِلَّهِ ٱلۡمَشۡرِقُ وَٱلۡمَغۡرِبُۚ فَأَيۡنَمَا تُوَلُّواْ فَثَمَّ وَجۡهُ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ وَٰسِعٌ عَلِيمٞ ١١٥ وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱللَّهُ وَلَدٗاۗ سُبۡحَٰنَهُۥۖ بَل لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ كُلّٞ لَّهُۥ قَٰنِتُونَ ١١٦ بَدِيعُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَإِذَا قَضَىٰٓ أَمۡرٗا فَإِنَّمَا يَقُولُ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ١١٧﴾[البقرة: 115-117]

{Kuma Allah ɗai yake da gabas da yamma sabõda haka, inda duk aka jũyar da ku, to, a can fuskar Allah take. Lalle ne, Allah Mawadãci ne, Mai ilmi.(115) Kuma suka ce: "Allah Yã riƙi ɗã." Tsarki yã tabbata a gare Shi! A'a, Shi ne da abin da yake a cikin sammai da ƙasa, dukansu, a gare Shi, mãsu ƙanƙan da kai ne.(116) Mai kyautata halittar sammai da ƙasa, kuma idan Ya hukunta wani al'amari, sai kawai Ya ce masa: "Kasance." Sai ya yi ta kasancewa.(117)} [al-baqara:115-117] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَقَالُواْ ٱتَّخَذَ ٱلرَّحۡمَٰنُ وَلَدٗا ٨٨ لَّقَدۡ جِئۡتُمۡ شَيۡـًٔا إِدّٗا ٨٩ تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرۡنَ مِنۡهُ وَتَنشَقُّ ٱلۡأَرۡضُ وَتَخِرُّ ٱلۡجِبَالُ هَدًّا ٩٠ أَن دَعَوۡاْ لِلرَّحۡمَٰنِ وَلَدٗا ٩١ وَمَا يَنۢبَغِي لِلرَّحۡمَٰنِ أَن يَتَّخِذَ وَلَدًا ٩٢ إِن كُلُّ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ إِلَّآ ءَاتِي ٱلرَّحۡمَٰنِ عَبۡدٗا ٩٣ لَّقَدۡ أَحۡصَىٰهُمۡ وَعَدَّهُمۡ عَدّٗا ٩٤ وَكُلُّهُمۡ ءَاتِيهِ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ فَرۡدًا ٩٥﴾[مريم: 88-95]

{Kuma suka ce Allah ya riqi xa" (88) Lalle ne haƙĩƙa kun zo da wani abu mai girman mũni.(89) Sammai sunã kusa su tsattsage sabõda shi, kuma ƙasa ke kẽce kuma duwãtsu su faɗi sunã karyayyu.(90) Saboda sun sanyawa Allah Xa (91) Alhãli bã ya kamata ga Mai rahama ya riƙi wani ɗã.(92) Dukkan wanda yake a cikin sammai da ƙasa bai zama ba fãce mai jẽ wa Mai rahama ne yanã bãwã.(93) Lalle ne haƙĩƙa Yã lissafe su, kuma ya ƙidãye su, ƙidãya.(94) Kuma dukan kõwanensu mai jẽ Masa ne a Rãnar ¡iyãma yanã shi kaɗai.(95)} [Maryam: 88-95] kuma

﴿ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡحَيُّ ٱلۡقَيُّومُۚ لَا تَأۡخُذُهُۥ سِنَةٞ وَلَا نَوۡمٞۚ لَّهُۥ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۗ مَن ذَا ٱلَّذِي يَشۡفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦۚ يَعۡلَمُ مَا بَيۡنَ أَيۡدِيهِمۡ وَمَا خَلۡفَهُمۡۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَيۡءٖ مِّنۡ عِلۡمِهِۦٓ إِلَّا بِمَا شَآءَۚ وَسِعَ كُرۡسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفۡظُهُمَاۚ وَهُوَ ٱلۡعَلِيُّ ٱلۡعَظِيمُ ٢٥٥﴾ [البقرة: 255]

Allah Madaukaki ya ce: {Allah, bãbu wani Ubangiji fãce Shi, Rãyayye, Mai tsayuwa da kõme, gyangyaɗi bã ya kãma Shi, kuma barci bã ya kãma Shi, Shi ne da abin da yake a cikin sammai da abin da yake a cikin ƙasa. Wane ne wanda yake yin cẽto a wurinSa, fãce da izninSa? Yana sanin abin da yake a gaba gare su da abin da yake a bãyansu. Kuma bã su kẽwayẽwa da kõme daga ilminSa, fãce da abin da Ya so. KursiyyunSa ya yalwaci sammai da ƙasa. Kuma tsare su bã ya nauyayarSa. Kuma Shi ne Maɗaukaki, Mai girma} [al-Bakara: 255]. To duk wanda wannan shi ne sha'aninsa kuma wannan shine sha'anin halittarSa to ta yaya zai sauka cikin wani daga cikin su? ko ya dauke Shi a matsayin da? ko ya sanya shi Allah tare da shi?

### 11-Allah - Madaukakin Sarki - Mai rangwame ne kuma Mai jin kai ga bayinSa shi Yasa ya aiko manzanni kuma Ya saukar da litattafai

Kuma Allah - SWT – Shi Mai rangwame da jin kai ga bayinSa daga cikin rahamarSa ga bayinSa cewa Ya aiko musu manzanni, kuma Ya saukar musu da litattafai; don Ya futar da su daga duffan kafirci da shirka zuwa hasken tauhidi da shiriya.

﴿هُوَ ٱلَّذِي يُنَزِّلُ عَلَىٰ عَبۡدِهِۦٓ ءَايَٰتِۭ بَيِّنَٰتٖ لِّيُخۡرِجَكُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِۚ وَإِنَّ ٱللَّهَ بِكُمۡ لَرَءُوفٞ رَّحِيمٞ ٩﴾[الحديد: 9]

Allah - Madaukaki - Ya ce: {Shĩ ne wanda ke sassaukar da ãyõyi bayyanannu ga BãwanSa, dõmin Ya fitar da ku daga duffai zuwa ga haske, kuma lalle Allah haƙĩƙa Mai tausayi ne gare ku, Mai jin ƙai} [al-Hadid: 9] Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا رَحۡمَةٗ لِّلۡعَٰلَمِينَ ١٠٧﴾[الأنبياء: 107]

{Kuma ba Mu aike ka ba fãce dõmin wata rahama ga talikai} [al-anbiya: 107] Kuma Allah Yayi umarni ga ManzonSa da ya bada labari ga bayi cewa Shi Mai gafara ne kuma Mai jin kaine, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞نَبِّئۡ عِبَادِيٓ أَنِّيٓ أَنَا ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٤٩﴾[الحجر: 49]

{Ka bai wa bãyiNa lãbari cẽwa lalle ne Ni, Mai gãfarane, Mai jin ƙai} [al-Hijr: 49] Kuma daga cikin jin qanSa da rahamarSa Shine wanda Yake yaye cuta kuma Yake saukar Al-khairi ga bayinSa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يُرِدۡكَ بِخَيۡرٖ فَلَا رَآدَّ لِفَضۡلِهِۦۚ يُصِيبُ بِهِۦ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦۚ وَهُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٧﴾[يونس: 107]

{Kuma idan Allah Ya shãfe ka da wata cũta, to, bãbu mai yãyẽ ta fãce shi, kuma idan Yanã nufin ka da wani alhẽri, to, bãbumai mayar da falalarSa. Yanã sãmun wanda Yake so daga cikin bãyinSa da shi. Kuma Shĩ ne Mai gãfara, Mai jin ƙai} [Yunus: 107]

**12. Allah Shine Ubangiji Mai jin kai Shi kadai wanda Shine zai yi hisabi ga halittu a ranar Al-qiyama lokacin da zai tashe su baki dayansu daga kaburburansu, saboda Ya sakawa kowanne mutum da aikin da yayi na Al-kairi ko sharri, saboda duk wanda yayi aiki nagari kuma yana mai imani to yana da ni'ama matabbaciya, kuma duk wanda ya kafirta kuma yayi mummunan aiki to yana da azaba mai girma a lahira.**

Allah Shine Ubangiji Mai jin kai Shi kadai wanda Shine zai yiwa halittu hisabi a ranar Al-qiyama lokacin da Ya tashe su baki dayansu daga kaburburansu, kuma Ya sakawa kowane mutum da abunda ya aikata na Al-kairi ko sharri saboda duk wanda ya aikata ayyuka nagari kuma yana mumini to yana ni'ima madawwamiya kuma duk wanda ya kafurta kuma yayi aiki mummuna to yana da azaba mai girma a ranar Al-qiyama saboda yana cikar adalcin Allah - SWT - da hikimarSa da rahamarSa ga halittarSa cewa Ya sanya wannan duniya gidan aiki kuma Ya sanya gida na biyu shi ne gidan sakamako da hisabi da lada; har wanda ya kyautata ya samu sakamakon kyautatawa kuma wanda ya munana da azzalumi da Mai ta'addanci uqubar barnarsa da kuma zaluncin sa; kuma saboda cewa wannan al'amari sau da yawa wasu rayukan suna nisanta hakan saboda Allah Ya kafa dalilai masu yawa da suke nuna cewa Lallai tashin Al-qiyama gaskiya ne babu kokwanto a cikinsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَمِنْ ءَايَٰتِهِۦٓ أَنَّكَ تَرَى ٱلْأَرْضَ خَٰشِعَةً فَإِذَآ أَنزَلْنَا عَلَيْهَا ٱلْمَآءَ ٱهْتَزَّتْ وَرَبَتْ ۚ إِنَّ ٱلَّذِىٓ أَحْيَاهَا لَمُحْىِ ٱلْمَوْتَىٰٓ ۚ إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٣٩﴾﴾ [فصلت: 39]

{Kuma akwai daga ãyõyinSa cẽwa lalle kai kanã ganin ƙasã ƙẽƙasasshiya, to, idan Mun saukar da ruwa a kanta, sai ta

girgiza kuma ta kumbura. Lalle wannan da Ya rãya ta, haƙĩƙa, Mai rãyar da matattu ne. Lalle Shĩ Mai ĩkon yi ne a kan kõwane abu} [Fussilat: 39] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمۡ فِي رَيۡبٖ مِّنَ ٱلۡبَعۡثِ فَإِنَّا خَلَقۡنَٰكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ مِنۡ عَلَقَةٖ ثُمَّ مِن مُّضۡغَةٖ مُّخَلَّقَةٖ وَغَيۡرِ مُخَلَّقَةٖ لِّنُبَيِّنَ لَكُمۡۚ وَنُقِرُّ فِي ٱلۡأَرۡحَامِ مَا نَشَآءُ إِلَىٰٓ أَجَلٖ مُّسَمّٗى ثُمَّ نُخۡرِجُكُمۡ طِفۡلٗا ثُمَّ لِتَبۡلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمۡۖ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ أَرۡذَلِ ٱلۡعُمُرِ لِكَيۡلَا يَعۡلَمَ مِنۢ بَعۡدِ عِلۡمٖ شَيۡـٔٗاۚ وَتَرَى ٱلۡأَرۡضَ هَامِدَةٗ فَإِذَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡهَا ٱلۡمَآءَ ٱهۡتَزَّتۡ وَرَبَتۡ وَأَنۢبَتَتۡ مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ٥﴾[الحج: 5]

{Ya ku mutãne! Idan kun kasance a cikin shakka a Tãshin ¡iyãma, to, lalle ne Mũ, Man halittaku daga turɓaya, sa'an nan kuma daga gudãjin jini, sa'an nan kuma daga taõka wadda ake halittãwa da wadda ba a halittawa dõmin, Mu bayyana muku. Kuma Munã tab batar da abin da Muke so a cikin mahaifa zuwa ga wani ajali ambatacce, sa'an nan kuma Munã fitar da ku kunã jãrĩri, sa'an nan kuma dõmin ku kai ga cikar ƙarfinku. Kuma daga cikin ku akwai wanda ke mutuwa, kuma daga gare ku akwai wanda ake mayarwa zuwa ga mafi ƙasƙancin rãyuwa dõmin kada ya san kõme a bãyan ya sani. Kuma kanã ganin ƙasa shiru, sa'an nan idan Muka saukar da ruwa a kanta, sai ta girgiza kuma ta kumbura, kuma ta tsirar da tsirrai daga kõwane nau'i mai ban sha'awa} [al-Hajji: 5] Sai Allah Ya tunatar a cikin wadan nan ayoyin dalilab hankali guda uku da suke nuni kan tashin Al-qiyama su ne:

1. Lallai cewa mutum Allah ne Ya halicce shi tun farko daga turbaya kuma wanda ya halicce shi daga turbaya zai iya mayar da halittarsa zuwa rayuwa lokacin da yake turbaya.

2. Lallai cewa wanda Ya halicci mutum daga maniyyi yana iya dawo da mutum zuwa rayuwa bayan mutuwarsa.

3. Lallai cewa wanda ya raya kasa da ruwa bayan mutuwarta Yana iya raya mutane bayan mutuwarsu, kuma a cikin wannan aya akwai dalili mai girma kan mu'ajizar Al-qur'ani saoda ta yaya wadan nan ayoyin suka hadu -kuma basu da tsawo- dalilan Hankali guda uku futattu kan babbar mas'ala.

Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَوۡمَ نَطۡوِي ٱلسَّمَآءَ كَطَيِّ ٱلسِّجِلِّ لِلۡكُتُبِۚ كَمَا بَدَأۡنَآ أَوَّلَ خَلۡقٖ نُّعِيدُهُۥۚ وَعۡدًا عَلَيۡنَآۚ إِنَّا كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٠٤﴾[الأنبياء: 104]

{A rãnar da Muke naɗe sãma kamar neɗẽwar takarda ga abũbuwan rubũtãwa kamar yadda Muka fãra a farKon halitta Muke mãyar da ita. Wa'adi ne a Kanmu. Lalle ne Mun kasance Mãsu aikatãwa} [al-Anbiya: 104] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَضَرَبَ لَنَا مَثَلٗا وَنَسِيَ خَلۡقَهُۥۖ قَالَ مَن يُحۡيِ ٱلۡعِظَٰمَ وَهِيَ رَمِيمٞ ٧٨ قُلۡ يُحۡيِيهَا ٱلَّذِيٓ أَنشَأَهَآ أَوَّلَ مَرَّةٖۖ وَهُوَ بِكُلِّ خَلۡقٍ عَلِيمٌ ٧٩﴾[يس: 78-79]

{Kuma ya buga Mana wani misãli, kuma ya manta da halittarsa, ya ce: "Wãne ne ke rãyar da ƙasũsuwa alhãli kuwa sunã rududdugaggu?" Ka ce: "Wanda ya ƙãga halittarsu a farkon lõkaci Shĩ ke rãyar da su, kuma Shi, game da kõwace halitta, Mai ilmi ne} [Yasin: 78] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ءَأَنتُمۡ أَشَدُّ خَلۡقًا أَمِ ٱلسَّمَآءُۚ بَنَىٰهَا ٢٧ رَفَعَ سَمۡكَهَا فَسَوَّىٰهَا ٢٨ وَأَغۡطَشَ لَيۡلَهَا وَأَخۡرَجَ ضُحَىٰهَا ٢٩ وَٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ ذَٰلِكَ دَحَىٰهَآ ٣٠ أَخۡرَجَ مِنۡهَا مَآءَهَا وَمَرۡعَىٰهَا ٣١ وَٱلۡجِبَالَ أَرۡسَىٰهَا ٣٢﴾[النازعات: 27-32]

{Shin, kũ ne mafi wuyar halitta ko sama? Allah Ya gina ta.(27) Ya ɗaukaka rufinta, sa'an nan Ya daidaita ta.(28) Kuma

Ya duhuntar da darenta, kuma Ya fitar da hantsinta.(29) Kuma Qasa bayan haka Muka sanya ta Dunqulalliya (30) Ya fitar da ruwanta daga gare ta da makiyãyarta.(31) Kuma Duwatsu Muka kafe su (32)} [al-Nazi'at: 27-32] sai Allah Yayi bayanin cewa halittar dan Adam bata fi wahalar halittar sama da kasa ba da abunda yake cikin su kuma Shi mai iko ne kan Ya halicci sammai da kasa kuma bai gajiya ba kan ya maida halittar mutum nan gaba.

**13. Allah - Madaukakin Sarki - Ya halicci dan Adam daga turbaya, kuma Ya sanya zurriyarsa tana yaduwa bayansa, saboda mutane a asalisu daidai suke, kuma babu banbanci a tsakanin jinsi da jinsi ko kuma mutane kan mutane sai da tsoron Allah.**

Allah - Madaukakin Sarki - Ya halicci dan Adam daga turbaya, kuma Ya sanya zurriyarsa tana yaduwa bayansa, saboda mutane a asalisu daidai suke, kuma babu banbanci a tsakanin jinsi da jinsi ko kuma mutane kan mutane sai da tsoron Allah.

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقۡنَـٰكُم مِّن ذَكَرٖ وَأُنثَىٰ وَجَعَلۡنَـٰكُمۡ شُعُوبٗا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْۚ إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ خَبِيرٞ ١٣﴾[الحجرات: 13]

{Yã kũ mutãne! Lalle ne Mũ, Mun halitta ku daga namiji da mace,kuma Muka sanya ku dangõgi da kabĩlõli, dõmin ku san jũna. Lalle mafĩfĩcinku daraja a wurin Allah, (shĩ ne) wanda yake mafĩfĩcinku a taƙawa. Lalle nẽ Allah Masani ne, Mai ƙididdigẽwa} [al-Hujurat: 13] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَٱللَّهُ خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ جَعَلَكُمۡ أَزۡوَٰجٗاۚ وَمَا تَحۡمِلُ مِنۡ أُنثَىٰ وَلَا تَضَعُ إِلَّا بِعِلۡمِهِۦۚ وَمَا يُعَمَّرُ مِن مُّعَمَّرٖ وَلَا يُنقَصُ مِنۡ عُمُرِهِۦٓ إِلَّا فِي كِتَٰبٍۚ إِنَّ ذَٰلِكَ عَلَى ٱللَّهِ يَسِيرٞ ١١﴾[فاطر: 11]

{Kuma Allah ne Ya halitta ku daga turɓãya, sa'an nan daga ɗigon maniyyi, sa'an nan Ya sanya ku surkin maza da mãtã. Kuma wata mace bã ta yin ciki, kuma bã ta haihuwa, fãce da saninSa, kuma bã zã a rãyar da wanda ake rãyarwa ba, kuma bã zã a rage tsawon ransa ba fãce yanã a cikin Littãfi. Lalle, wancan mai sauki ne ga Allah} [Fadir: 11] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿هُوَ ٱلَّذِي خَلَقَكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ مِنۡ عَلَقَةٖ ثُمَّ يُخۡرِجُكُمۡ طِفۡلٗا ثُمَّ لِتَبۡلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمۡ ثُمَّ لِتَكُونُواْ شُيُوخٗاۚ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ مِن قَبۡلُۖ وَلِتَبۡلُغُوٓاْ أَجَلٗا مُّسَمّٗى وَلَعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٦٧﴾[غافر: 67]

{Shĩ ne Wanda Ya halitta ku daga turɓãya, sa'an nan daga maniyyi, sa'an nan daga sãren jini, sa'an nan Ya fitar da ku kunã jãrĩri, sa'an nan dõmin ku isa ga cikar ƙarfinku sa'an nan dõmin ku kasance tsõfaffi, kuma daga cikinku, akwai wanda ake karɓar ransa a gabãnin haka, kuma dõmin ku isa ga ajali ambatacce, kuma dammãninku ko zã ku hankalta} [Ghafir: 67] Kuma Allah – Madaukaki - Yai bayani cewa Shine wanda Ya halicci Annabi Isa da Umarnin kasance kamar yadda Ya halicci Adam daga kasa da umarnin kasance, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿إِنَّ مَثَلَ عِيسَىٰ عِندَ ٱللَّهِ كَمَثَلِ ءَادَمَۖ خَلَقَهُۥ مِن تُرَابٖ ثُمَّ قَالَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ ٥٩﴾

{Lalle ne misãlin Ĩsã a wurin Allah kamar misãlin Ãdama ne, (Allah) Yã halitta shi daga turɓãya, sa'an nan kuma Ya ce masa: "Ka kasance: "Sai yana kasancewa} [Aal Imran: 59] kuma ya

gabata na fada a sakin layi na (2) cewa Manzon Allah - SAW - yayi bayanin cewa mutane daidai suke kuma babu wani fifiko akan wani sai da tsoron Allah.

**14. Kuma kowane yaro ana haifarsa ne akan fidra**

Kuma kowane yaro ana haifarsa ne kan turba, Allah – Madaukaki - Ya ce: {Sabõda haka, ka tsayar da fuskarka ga addini, kanã mai karkata zuwa ga gaskiya, halittar Allah da Ya halitta mutãne a kanta. Bãbu musanyãwa ga halittar Allah, wannan shĩ ne addini madaidaici kuma amma mafi yawan mutãne ba su sani ba} Kuma Hanifiyya ita ce tafarkin Anabi Ibrahim - amincin Allah a gare shi-, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ثُمَّ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ أَنِ ٱتَّبِعۡ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۖ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ١٢٣﴾[النحل: 123]

{Sa'an nan kuma Muka yi wahayi zuwa gare ka (cẽwa), "Ka bi akĩdar Ibrahĩm, mai karkatã zuwa ga gaskiya, kuma bai kasance daga mãsu shirki ba} [al-Nahl: 123] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Babu wani yaro face an haife shi kan turba ne sai dai iyayensa su mayar da shi bayahude ko banasare ko bamajuse kamar yadda kosashiyar dabba shin zaku" Sannan Abu Huraira -Allah Ya yarda da shi- ya ce:

﴿فَأَقِمۡ وَجۡهَكَ لِلدِّينِ حَنِيفٗاۚ فِطۡرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيۡهَاۚ لَا تَبۡدِيلَ لِخَلۡقِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلۡقَيِّمُ وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يَعۡلَمُونَ٣٠﴾[الروم: 30]

{ka tsaida fukarka ga addini mikakke, halittar Allah da Ya halitta mutãne a kanta. Bãbu musanyãwa ga halittar Allah, wannan shĩ ne addini madaidaici kuma amma mafi yawan mutãne ba su sani ba} [al-rum: 30] Sahih Al-Bukhari: 4775 Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ku saurara Ubangiji na Ya umarceni da in sanar da ku abunda

baku sani ba daga cikin abunda Ya sanar da ni a wannan rana tawa dukkan dukiyar da na bawa bawa to halal ce, kuma lallai Ni Na halicci bayi Na akan turbar gaskiya baki dayansu sai dai cewa wasu shaidanu sun zo musu sun kautar da su daga kan Addininsu suka haramta musu abunda Na halatta musu suka umarce su da suyi shirka da Ni abun da ban saukar musu da wani dalili ba" Muslim ne ya rawaito shi 2865.

**15. Kuma babu wani mutum da aka haifeshi da sabo ko ya gaji sabon waninsa**

Babu wani mutum da aka gaifeshi da zunubai ko kuma ya gaji zunubai daga waninsa, kuma Allah - Madaukaki - Ya bamu labarin cewa Annabi - amincin Allah a gare shi- yayin da ya saba umarnin Allah kuma ya ci bishiya shi da matarsa cewa shi yayi nadama kuma ya tuba ya roqi Allah gafara sai Allah Ya kimsa masa wasu kalmomi kyawawa sai ya fade su sai Allah Ya karbi tubansu, Allah – Madaukaki - Ya ce:

﴿وَقُلْنَا يَٰٓـَٔادَمُ ٱسْكُنْ أَنتَ وَزَوْجُكَ ٱلْجَنَّةَ وَكُلَا مِنْهَا رَغَدًا حَيْثُ شِئْتُمَا وَلَا تَقْرَبَا هَٰذِهِ ٱلشَّجَرَةَ فَتَكُونَا مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ٣٥ فَأَزَلَّهُمَا ٱلشَّيْطَٰنُ عَنْهَا فَأَخْرَجَهُمَا مِمَّا كَانَا فِيهِ ۖ وَقُلْنَا ٱهْبِطُوا۟ بَعْضُكُمْ لِبَعْضٍ عَدُوٌّ ۖ وَلَكُمْ فِى ٱلْأَرْضِ مُسْتَقَرٌّ وَمَتَٰعٌ إِلَىٰ حِينٍ ٣٦ فَتَلَقَّىٰٓ ءَادَمُ مِن رَّبِّهِۦ كَلِمَٰتٍ فَتَابَ عَلَيْهِ ۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ٣٧ قُلْنَا ٱهْبِطُوا۟ مِنْهَا جَمِيعًا ۖ فَإِمَّا يَأْتِيَنَّكُم مِّنِّى هُدًى فَمَن تَبِعَ هُدَاىَ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ٣٨﴾ [البقرة: 35-38]

{Kuma Muka ce Ya kai Adam ku zauna kai da matar ka cikin Aljanna kuma kuci daga cikinta duk yanda kuka so amma kada ku kusanci wannan itaciya to sai ku zamanto cikin azzalumai (35) Sai Shaiɗan ya talãlãɓantar da su ga barinta, sai ya fitar da su daga abin da suka kasance a cikinsa, kuma Muka ce: ku sauko Sãshenku nã maƙiyi ga sãshe, kuma kuna da a cikin ƙasa

matabbata da jin dãɗi zuwa wani lõkaci." (36) To take sai Adam yakarbi kalmomi daga Ubangijinsa to take sai ya karbi tubansa lallai shi ne mai yawan karbar tuba ne kuma mai rahma.(37) Muka ce: "Ku ku sauka daga gare ta gabã ɗaya. To, imma lalle shiriya ta je muku daga gare Ni, to, wanda ya bi shiriya ta to, bãbu tsõro a kansu, kuma bã su yin baƙin ciki(38)} [al-Baqara: 35-38] Kuma a lokacin da Allah Ya karbi tuban Annabi Adam - amincin Allah a gare shi- babu sauran wani zunubi a kansa kuma daga nan ma cewa zurriyarsa basu gaji komai ba na zunubin tuni ya gushe da tuban kuma asali cewa mutum baya daukan laifin waninsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قُلۡ أَغَيۡرَ ٱللَّهِ أَبۡغِي رَبّٗا وَهُوَ رَبُّ كُلِّ شَيۡءٖۚ وَلَا تَكۡسِبُ كُلُّ نَفۡسٍ إِلَّا عَلَيۡهَاۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۚ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُم مَّرۡجِعُكُمۡ فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ١٦٤﴾[الأنعام: 164]

{Kuma ba'a bawa ko wane rai sai abunda ya aikata, kuma wani rai baya daukan laifin wani rai, sannan kuma makomarku zuwa Ubangijinku ce sai ya baku labarin abunda kuke sabani a cikinsa} [al-an'am 164] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿مَّنِ ٱهۡتَدَىٰ فَإِنَّمَا يَهۡتَدِي لِنَفۡسِهِۦۖ وَمَن ضَلَّ فَإِنَّمَا يَضِلُّ عَلَيۡهَاۚ وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۗ وَمَا كُنَّا مُعَذِّبِينَ حَتَّىٰ نَبۡعَثَ رَسُولٗا١٥﴾[الإسراء: 15]

{Wanda ya nẽmi shiryuwa, to, ya nẽmi shiryuwa ne dõminkansa kawai kuma wanda ya ɓace, to, ya ɓace ne a kansa kawai kuma rai mai ɗaukar nauyi bã ya ɗaukar nauyin wani ran, kuma ba Mu zama mãsu yin azãba ba, sai Mun aika wani Manzo} [al-Israa: 15] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَلَا تَزِرُ وَازِرَةٞ وِزۡرَ أُخۡرَىٰۚ وَإِن تَدۡعُ مُثۡقَلَةٌ إِلَىٰ حِمۡلِهَا لَا يُحۡمَلۡ مِنۡهُ شَيۡءٞ وَلَوۡ كَانَ ذَا قُرۡبَىٰٓۗ إِنَّمَا تُنذِرُ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَۚ وَمَن تَزَكَّىٰ فَإِنَّمَا يَتَزَكَّىٰ لِنَفۡسِهِۦۚ وَإِلَى ٱللَّهِ ٱلۡمَصِيرُ١٨﴾[فاطر: 18]

{Kuma wani rai mai ɗaukar nauyi, bai ɗaukar nauyin wani rai. Kuma idan ran da aka nauyaya wa kãya ya yi kira (ga wani mataimaki) zuwa ga kãyansa, bã zã a dauki kõme ba daga gare shi, kuma kõ dã (wanda ake kiran) yã kasance makusancin zumunta ne. Kanã gargaɗi kawai ne ga waɗanda ke tsoron Ubangijinsu a fake, kuma suka tsayar da salla. Kuma wanda ya tsarkake, to, yanã tsarkaka ne dõmin kansa. Kuma zuwa ga Allah kawai makõma take} [Fadir: 18].

**16. Kuma manufa na halittar mutane ita ce bautar Allah shi kadai**

Manufar halittar mutane ita ce bautar Allah Shi kadai, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَمَا خَلَقْتُ ٱلْجِنَّ وَٱلْإِنسَ إِلَّا لِيَعْبُدُونِ٥٦﴾[الذاريات: 56]

{Kuma Ban halitta aljannu da mutãne ba sai dõmin su bauta Mini} [al-Zariyat: 56]

**17. Musilunci ya karrama mutum -maza da mata- kuma ya dauke masa baki dayan haqqoqinsa, kuma ya sanya shi abun tambaya akan baki dayan sauran zaxuxxukansa, da ayyukansa da kuma Tasarrufinsa, kuma ya dora masa nauyin kowane irin aiki da zai cutar da kansa ko ga wani akansa**

Musulunci ya karrama mutum -maza da mata- saboda Allah - Madauakaki - Ya halicci mutum saboda ya zamanto halifanSa a bayan kasa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَإِذْ قَالَ رَبُّكَ لِلْمَلَٰٓئِكَةِ إِنِّي جَاعِلٞ فِي ٱلْأَرْضِ خَلِيفَةٗۖ...٣٠﴾[البقرة: 30]

{Ka tuna lokacin da Ubangijinka Ya ce da Mala'iku lallai ni zan sanya halifaNa a bayan kasa} [al-Baqara: 30] Kuma wannan karramawar ta hade baki dayan 'Yan Adam, Allah - Maxaukaki - Ya ce:

﴿۞ وَلَقَدۡ كَرَّمۡنَا بَنِيٓ ءَادَمَ وَحَمَلۡنَٰهُمۡ فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِ وَرَزَقۡنَٰهُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَفَضَّلۡنَٰهُمۡ عَلَىٰ كَثِيرٖ مِّمَّنۡ خَلَقۡنَا تَفۡضِيلٗا ٧٠﴾ [الإسراء: 70]

{Kuma lalle ne Mun girmama 'yan Adam, kuma Muka ɗauke su a cikin ƙasa da tẽku kuma Muka azurta su daga abũbuwa mãsu dãɗi kuma Muka fĩfĩta su a kan mãsu yawa daga waɗanda Muka halitta, fĩfĩtãwa} [al-Isra'a: 70] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِيٓ أَحۡسَنِ تَقۡوِيمٖ ٤﴾ [التين: 4]

{Lalle ne, Mun halitta mutum a cikin mafi kyawon tsayuwa} [al-Teen: 4] Kuma Allah Ya hana mutum ya sanya kansa mai bi qasqantacce ga wani abun bauta ko abun bi ko da'a koma bayan Allah, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَمِنَ ٱلنَّاسِ مَن يَتَّخِذُ مِن دُونِ ٱللَّهِ أَندَادٗا يُحِبُّونَهُمۡ كَحُبِّ ٱللَّهِۖ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَشَدُّ حُبّٗا لِّلَّهِۗ وَلَوۡ يَرَى ٱلَّذِينَ ظَلَمُوٓاْ إِذۡ يَرَوۡنَ ٱلۡعَذَابَ أَنَّ ٱلۡقُوَّةَ لِلَّهِ جَمِيعٗا وَأَنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعَذَابِ ١٦٥ إِذۡ تَبَرَّأَ ٱلَّذِينَ ٱتُّبِعُواْ مِنَ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُواْ وَرَأَوُاْ ٱلۡعَذَابَ وَتَقَطَّعَتۡ بِهِمُ ٱلۡأَسۡبَابُ ١٦٦﴾ [البقرة: 165-166]

{Kuma akwai daga mutãne wanda yake riƙon kinãye, baicin Allah, suna son su, kamar son Allah, kuma waɗanda suka yi ĩmãni ne mafiya tsananin so ga Allah. Kuma dã waɗanda suka yi zãlunci, suna ganin lõkacin da zã su ga azãba, da cewa lalle ne ƙarfi ga Allah yake duka, da cẽwa lalle neAllah Mai tsananin azãba ne} [al-Baqara: 165-166] Kuma Allah - Madaukakin Sarki - Ya bayyana cewa cikakken mulki nasa ne a ranar Al-qiyama:

﴿قَالَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ لِلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُوٓاْ أَنَحۡنُ صَدَدۡنَٰكُمۡ عَنِ ٱلۡهُدَىٰ بَعۡدَ إِذۡ جَآءَكُمۖ بَلۡ كُنتُم مُّجۡرِمِينَ ٣٢ وَقَالَ ٱلَّذِينَ ٱسۡتُضۡعِفُواْ لِلَّذِينَ ٱسۡتَكۡبَرُواْ بَلۡ مَكۡرُ ٱلَّيۡلِ وَٱلنَّهَارِ إِذۡ تَأۡمُرُونَنَآ

أَن نَّكۡفُرَ بِٱللَّهِ وَنَجۡعَلَ لَهُۥٓ أَندَادٗاۚ وَأَسَرُّواْ ٱلنَّدَامَةَ لَمَّا رَأَوُاْ ٱلۡعَذَابَۚ وَجَعَلۡنَا ٱلۡأَغۡلَٰلَ فِيٓ أَعۡنَاقِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْۖ هَلۡ يُجۡزَوۡنَ إِلَّا مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٣٣﴾ [سبأ: 32-33]

{Makangara suka ce wa maraunana: Ashe, mũ ne muka kange ku daga shiriya a bãyan ya zo muku? Ã, a' kun dai kasance mãsu laifi." (32) Kuma maraunana suka ce wa makangara. "Ã'a, (ku tuna) mãkircin dare da na rãna a lõkacin da kuke umurnin mu da mu kãfirta da Allah, kuma mu sanya Masa abõkan tãrayya." Kuma suka assirtar da nadãma a lõkacin da suka ga azãba. Kuma Muka sanya ƙuƙumma a cikin wuyõyin waɗanda suka kãfirta. Lalle, bã zã a yi musu sakamako ba fãce da abin da suka kasance sunã aikatãwa(33)} [Saba'i:32-33] Kuma daga cikar adalcin Allah - SWT - a ranar Alqiyama cewa zai dora alhaki ga masu da jagororin da suka batar da zunuban wadan da suka batar da su ba tare da ilimi ba, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿لِيَحۡمِلُوٓاْ أَوۡزَارَهُمۡ كَامِلَةٗ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَمِنۡ أَوۡزَارِ ٱلَّذِينَ يُضِلُّونَهُم بِغَيۡرِ عِلۡمٍۗ أَلَا سَآءَ مَا يَزِرُونَ ٢٥﴾ [النحل: 25]

{Dõmin su ɗauki zunubansu cikakku a Rãnar ¡iyãma, kuma daga zunuban waɗanda suke ɓatarwa bã da wani ilmi ba. To, abin da suke ɗauka na zunubi ya mũnana} [al-Nahl: 25] kuma Allah Ya lamincewa mutum baki dayan haqqoqinsa a duniya da lahira, kuma mafi girman haqqoqin da Allah da Musulunci ya lamunce kuma ya bayyana su ga mutane haqqin Allah kan mutane da haqqin mutane kan Allah. An rawaito daga Mu'az - Allah Ya yarda da shi- ya ce: Na kasance abayan Annabi - SAW - munyi goyo sai ya ce: "Yakai Mu'az ko kasan haqqin Allah akan bayinSa da haqiin bayi akan Allah sai nace: A'a sai ya ce: "

Haqqin Allah akan bayi shi ne su bauta maSa kuma kada suyi masa shirka: sannan yayi tafiya wani lokaci sai ya ce: "Ya kai Mu'az" sai nace: Amsawarka bayan Amsawa sai ya ce: "Shin kasan haqqin bayi akan Allah? wanda idan suka aikata wancan bazaiyi musu azaba ba" Sahih Al-Bukhari: 6840 Kuma Musulunci ya lamunce ga mutum Addininsa na gaskiya da zuriyarsa da dukiyarsa da mutuncinsa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ka ce lallai Allah Ya haramta a gare ku jinnanenku da dukiyoyinku da mutuncinku kamar haramcin wannan ranar taku a cikin wannan watan naku a wannan garin naku" Sahih Al-Bukhari: 6501 Kuma haqiqa Manzon Allah - SAW - ya bayyana wannan alkawarin mai girma a cikin hajjin bankwana wanda ya halarta a tare da sama da Sahabi dubu, kuma ya maimaita wannan ma'anar kuma ya qarfafata a ranar Layya a hajiin bankwana" Kuma musulunci ya sanya mutum ya zamanto mai dauakar nauyin sauran zabubbukansa da ayyukansa da kuma tasarrufinsa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَكُلَّ إِنسَٰنٍ أَلۡزَمۡنَٰهُ طَٰٓئِرَهُۥ فِي عُنُقِهِۦۖ وَنُخۡرِجُ لَهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ كِتَٰبٗا يَلۡقَىٰهُ مَنشُورًا ١٣﴾[الإسراء: 13]

{Kuma kowane mutum mun lazamta masa wani littafinsa a wuyansa, kuma za'a futo da shi a ranar Alkiyama wani littafi da zai gamu da shi an yada shi, ka karanta Littafinka ya isheka yiwa kanka da kanka Hisabi} [al-Isra'a: 13] Ai abunda ya aikata na Al-kairi ko sharri da Allah Ya sanya shi yana lizimtarsa kuma baya iya wuce shi zuwa waninsa, saboda ba za'a yi masa hisabi ba da aikin waninsa, kuma ba za'a yiwa waninsa hisabi ba da aikinsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلۡإِنسَٰنُ إِنَّكَ كَادِحٌ إِلَىٰ رَبِّكَ كَدۡحٗا فَمُلَٰقِيهِ۝٦﴾[الانشقاق: 6]

{Ya kai mutum! Lalle ne kai mai aikin wahal da kai ne zuwa ga Ubangijinka, wahala mai tsanani, To, kai mai haɗuwa da Shi ne} [al-Inshiqaq: 6], kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿مَّنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ۝٤٦﴾[فصلت: 46]

{Wanda ya aikata aiki na ƙwarai to sabõda kansa ne, kuma wanda ya mũnanã, to, yanã akansa. Kuma Ubangiwinka, bã Mai zãlunci ga bãyinSa ne ba} [Fussilat: 46] Kuma Musulunci yana dorawa mutum nauyin kowane aiki, ai aikin da ya cutar da kansa ko ya cutar da wasu, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَمَن يَكۡسِبۡ إِثۡمٗا فَإِنَّمَا يَكۡسِبُهُۥ عَلَىٰ نَفۡسِهِۦۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا۝١١١﴾[النساء: 111]

{Kuma wanda ya yi tsirfanci zunubi, to yanã tsirfarsa ne a kan kansa kawai. Kuma Allah Yã kasance Masani, Mai hikima} [al-Nisa'a: 111] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿مِنۡ أَجۡلِ ذَٰلِكَ كَتَبۡنَا عَلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَنَّهُۥ مَن قَتَلَ نَفۡسَۢا بِغَيۡرِ نَفۡسٍ أَوۡ فَسَادٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَكَأَنَّمَا قَتَلَ ٱلنَّاسَ جَمِيعٗا وَمَنۡ أَحۡيَاهَا فَكَأَنَّمَآ أَحۡيَا ٱلنَّاسَ جَمِيعٗاۚ وَلَقَدۡ جَآءَتۡهُمۡ رُسُلُنَا بِٱلۡبَيِّنَٰتِ ثُمَّ إِنَّ كَثِيرٗا مِّنۡهُم بَعۡدَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡأَرۡضِ لَمُسۡرِفُونَ۝٣٢﴾[المائدة: 32]

{Saboda wancan ne muka wajabtawa Bani Isra'ila cewa duk wanda ya kashe wani rai ba tare da ya kashe wani ba ko yayi barna a bayan kasa to kamar ya kashe mutane ne baki daya kuma duk wanda ya raya ta to kamar ya raya mutane ne baki dayan su, kuma hakika manzanninMu sunzo musu a ayoyinMu bayyanannu sannan mafi yawa daga cikinsu masu barna ne bayan nan} [Al-Ma'ida: 32] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Ba wani rai da za'a kashe akan zalunci sai idan ya kasance dan Annabi Adam na farko yana da

alhaki a cikin sadomin shi ne wanda ya sunnata kisa". Sahih Muslim: 5150.

**18. kuma ya Sanya namiji da mace daidai da daidai wajen daukar alhakim aikinsu da kuma sakamako da bada lada**

Musulunci yasanya mata da maza daidai wajen aiki da kuma daukar nauyi da sakamako da lada, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَمَن يَعۡمَلۡ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ وَلَا يُظۡلَمُونَ نَقِيرٗا ١٢٤﴾[النساء: 124]

{Kuma wanda ya yi aiki daga ayyukan ƙwarai, namiji ne ko kuwa mace, alhãli kuwa Yanã mũmini, to, waɗannan sunã shiga Aljanna kuma bã zã a zãlunce su da gwargwadon hancin gurtsun dabĩ no ba} [al-Nisa'a: 124] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗۖ وَلَنَجۡزِيَنَّهُمۡ أَجۡرَهُم بِأَحۡسَنِ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩٧﴾[النحل: 97]

{Wanda ya aikata aiki na ƙwarai daga namiji kõ kuwa mace, alhãli yanã mũmini, to, haƙĩka Munã rãyar da shi, rãyuwa mai dãɗi. Kuma haƙĩka Munã sãkã musu lãdarsu da mafi kyãwun abin da suka kasance sunã aikatãwa} [al-Nahl: 97] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿مَنۡ عَمِلَ سَيِّئَةٗ فَلَا يُجۡزَىٰٓ إِلَّا مِثۡلَهَاۖ وَمَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَأُوْلَٰٓئِكَ يَدۡخُلُونَ ٱلۡجَنَّةَ يُرۡزَقُونَ فِيهَا بِغَيۡرِ حِسَابٖ ٤٠﴾[غافر: 40]

{Wanda ya aikata mummunan aiki to, ba za a sãka masa ba fãce da misãlinsa, kuma wanda ya aikata aiki na ƙwarai daga namiji kõ mace alhãli kuwa shĩ mũmini ne, to, waɗannan sunã shiga Aljanna, anã ciyar da su a cikinta, bã da lissãfi ba} Ghafir: 40] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلۡمُسۡلِمِينَ وَٱلۡمُسۡلِمَٰتِ وَٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ وَٱلۡقَٰنِتِينَ وَٱلۡقَٰنِتَٰتِ وَٱلصَّٰدِقِينَ وَٱلصَّٰدِقَٰتِ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَٱلصَّٰبِرَٰتِ وَٱلۡخَٰشِعِينَ وَٱلۡخَٰشِعَٰتِ وَٱلۡمُتَصَدِّقِينَ وَٱلۡمُتَصَدِّقَٰتِ وَٱلصَّٰٓئِمِينَ وَٱلصَّٰٓئِمَٰتِ وَٱلۡحَٰفِظِينَ فُرُوجَهُمۡ وَٱلۡحَٰفِظَٰتِ وَٱلذَّٰكِرِينَ ٱللَّهَ كَثِيرٗا وَٱلذَّٰكِرَٰتِ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُم مَّغۡفِرَةٗ وَأَجۡرًا عَظِيمٗا ٣٥﴾[الأحزاب: 35]

{Lalle, Musulmi maza da Musulmi mãtã da muminai maza da muminai mãtã, da mãsu tawãli'u maza da mãsu tawãlĩu mãtãda mãsu gaskiya maza da mãsu gaskiya mãtã, da mãsu haƙuri maza da mãsu haƙuri mãtã, da mãsu tsõron Allah maza da mãsu tsõron Allah mãtã, da mãsu sadaka maza da mãsu sadaka mãtã, da mãsu azumi maza da mãsu azumi mãtã da mãsu tsare farjõjinsu maza da mãsu tsare farjõjinsu mãtã, da mãsu ambaton Allah da yawa maza da mãsu ambatonsa mãtã, Allah Ya yi musu tattalin wata gãfara da wani sakamako mai girma} [al-Ahzab: 35].

**19. Musulunci ya karrama mace, kuma ya sanya mata su zamanto abokan tafiyar maza, kuma ya lazamtawa mazan ciyar da su idan ya kasance yana da iko, saboda haka ya wajaba uba ya ciyar da diyarsa, haka uwa akan danta idan ya kasance ya balaga kuma yana da Iko, haka mata akan mijinta**

Kuma Musulunci ya dauki mata a matsayin 'yan uwan maza manzon Allah - tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce "Lallai Mata 'yan Uwan maza ne" Tirmizi da Ahmad suka rawaito shi (113) Kuma yana daga cikin Karramawar da Allah Yayiwa mace cewa Musulunci ya wajabta ciyar da uwa akan danta idan yana da iko Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Hannun da ya bayar shi ne a sama kuma ka fara da mahaifiyarka da mahaifinka da 'yar uwatka

sannan mafi kusancin ka" Imam Ahmad ya ru.waito shi Kuma bayanin matsayin iyaye zai zo in Allah Ya so a sakin layi lamba ta (29) Kuma yana daga cikin karramawar da Musulunci yayiwa mace cewa an wajabtawa miji ciyar da matarsa idan ya kasance zai iya, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿لِيُنفِقۡ ذُو سَعَةٖ مِّن سَعَتِهِۦۖ وَمَن قُدِرَ عَلَيۡهِ رِزۡقُهُۥ فَلۡيُنفِقۡ مِمَّآ ءَاتَىٰهُ ٱللَّهُۚ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفۡسًا إِلَّا مَآ ءَاتَىٰهَاۚ سَيَجۡعَلُ ٱللَّهُ بَعۡدَ عُسۡرٖ يُسۡرٗا ٧﴾[الطلاق: 7]

{Sai mawadãci ya ciyar daga wadãtarsa kuma wanda aka ƙuntata masa arzikinsa, to, sai ya ciyar daga abin da Allah Ya bã shi. Allah bã Ya kallafa wa wani rai fãce abin da Ya bã shi. Allah zai sanya sauƙi a bãyan tsanani} [al-Dalaq:7] Kuma wani mutum ya tambayi Annabi - SAW - maye haqqin mace akan mijinta ya ce: "Ka ciyar da ita idan kaci kuma ka tufatar da ita idan kayi tufa, kuma kada daketa a fuska kuma kada ka ci nata mutunci" Imam Ahmad ya ruwaito shi. Kuma Manzon Allah - SAW - ya ce: Yana mai bayanin wasu haqqoqin mata kan mazajensu "Kuma suna da haqqin ciyarwa da tufatarwa akan ku gaawrgawadon iko" Sahih Muslim. Kuma Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Ya ishi mutum laifi ya tozarta wanda yake ciyarwa" Imam Ahmad ya ruwaito shi. Kuma Khaddabi ya ce: Fadinsa "Wanda yake ciyarwa: Yana nufin wanda ya zama dole ya ciyar da shi kuma ma'ana kamar shi ya ce ga wanda yake sadaka kada kayi sadaka ba da abunda ya ragu ba na abincin iyalanka don kana neman lada; sai abun ya juye alhaki idan ka tozarta su" Kuma yana daga cikin girmamawa da Musulunci yayiwa mace lallai cewa ya wajabta masa ciyar da diya kan ubanta, Allah - Madaukakiin Sarki - Ya ce:

﴿۞ وَٱلۡوَٰلِدَٰتُ يُرۡضِعۡنَ أَوۡلَٰدَهُنَّ حَوۡلَيۡنِ كَامِلَيۡنِۖ لِمَنۡ أَرَادَ أَن يُتِمَّ ٱلرَّضَاعَةَۚ وَعَلَى ٱلۡمَوۡلُودِ لَهُۥ رِزۡقُهُنَّ وَكِسۡوَتُهُنَّ بِٱلۡمَعۡرُوفِۚ لَا تُكَلَّفُ نَفۡسٌ إِلَّا وُسۡعَهَاۚ...﴿٢٣٣﴾﴾[البقرة: 233]

"Iyaye Mata suna shayar da 'Ya'ansu shekara biyu cikakku ga wanda yake son cikar shayarwa kuma yana kan wanda aka haifa Masa ya ciyar da su da kuma tufatar da su gwargwadon iko} [al-Baqara: 233] Sai yayi bayani cewa lallai ne yana kan uba wanda aka haifa masa yaro ya ciyar da shi da tufatar da shi gwargwadin iko, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿...فَإِنۡ أَرۡضَعۡنَ لَكُمۡ فَـَٔاتُوهُنَّ أُجُورَهُنَّ ...﴿٦﴾﴾[الطلاق: 6]

{To idan suka shayar muku to ku basu ladan su} [al-Dalaq: 6] Sai Allah Ya wajabta ladan shayar da yaro kan mahaifi; sai hakan ya nuna cewa ciyarwar da akan mahaifinsa take kuma yaro ya hade mace da namiji kuma ya zo a cikin hadisi mai zuwa dalilin da yake nuna wajabcin ciyar da mata da 'ya'yamta a kan uba. Saboda an rawaito daga Nana Aisha -Allah Ya yarda da ita- cewa Hindu ta ce da manzon Allah - SAW - lallai Abu Sufyan mutum ne mai kauro saboda haka ina da buqatar in riqa daukar wani abu daga dukiyarsa sai ya ce: "Ki dauki abunda zai isheki ke da danki daidai gwargwado" Bukhari ne ya rawaito shi. Kuma Annabi yayi bayanin falalar ciyar da 'ya'ya mata da 'yan uwa mata sai Manzon Allah - SAW - ya ce: "Duk wanda ya raini 'yan mata biyu ko uku ko 'yan mata biyu ko uku har sukai aure ko ya mutu ya barsu to ni da shi zamu shiga Al-janna kafada da kafada, sai yai nuni da yatsunsa na nuni da na tsakiya" Al-silsila Al-Sahiha: 296.

**20. kuma mutuwa ba karewa bace ta har abada, a'a ita wata tafiya daga gidan aiki zuwa gidan sakamako, kuma mutuwa**

**yana samun jiki da ruhi, mutuwar ruhi ita ce rabuwar ruhi daga jiki, sannan kuma ya dawo zuwa jinkin bayan tashin Al-qiyama, kuma ruhi baya tafiya zuwa wani jikin bayan mutuwa, kuma baya sake tsiruwa a wabi jikin daban**

Mutuwa ba ita ba ce qarewa ta har abada Allah - Madukaki - Ya ce: Ka ce:

:﴿۞قُلۡ يَتَوَفَّىٰكُم مَّلَكُ ٱلۡمَوۡتِ ٱلَّذِي وُكِّلَ بِكُمۡ ثُمَّ إِلَىٰ رَبِّكُمۡ تُرۡجَعُونَ ١١﴾[السجدة: 11]

{Mala, ikin mutuwa ne. wanda aka wakkala a gare ku, shĩ ne ke karɓar rãyukanku. Sa'an nan zuwa ga Ubangijinku ake mayar da ku} Mutuwa ba ita ba ce qarewa ta har abada, kuma mutuwa tana samun jiki ne da ruhi kuma mutuwar Ruhi shi ne futarsa daga jiki sannan ya dawo zuwa gare shi bayan Tashin Al-qiyama, Allah Madaukakin Sarki - Ya ce:

{Allah ne ke karɓar rãyuka a lõkacin mutuwarsu, da waɗannan da ba su mutu ba, a cikin barcinsu. Sa'an nan Ya riƙe wanda Ya hukunta mutuwa a kansa kuma Ya saki gudar, har zuwa ga ajali ambatacce. Lalle a cikin wancan, haƙĩƙa, akwai ãyõyi ga mutãne waɗanda ke yin tunãni} [al-Zumar: 42] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Lallai ruhi idan aka karbe shi yana bin Ido" Muslim ne ya rawaito shi 920. Kuma bayan mutuwa mutum daga gidan aiki yana tafiya zuwa gidan sakamako, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿إِلَيۡهِ مَرۡجِعُكُمۡ جَمِيعٗاۖ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقًّاۚ إِنَّهُۥ يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ لِيَجۡزِيَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ بِٱلۡقِسۡطِۚ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَهُمۡ شَرَابٞ مِّنۡ حَمِيمٖ وَعَذَابٌ أَلِيمُۢ بِمَا كَانُواْ يَكۡفُرُونَ ٤﴾ [يونس: 4]

{zuwa gare Shi makõmarku take gabã ɗaya, wa'adin Allah gaskiya ne. Haƙĩƙa, Shi ne Yake fara halitta, sa'an nan kuma Ya

mayar da ita dõmin Ya sãka wa waɗanda suka yi ĩmãni kuma suka aikata ayyukan ƙwarai da ãdalci, kuma waɗanda suka kãfirta sunã da abin sha daga ruwan zãfi, da azãba mai raɗaɗi, sabõda abin da suka kasance sunã yi na kãfirci} [Yunus: 4]

Kuma rai baya tafiya zuwa wani jikin bayan mutuwa kuma baya komawa cikin wani saboda haka da'awar komawar rai cikin wani hankali ma ba zai dauke shi ba ko ji kuma ba'a samu wani dalili da yake nuna wannan aqida ba daga Annabawa -amincin Allah a gare su -.

**21, kuma Musulunci yana kira ne zuwa imani da jigajigan imani manya, kuma shi ne imani da Allah da Mala'ikunsa da imani da litattafan Allah kamar Al-taura da Linjila da Zabura -kafin jirkita su- da kuma Al-qurani, da kuma imani da bai dayan Annabawa da Manzanni -Amincin Allah a gare su- kuma yayi imani da cika makin su shi Annabu Muhammadu Manzon Allah cikamakin Annabawa da Manzanni da Kuma imani da ranar Lahira kuma ya sani cewa rayuwar duniya da ita ce karshe da kuma da halittu sun zama tsantsar wasa kuma imani da hukuncin Allah da kaddarara**

Musulunci yana kira zuwa imani da babban tushen imani wanda baki dayan Annabawa da Manzanni sukai kira akansa -amincin Allah a gare su- kuma su ne:

Na farko: Imani da Allah cewa shi ne Ubangiji kuma Mahalicci kuma Mai Azurtawa kuma Mai gudanar da wannan halitta kuma cewa shi kadai ya ke wanda ya cancanci ibada kuma cewa bautar waninsa batacciya ce kuma kowane abun bauta in ba shi ba to barna ne kuma ibada bata cancanci wani sai shi kuma ibada bata inganta ba sai a gare shi, kuma bayanin wannan mas'alar ya gabata a sakin layi na (8)

Kuma Allah - SWT - Ya fadi waxan nan manyan gishikai a cikin ayoyi masu yawa daban daban a cikin Al-qur'ano mai girma daga cikin su fadin Allah – Madaukaki -:

﴿ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ وَقَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ غُفۡرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيۡكَ ٱلۡمَصِيرُ٢٨٥﴾[البقرة: 285]

"Mun ji kuma mun yi dã'a; (Muna nẽman) gãfararKa, yã { Manzon Allah yã yi ĩmãni da abin da aka saukar zuwa gare shi daga Ubangijinsa, da mũminai. Kõwanensu yã yi ĩmãni da Allah, da mala'ikunSa, da littattafanSa, da manzanninSa. Bã mu rarrabẽwa a tsakãnin daya daga manzanninSa. Kuma (mũminai) suka ce: Ubangijinmu, kuma zuwa a gare Ka makõma take} [al-Baqara: 285] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿۞لَّيۡسَ ٱلۡبِرَّ أَن تُوَلُّواْ وُجُوهَكُمۡ قِبَلَ ٱلۡمَشۡرِقِ وَٱلۡمَغۡرِبِ وَلَٰكِنَّ ٱلۡبِرَّ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ وَٱلۡكِتَٰبِ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ وَءَاتَى ٱلۡمَالَ عَلَىٰ حُبِّهِۦ ذَوِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينَ وَٱبۡنَ ٱلسَّبِيلِ وَٱلسَّآئِلِينَ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى ٱلزَّكَوٰةَ وَٱلۡمُوفُونَ بِعَهۡدِهِمۡ إِذَا عَٰهَدُواْۖ وَٱلصَّٰبِرِينَ فِي ٱلۡبَأۡسَآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَحِينَ ٱلۡبَأۡسِۗ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُتَّقُونَ١٧٧﴾[البقرة: 177]

{Bai zama addini ba dõmin kun jũyar da fuskõkinku wajen gabas da yamma, kuma amma addini shi ne ga wanda ya yi ĩmãni da Allah da Rãnar Lãhira da malã'iku da Littattafan sama da Annabãwa, kuma ya bãyar da dũkiya, akan yana son ta, ga mai zumunta da marãyu da matalauta da ɗan hanya da mãsu rõƙo, kuma a cikin fansar wuya, kuma ya tsayar da salla, kuma ya bãyar da zakka, da mãsu cika alkawari idan sun ƙulla

alkawarin da mãsu haƙuri a cikin tsanani da cũta da lõkacin yãƙi. Waɗannan su ne suka yi gaskiya. Kuma waɗannan su ne mãsu taƙawa} [al-Baqara: 177] Kuma Allah - Madaukaki - Yayi kira zuwa imani da wadan nan ginshikan kuma Ya bayyana cewa duk wanda ya kafirta da su to haqiqa ya bata bata mai nisa Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلْكِتَـٰبِ ٱلَّذِى نَزَّلَ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلْكِتَـٰبِ ٱلَّذِىٓ أَنزَلَ مِن قَبْلُ ۚ وَمَن يَكْفُرْ بِٱللَّهِ وَمَلَـٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلْيَوْمِ ٱلْـَٔاخِرِ فَقَدْ ضَلَّ ضَلَـٰلًۢا بَعِيدًا ﴿١٣٦﴾﴾ [النساء: 136]

{Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku yi ĩmãni da Allah da Manzonsa, da Littãfin da Ya sassaukar ga ManzonSa da Littãfin nan wanda Ya saukar daga gabãni. To, wanda ya kãfirta da Allah da malã'ikunSa, da LittattafanSa, da ManzanninSa, da Rãnar Lãhira, to, lalle ne yã ɓace, ɓata mai nĩsa} [al-nisa'a: 136] Kuma ya zo a cikin hadisin Umar Bn Khaddab -Allah Ya yarda da shi- ya ce: "Wata rana muna zaune a wajen manzon Allah - SAW - wata rana sai wani mutum ya bullo mana mai tsananin farin kaya mai tsananin baqin gashin kai kuma ba'a ganin alamar tafiya tare da shi kuma babu wanda ya san shi daga cikin mu, har ya zauna a gaban Manzon Allah - SAW - sannan ya jingina guiwoyinsa zuwa Guiwoyinsa sannan ya dora hannayensa akan cinyoyinsa kuma ya ce: ya Muhammad bani labarin game da Musulunci sai Manzon Allah - SAW - ya ce: Ka tsaida sallah ka bada zakka kuma kayi Azumin watan Ramadana da hajjatar dakin Allah idan kasamu Iko" ya ce: Kayi gaskiya ya ce: sai muka yi mamaki yana tambayarsa kuma yana gasgatashi ya ce: to ka bani labari game da Imani ya ce: "Ka yi Imani da Allah da Mala'ikunSa da

litattafanSa da ManzanninSa da Ranar lahira da Imani da kaddara alkairinsa da sharrinsa" ya ce: kayi gaskiya, ya ce: to ka bani labarin kyautatawa ya ce: "ka bautawa Allah kamar kana ganinSa saboda in baka ganinsa Shi Yana ganinka" Sahih Muslim: 8 A cikin wannan hadisin Mala'ika Jibril - amincin Allah a gare shi- ya zo wajen manzon Allah – SAW - kuma ya tambaye shi dangane da kingishikan Musulunci kuma sune: Musulunci da imani da Kyautatawa sai Manzon AllaH - SAW - ya amsa masa, sannan Manzon Allah - SAW - ya bawa sahabbansa labari cewa wannan Mala'ika Jibril ne wanda ya zo musu don ya sanar da su Addininsu saboda wannan musuluncin saqon Allah ne wanda Mala'ika Jibril - amincin Allah a gare shi - ya kawo kuma ya isar da shi ga mutane, Manzo - SAW - da Sahabban sa -Allah ya yarda da su- suka kiyaye shi kuma suka isar da shi ga mutane bayansa. Na biyu: Imani da mala'iku kuma su wata duniya ce boyayyiya Allah Ya halicce su kuma ya sanya su a wata kama ta musamman kuma ya dora musu wasu ayyuka masu girma kuma mafi girman ayyukansu shi ne Isar da saqonnin Manzannin Allah ga Manzanni da Annabawa - amincin Allah su tabbata a gare su- kuma mafi girman Mala'iku - amincin Allah a gare su-, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يُنَزِّلُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ بِٱلرُّوحِ مِنۡ أَمۡرِهِۦ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنۡ عِبَادِهِۦٓ أَنۡ أَنذِرُوٓاْ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱتَّقُونِ ٢﴾[النحل: 2]

{Yanã sassaukar da malã'iku da Rũhi daga umurninSaa kan wanda Yake so daga bãyinSa, cẽwa ku yi gargaɗi cẽwa: Lalle ne shĩ, bãbu abin bautãwa fãce Ni, sabõda haka ku bĩ Ni da taƙawa} [al-Nahl: 2] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَإِنَّهُۥ لَتَنزِيلُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٩٢ نَزَلَ بِهِ ٱلرُّوحُ ٱلۡأَمِينُ ١٩٣ عَلَىٰ قَلۡبِكَ لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ١٩٤ بِلِسَانٍ عَرَبِيّٖ مُّبِينٖ ١٩٥ وَإِنَّهُۥ لَفِي زُبُرِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٩٦﴾[الشعراء: 192-196]

{Kuma lalle shi (Alƙur'ãni), haƙĩƙa, saukarwar Ubangijinhalittu ne.(192) Rũhi amintacce ne ya sauka da shi.(193) A zũciyarka, dõmin ka kasance daga mãsu gargaɗi.(194) Da harshe na Larabci mai bayãni.(195) Kuma lalle shin, haƙĩƙa, yanã a cikin litattafan (Manzannin) farko.(196)} [al-Shu'araa: 192-196] Na Uku: Imani da litattan Allah kamar Altaura da Linjila da zabura -kafin a canza su- da kuma imani da Al-qur'ani, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِي نَزَّلَ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِن قَبۡلُۚ وَمَن يَكۡفُرۡ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٣٦﴾ [النساء: 136]

{Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku yi ĩmãni da Allah da Manzonsa, da Littãfin da Ya sassaukar ga ManzonSa da Littãfin nan wanda Ya saukar daga gabãni. To, wanda ya kãfirta da Allah da malã'ikunSa, da LittattafanSa, da ManzanninSa, da Rãnar Lãhira, to, lalle ne yã ɓace, ɓata mai nĩsa} [al-nisa'a: 136] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿نَزَّلَ عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَأَنزَلَ ٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَ ٣ مِن قَبۡلُ هُدٗى لِّلنَّاسِ وَأَنزَلَ ٱلۡفُرۡقَانَۗ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٞۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٞ ذُو ٱنتِقَامٍ ٤﴾ [آل عمران: 3-4]

{Yã sassaukar da Littãfi a gare ka da gaskiya, yana mai gaskatãwa ga abin da ke gaba gare shi, kuma Allah Yã saukar da Attaura da Linjĩlã(3) A gabãni, suna shiryar da mutãne, kuma

Ya saukar da littattafai mãsu rarrabẽwa. Lalle ne waɗanda suka kãfirta da ãyõyin Allah, suna da azãba mai tsanani. Kuma Allah Mabuwayi ne, Ma'abucin azãbar rãmuwa.(4)} [ali-Imran: 3-4] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ وَقَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ غُفۡرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيۡكَ ٱلۡمَصِيرُ٢٨٥﴾[البقرة: 285]

{Manzon Allah yã yi ĩmãni da abin da aka saukar zuwa gare shi daga Ubangijinsa, da mũminai. Kõwanensu yã yi ĩmãni da Allah, da mala'ikunSa, da littattafanSa, da manzanninSa. Bã mu rarrabẽwa a tsakãnin daya daga manzanninSa. Kuma (mũminai) suka ce: "Mun ji kuma mun yi dã'a; (Muna nẽman) gãfararKa, yã Ubangijinmu, kuma zuwa a gare Ka makõma take} [al-Baqara: 285] kuma Allah - Maaukaki - Ya ce Ka ce:

﴿قُلۡ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ٨٤﴾ [آل عمران: 84]

{Kace: Mun yi ĩmãni da Allah kuma da abin da aka saukar mana da abin da aka saukar wa Ibrãhĩma da Isma'ĩla da Is'hãƙa da Yãƙũba da jĩkõki, da abin da aka bai wa Mũsã da Ĩsã da annabãwa daga Ubangijinsu, bã mu bambantãwa a tsakãnin kõwa daga gare su. Kuma mũ, zuwa gare Shi mãsu sallamãwa ne} [Aal Imran: 84] Na hudu: Imani da bai dayan Annabawa da Manzanni - amincin Allah a gare su- saboda ya wajaba ayi imani da baki dayan Annabawa da manzanni – amincin Allah a gare su- da kuma kudurcewa cewa su baki dayan su Manzanni

ne daga Allah don su isarwa da al'umman su saqonnin Allah da AddininSa da shari'arSa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قُولُوٓاْ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَمَآ أُوتِيَ ٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ۝١٣٦﴾[البقرة: 136]

{Kuce: Mun yi ĩmãni da Allah, da abin da aka saukar zuwa gare mu, da abin da aka saukar zuwa ga Ibrãhĩm da Ismã'ĩla da Is'hãka da Ya'ƙũbu da jĩkõki, da abin da aka bai wa Mũsã da Ĩsã, da abin da aka bai wa annabãwa daga Ubangijinsu, bã mu rarrabẽwa a tsakãnin kõwa daga gare su, kuma mu, a gare Shi, mãsu miƙa wuya ne} [al-Baqara: 136] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَـٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ وَقَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ غُفۡرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيۡكَ ٱلۡمَصِيرُ۝٢٨٥﴾[البقرة: 285]

{Manzon Allah yã yi ĩmãni da abin da aka saukar zuwa gare shi daga Ubangijinsa, da mũminai. Kõwanensu yã yi ĩmãni da Allah, da mala'ikunSa, da littattafanSa, da manzanninSa. Bã mu rarrabẽwa a tsakãnin daya daga manzanninSa. Kuma (mũminai) suka ce: "Mun ji kuma mun yi dã'a; (Muna nẽman) gãfararKa, yã Ubangijinmu, kuma zuwa a gare Ka makõma take} [al-Baqara: 285] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿قُلۡ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَمَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا وَمَآ أُنزِلَ عَلَىٰٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ وَيَعۡقُوبَ وَٱلۡأَسۡبَاطِ وَمَآ أُوتِيَ مُوسَىٰ وَعِيسَىٰ وَٱلنَّبِيُّونَ مِن رَّبِّهِمۡ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّنۡهُمۡ وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ۝٨٤﴾[آل عمران: 84]

{Mun yi ĩmãni da Allah kuma da abin da aka saukar mana da abin da aka saukar wa Ibrãhĩma da Isma'ĩla da Is'hãƙa da Yãƙũba da jĩkõki, da abin da aka bai wa Mũsã da Ĩsã da annabãwa daga Ubangijinsu, bã mu bambantãwa a tsakãnin kõwa daga gare su. Kuma mũ, zuwa gare Shi mãsu sallamãwa ne} [Aal Imran: 84] Kuma yayi imani da cikamakin su shi ne Annabi Muhammad Manzon Allah cika makin Annabawa da Manzanni - amincin Allah a gare su-, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَإِذۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ لَمَآ ءَاتَيۡتُكُم مِّن كِتَٰبٖ وَحِكۡمَةٖ ثُمَّ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مُّصَدِّقٞ لِّمَا مَعَكُمۡ لَتُؤۡمِنُنَّ بِهِۦ وَلَتَنصُرُنَّهُۥۚ قَالَ ءَأَقۡرَرۡتُمۡ وَأَخَذۡتُمۡ عَلَىٰ ذَٰلِكُمۡ إِصۡرِيۖ قَالُوٓاْ أَقۡرَرۡنَاۚ قَالَ فَٱشۡهَدُواْ وَأَنَا۠ مَعَكُم مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٨١﴾[آل عمران: 81]

{Kuma a lõkacin da Allah Ya riƙi alkawarin Annabãwa: "Lalle ne ban bã ku wani abu ba daga Littãfi da hikima, sa'an nan kuma wani manzo ya je muku, mai gaskatãwa ga abin da yake tãre da ku; lalle ne zã ku gaskata Shi, kuma lalle ne zã ku taimake shi." Ya ce: "Shin, kun tabbatar kuma kun riƙi alkawarĩNa a kan wannan a gare ku?" suka ce: "Mun tabbatar." Ya ce: "To, ku yi shaida, kuma Nĩ a tãre da ku Inã daga mãsu shaida} [Aal Imran: 81] Saboda Musulunci ya wajabta imani da baki dayan Annabawa da Manzanni baki daya kuma ya wajabta Imani da na qarshen su, shi ne Manzon Allah Muhammad - SAW -, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿قُلۡ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَسۡتُمۡ عَلَىٰ شَيۡءٍ حَتَّىٰ تُقِيمُواْ ٱلتَّوۡرَىٰةَ وَٱلۡإِنجِيلَ وَمَآ أُنزِلَ إِلَيۡكُم مِّن رَّبِّكُمۡۗ... ٦٨﴾[المائدة: 68]

{Kace ya ku ma'abota littafi ku ba komai bane har sai tsaida Al-taura da Linjila da abun da aka saukar gareku daga Ubangijinku} [al-Ma'ida: 68], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿قُلۡ يَـٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَـٰبِ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ كَلِمَةٖ سَوَآءِۭ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمۡ أَلَّا نَعۡبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشۡرِكَ بِهِۦ شَيۡـٔٗا وَلَا يَتَّخِذَ بَعۡضُنَا بَعۡضًا أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِۚ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُولُواْ ٱشۡهَدُواْ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ٦٤﴾[آل عمران: 64]

{Ka ce: "Yã ku Mutãnen Littãfi! Ku tafo zuwa ga kalma mai daidaitãwa a tsakã ninmu da ku; kada mu bauta wa kõwa fã ce Allah. Kuma kada mu haɗa kõme da Shi, kuma kada sãshenmu ya riƙi sãshe Ubangiji, baicin Allah." To, idan sun jũya bã ya sai ku ce: "ku yi shaida cẽwa, lalle ne mu masu sallamã wa ne} [Aal Imran: 64] Kuma duk wanda ya kafurta da Annabi daya to haqiqa ya kafuta da baki dayan Annabawa da Manzanni -amincin Allah a gare su- saboda da haka Allah Ya ce yana mai bada labari game da hukuncinSa ga

﴿كَذَّبَتۡ قَوۡمُ نُوحٍ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٠٥﴾[الشعراء: 105]

{Mutanen annabi Nuhu -Amincin Allah a gare shi- Mutãnen Nũhu sun ƙaryata Manzanni} [al-Shu'araa:105] Kuma abu ne sananne cewa Annabi Nuhu -Amincin Allah a gare shi- babu wani Manzo da ya gabace shi kuma duk da hakan yayin da mutanensa suka qaryata shi wannan qaryatawar ta su ta kasance qaryatawa ne ga baki dayan Annabawa da Manzann; saboda da'awar su daya ce kuma manufar su xaya ce. Na Biyar: Imani da ranar lahira kuma ita ce Ranar Alqiyama kuma a qarshen wannan duniyar ce Allah zai umarci Mala'ika Israfil -amincin Allah a gare shi- sai yai busa busar mutuwa kuma sai duk wanda Allah Ya so mutuwa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِ فَصَعِقَ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَن فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا مَن شَآءَ ٱللَّهُۖ ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخۡرَىٰ فَإِذَا هُمۡ قِيَامٞ يَنظُرُونَ ٦٨﴾[الزمر: 68]

{Kuma aka busa a cikin ƙaho, sai waɗanda ke a cikin sammai da ƙasã suka sũma sai wanda Allah Ya so (rashin sumansa) sa'an nan aka hũra a cikinsa, wata hũrãwa, sai gã su tsaitsaye, sunã kallo} [al-zumar: 68] kuma baki dayan waxanda suke sammai da wadanda suke kasa sai wanda Allah Yaso to lallai cewa Allah zai nade sammai da kasa kamar yadda Madaukaki Ya ce:

﴿يَوۡمَ نَطۡوِي ٱلسَّمَآءَ كَطَيِّ ٱلسِّجِلِّ لِلۡكُتُبِۚ كَمَا بَدَأۡنَآ أَوَّلَ خَلۡقٖ نُّعِيدُهُۥۚ وَعۡدًا عَلَيۡنَآۚ إِنَّا كُنَّا فَٰعِلِينَ ١٠٤﴾[الأنبياء: 104]

{A rãnar da Muke naɗe sãma kamar neɗẽwar takarda ga abũbuwan rubũtãwa kamar yadda Muka fãra a farKon halitta Muke mãyar da ita. Wa'adi ne a Kanmu. Lalle ne Mun kasance Mãsu aikatãwa} [al-anbiya: 104] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦ وَٱلۡأَرۡضُ جَمِيعٗا قَبۡضَتُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ مَطۡوِيَّٰتُۢ بِيَمِينِهِۦۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٦٧﴾[الزمر: 67]

{Kuma ba su ƙaddara Allah a kan haƙĩƙanin ĩkon yinsa ba: ¡asã duka damƙarSa ce, a Rãnar ¡iyãma, kuma sammai abũbuwan naɗewa ne ga dãmanSa. Tsarki ya tabbata a gare Shi, kuma Ya ɗaukaka daga barin abin da suke shirki da shi} [al-zumar: 67] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Allah Madaukaki zai nade sammai da a ranar Al-qiyama sannan Ya daukesu da hannunSa na dama sannan ya ce: Ni ne Mai Mulki ina masu jabberanci? kuma sannan sai nade kasa ma da hannunSa na hagu sannan ya ce: Ni ne Mai Mulki ina masu jabberanci?" Muslim ya rawaito shi. Sannan sai Allah Ya umarci Mala'ika da yai busa ta biyu to yayin nan su zasu tashi suna kallo, Allah - Madaukaki Ya ce:

﴿... ثُمَّ نُفِخَ فِيهِ أُخۡرَىٰ فَإِذَا هُمۡ قِيَامٞ يَنظُرُونَ ٦٨﴾[الزمر: 68]

{Sannan sai ayi Busa acikin Kaho to yayin nan su Alkiyama kawai suke sauraro} [al-zumar: 68] Saboda idan Allah Ya tashi halitta zai tashe su don hisabi, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَوۡمَ تَشَقَّقُ ٱلۡأَرۡضُ عَنۡهُمۡ سِرَاعٗاۚ ذَٰلِكَ حَشۡرٌ عَلَيۡنَا يَسِيرٞ ٤٤﴾[ق: 44]

{Rãnar da ƙasã ke tsattsãgẽwa daga gare su, sunã mãsu gaggãwa. Wancan tãrãwar mutãne ne, mai sauƙi a gare Mu} [Qaaf: 44] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَوۡمَ هُم بَٰرِزُونَۖ لَا يَخۡفَىٰ عَلَى ٱللَّهِ مِنۡهُمۡ شَيۡءٞۚ لِّمَنِ ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَۖ لِلَّهِ ٱلۡوَٰحِدِ ٱلۡقَهَّارِ ١٦﴾[غافر: 16]

{Rãnar da suke bayyanannu, bãbu wani abu daga gare su wanda yake iya bõyuwa ga Allah. "Mulki ga wa ya ke a yau?" Yana ga Allah, Makaɗaici, Mai tĩlastãwa} [Ghafir: 16] Kuma a cikin wannan rana Allah zai yiwa mutane hisabi baki dayansu kuma ya dauki fansa ga wanda aka zalunta daga wanda ya zalunce shi kuma ya sakawa kowane mutum da abunda ya aikata, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿ٱلۡيَوۡمَ تُجۡزَىٰ كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا كَسَبَتۡۚ لَا ظُلۡمَ ٱلۡيَوۡمَۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٧﴾[غافر: 17]

{Yau anã sãka wa kõwane rai a game da abin da ya aikata, bãbu zãlunci a yau. Lalle Allah Mai gaggawar hisãbi ne} [Ghafir: 17], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَظۡلِمُ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖۖ وَإِن تَكُ حَسَنَةٗ يُضَٰعِفۡهَا وَيُؤۡتِ مِن لَّدُنۡهُ أَجۡرًا عَظِيمٗا ٤٠﴾[النساء: 40]

{Lalle ne, Allah bã Ya zãluncin gwargwadon nauyin zarra, idan ta kasance alhẽri ce, zai riɓanya ta, kuma Ya kãwo daga gunsa ijãra mai girma} [al-nisa'a: 40], Kuma Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿فَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٍ خَيۡرٗا يَرَهُۥ ۝٧ وَمَن يَعۡمَلۡ مِثۡقَالَ ذَرَّةٖ شَرّٗا يَرَهُۥ ۝٨﴾[الزلزلة: 7-8]

{To duk wanda ya ya aikata alkairi kwatankwacin kwayar zarra na alkhairi zai ganshi (7) Kuma wanda ya aikata gwargwadon nauyin zarra na sharri, zai gan shi(6)} [al-zalzalah: 7-8] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَنَضَعُ ٱلۡمَوَٰزِينَ ٱلۡقِسۡطَ لِيَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِ فَلَا تُظۡلَمُ نَفۡسٞ شَيۡـٔٗاۖ وَإِن كَانَ مِثۡقَالَ حَبَّةٖ مِّنۡ خَرۡدَلٍ أَتَيۡنَا بِهَاۗ وَكَفَىٰ بِنَا حَٰسِبِينَ ۝٤٧﴾[الأنبياء: 47]

{Kuma Munã aza ma'aunan ãdalci ga Rãnar ¡iyãma, sabõda haka ba a zãluntar rai da kõme. Kuma kõ dã ya kasance nauyin ƙwãya daga kõmayya ne Mun zo da ita. Kuma Mun isa zama Mãsu hisãbi} [al-anbiya'a: 47] Kuma bayan tashin Al-qiyama da hisabi sakamako zaiKasance, saboda duk wanda ya aikata wani alkairi to yana da ni'ima dawwamammiya wacce bata gushewa, kuma duk wanda ya aikata sharri da kafirci to yana da azaba, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ٱلۡمُلۡكُ يَوۡمَئِذٖ لِّلَّهِ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ فِي جَنَّٰتِ ٱلنَّعِيمِ ۝٥٦ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَكَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَأُوْلَٰٓئِكَ لَهُمۡ عَذَابٞ مُّهِينٞ ۝٥٧﴾[الحج: 56-57]

{Mulki a rãnar nan ga Allah yake, Yanã hukunci a tsakãninsu. To, waɗanda suka yi ĩmãni, kuma suka aikata ayyukan ƙwarai, sunã a cikin gidãjen Aljannar ni'ima.(56) Kuma waɗandra suka kãfirta kuma suka ƙaryata, game da ãyõyinMu, to, waɗannan sunã da azãba mai wulãkantarwa.(57)} [al-Hajj: 56-57] Kuma mun san cewa rayuwar duniya da ita ce qarshen rayuwa; da rayuwa da halittu sun zamanto tsantsan wasa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أَفَحَسِبۡتُمۡ أَنَّمَا خَلَقۡنَٰكُمۡ عَبَثٗا وَأَنَّكُمۡ إِلَيۡنَا لَا تُرۡجَعُونَ ۝١١٥﴾[المؤمنون: 115]

{Shin, to, kun yi zaton cẽwa Mun halitta ku ne da wãsa kuma lalle ku, zuwa gare Mu, bã zã ku kõmo ba?} [al-Mua'Munun: 115].

Na Shida: Imani da hukuncin Allah da kaddara kuma shi ne cewa ya wajaba Imani da Allah cewa haqiqa Ya san dukkan abinda ya kasance da kuma wanda zai kasance, a wannan halitta kuma cewa Allah Ya wajabta dukkan wancan kafin ya halicci sammai da kasa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿۞وَعِندَهُۥ مَفَاتِحُ ٱلۡغَيۡبِ لَا يَعۡلَمُهَآ إِلَّا هُوَۚ وَيَعۡلَمُ مَا فِي ٱلۡبَرِّ وَٱلۡبَحۡرِۚ وَمَا تَسۡقُطُ مِن وَرَقَةٍ إِلَّا يَعۡلَمُهَا وَلَا حَبَّةٖ فِي ظُلُمَٰتِ ٱلۡأَرۡضِ وَلَا رَطۡبٖ وَلَا يَابِسٍ إِلَّا فِي كِتَٰبٖ مُّبِينٖ ٥٩﴾[الأنعام: 59]

{Kuma a wurinSa mabũdan gaibi suke, babu wanda yake sanin su fãce Shi, kuma Yanã sanin abin da ke a cikin tudu da ruwa, kuma wani ganye ba ya fãɗuwa, fãce Yã san shi, kuma bãbu wata ƙwãya a cikin duffan ƙasã, kuma babu ɗanye, kuma babu ƙẽƙasasshe, fãce yanã a cikin wani Littãfi mai bayyanãwa} [al-An'am: 59] Haqiqa cewa Allah Ya kewaye dukkan komai da sani, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ٱللَّهُ ٱلَّذِي خَلَقَ سَبۡعَ سَمَٰوَٰتٖ وَمِنَ ٱلۡأَرۡضِ مِثۡلَهُنَّۖ يَتَنَزَّلُ ٱلۡأَمۡرُ بَيۡنَهُنَّ لِتَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ وَأَنَّ ٱللَّهَ قَدۡ أَحَاطَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عِلۡمَۢا ١٢﴾[الطلاق: 12]

{Allah, wanda Ya halitta bakwai ɗin sammai kuma daga ƙasã kwatankwacinsu, umuruinSa yanã ta sauka a tsakaninsu dõmin ku san lalle Allah Mai ĩkon yi ne akan dukan kõme, kuma lalle Allah, haƙĩka Ya kẽwaye ga dukan kõme da sani} [al-Dalaq:12] Kuma cewa shi babu wani abu da zai faru a wannan duniya na wani abu face sai da nufin Allah da kuma da Mashi'arsa, kuma shi ya halicce shi kuma ya sauqaqe sababansa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ٱلَّذِى لَهُۥ مُلۡكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَلَمۡ يَتَّخِذۡ وَلَدٗا وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٞ فِي ٱلۡمُلۡكِ وَخَلَقَ كُلَّ شَيۡءٖ فَقَدَّرَهُۥ تَقۡدِيرٗا٢﴾[الفرقان: 2]

{wanda Yake da mulkin sammai da ƙasa kuma bai riƙi abin haihuwa ba, kuma abõkin tãrayya bai kasance a gare Shi ba a cikin mulkinSa kuma Ya halitta dukan kowane abu, sa'an nan Ya ƙaddara shi ƙaddarãwa} [Al-furqan: 2] Kuma yana babbar hikima cikin yin hakan wacce mututane ba zasu iya saninsu ba. Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿حِكۡمَةُۢ بَٰلِغَةٞۖ فَمَا تُغۡنِ ٱلنُّذُرُ٥﴾[القمر: 5]

{Hikima cikakka! Sai dai abũbuwan gargaɗi bã su amfãni} [al-qamar: 5], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى يَبۡدَؤُاْ ٱلۡخَلۡقَ ثُمَّ يُعِيدُهُۥ وَهُوَ أَهۡوَنُ عَلَيۡهِۚ وَلَهُ ٱلۡمَثَلُ ٱلۡأَعۡلَىٰ فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ٢٧﴾[الروم: 27]

{Kuma Shĩ ne Wanda Ya fãra halitta, sa'an nan Ya sãke ta kuma sakẽwarta tã fi sauƙi a gare shi. Kuma Yanã da misãli wanda ya fi ɗaukaka a cikin sammai da ƙasã kuma Shĩ ne Mabuwãyi, Mai jin ƙai} [al-Rum: 27], Kuma Allah Ya siffanta kansa da hikima kuma Ya kirawo kanSa da Mai hikima, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلۡعِلۡمِ قَآئِمَۢا بِٱلۡقِسۡطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ١٨﴾[آل عمران: 18]

{Allah Ya shaida cẽwa: Lalle ne bãbu abin bautãwa fãce Shi kuma malãiku da ma'abũta ilmi sun shaida, yana tsaye da ãdalci, bãbu abin bautãwa face Shi, Mabuwãyi, Mai hikima} [Aal Imran: 18], Kuma Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce Ya na

bada labarin Annabi Isa -amincin Allah a gare shi- cewaa shi yana magana da Allah Ranar Al-qiyama yana mai cewa:

﴿إِن تُعَذِّبۡهُمۡ فَإِنَّهُمۡ عِبَادُكَۖ وَإِن تَغۡفِرۡ لَهُمۡ فَإِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١١٨﴾[المائدة: 118]

{Idan Ka azabta su, to lalle ne su, bãyinKa ne, kuma idan Ka gãfarta musu, to, lalle ne Kai ne Mabuwayi Mai hikima} [al-Ma'ida: 118] Kuma Allah - Madaukakin sarki - Ya ce Annabi Musa - amincin Allah a gare shi- yayin da ya kirawo shi yana gefen dutsen Al-Dur

﴿يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّهُۥٓ أَنَا ٱللَّهُ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ٩﴾[النمل: 9]

{Yã Mũsã lalle ne shi, Nĩ ne Allah, Mabuwãyi, Mai hikima} [al-Naml: 9]

﴿الٓرۚ كِتَٰبٌ أُحۡكِمَتۡ ءَايَٰتُهُۥ ثُمَّ فُصِّلَتۡ مِن لَّدُنۡ حَكِيمٍ خَبِيرٍ ١﴾[هود: 1]

{Kuma Allah ya siffanta Al-qur'ani maigirma da hikima sai yake cewa: A. L̃.R. Littãfi ne an kyautata ãyõyinsa, sa'an nan an bayyanã su daki-daki, daga wurin Mai hikima, Mai ƙididdigewa} [Hud: 1], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ذَٰلِكَ مِمَّآ أَوۡحَىٰٓ إِلَيۡكَ رَبُّكَ مِنَ ٱلۡحِكۡمَةِۗ وَلَا تَجۡعَلۡ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتُلۡقَىٰ فِي جَهَنَّمَ مَلُومًا مَّدۡحُورًا ٣٩﴾[الإسراء: 39]

{Wancan yãnã daga abin da Ubangijinka Ya yi wahayi zuwa gare ka na hikima. Kuma kada ka sanya wani abin bautãwa na daban tãre da Allah har a jẽfa ka a cikin Jahannama kanã wanda ake zargi, wanda ake tunkuɗẽwa} [al-Isra'a: 39]

**22. kuma Annabwa ma'asumai ne -amincin Allah a gare su- cikin abunda suka isar da shi daga Allah, kuma ma'asumai ne ga barin dukkanin abunda ya saba da hankali, ko kuma kyawawan halaye su kyamace shi, kuma Annabawa an dora musu isar da umarnin Allah ga bayinSa, kuma Annabawa basu da wani abu na abunda ya kebanci Allantaka; aa suma mutane kamar sauran mutane Allah Yayi musu wahayi da Manzantakarsa**

Kuma Annabawa ma'asumai ne -Amincin Allah a gare su- cikin abunda suka isar daga Allah; Saboda Allah Ya zabi zababbun halittarSa don su isar da saqonninsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿ٱللَّهُ يَصۡطَفِي مِنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ رُسُلٗا وَمِنَ ٱلنَّاسِۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعُۢ بَصِيرٞ ٧٥﴾[الحج: 75]

Allah nã zãɓen Manzanni daga malã'iku kuma daga mutãne. Lalle Allah, Mai ji ne, Mai gani} [al-Hajj: 75], kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞إِنَّ ٱللَّهَ ٱصۡطَفَىٰٓ ءَادَمَ وَنُوحٗا وَءَالَ إِبۡرَٰهِيمَ وَءَالَ عِمۡرَٰنَ عَلَى ٱلۡعَٰلَمِينَ ٣٣﴾
[آل عمران: 33]

{Lalle ne Allah Yã zãɓi Ãdama da Nũhu da Gidan Ibrãhĩma da Gidan Imrãna a kan tãlikai} [Aal Imran: 33] kuma Allah - Madaukaki -Ya ce:

﴿قَالَ يَٰمُوسَىٰٓ إِنِّي ٱصۡطَفَيۡتُكَ عَلَى ٱلنَّاسِ بِرِسَٰلَٰتِي وَبِكَلَٰمِي فَخُذۡ مَآ ءَاتَيۡتُكَ وَكُن مِّنَ ٱلشَّٰكِرِينَ ١٤٤﴾[الأعراف: 144]

{Ya Mũsã! Lalle ne Nĩ, Nã zãɓe ka bisa ga mutãne da manzanciNa, kuma da maganãTa. Sabõda haka ka riƙi abin da Nã bã ka, kuma ka kasance daga mãsu gõdiya} [Al-a'araf: 144] Kuma Manzanni -amincin Allah a gare su- sunsan abunda aka

saukar musu na wahayin Allah kuma suna ganin Mala'iku da suke saukar musu da wahayi, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿عَٰلِمُ ٱلۡغَيۡبِ فَلَا يُظۡهِرُ عَلَىٰ غَيۡبِهِۦٓ أَحَدًا٢٦ إِلَّا مَنِ ٱرۡتَضَىٰ مِن رَّسُولٖ فَإِنَّهُۥ يَسۡلُكُ مِنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَمِنۡ خَلۡفِهِۦ رَصَدٗا٢٧ لِّيَعۡلَمَ أَن قَدۡ أَبۡلَغُواْ رِسَٰلَٰتِ رَبِّهِمۡ وَأَحَاطَ بِمَا لَدَيۡهِمۡ وَأَحۡصَىٰ كُلَّ شَيۡءٍ عَدَدَۢا٢٨﴾[الجن: 26-28]

{Shi ɗai ne Masanin fake sabõda haka, bã Ya bayyana gaibinSa ga kowa."(26) "Fãce ga wanda Yã yarda da shi, wato wani manzo sa'an nan lalle ne, zai sanya gãdi a gaba gare shi da bãya gare shi."(27) "Dõmin Ya san lalle, sun iyar da sãƙonnin Ubangijinsu, kuma (Shi Ubangijin) Yã kẽwaye su da sani, kuma Yã lissafe dukan kõme da ƙididdiga (28)} [al-Jinn: 26-28], Kuma Allah Ya umarce su da isar da saqonninsa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿۞يَٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغۡ مَآ أُنزِلَ إِلَيۡكَ مِن رَّبِّكَۖ وَإِن لَّمۡ تَفۡعَلۡ فَمَا بَلَّغۡتَ رِسَالَتَهُۥۚ وَٱللَّهُ يَعۡصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ٦٧﴾[المائدة: 67]

{Yã kai Manzo! Ka iyar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka. Kuma idan ba ka aikata ba, to, ba ka iyar da manzancinSa ba ke nan. Kuma Allah Yanã tsare ka daga mutãne. Lalle ne, Allah bã Ya shiryar da mutãne kãfirai} [al-Ma'ida: 67].

﴿رُّسُلٗا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةُۢ بَعۡدَ ٱلرُّسُلِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا١٦٥﴾[النساء: 165]

{kuma Allah Maxaukaki ya ce Manzanni mãsu bãyar da bushãra kuma mãsu gargaɗi dõmin kada wata hujja ta kasance ga mutãne a kan Allah bãyan Manzannin. Kuma Allah yã kasance Mabuwãyi, Mai hikima} [al-nisa'a: 165], Kuma Manzanni - amincin Allah a gare su- suna tsoron Allah matuqa

jin tsoro kuma suna jin tsoro basa qarin a kan saqonninsa kuma basa ragewa. Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَلَوْ تَقَوَّلَ عَلَيْنَا بَعْضَ ٱلْأَقَاوِيلِ ۝٤٤ لَأَخَذْنَا مِنْهُ بِٱلْيَمِينِ ۝٤٥ ثُمَّ لَقَطَعْنَا مِنْهُ ٱلْوَتِينَ ۝٤٦ فَمَا مِنكُم مِّنْ أَحَدٍ عَنْهُ حَٰجِزِينَ ۝٤٧﴾[الحاقة: 44-47]

{Kuma dã (Muhammadu) yã faɗi wata maganã, yã jingina ta garẽ Mu.(44) Dã Mun kãma shi da dãma.(45) sa'an nan, lalle ne, dã Mun kãtse masa lakã.(46) Kuma daga cikinku bãbu wasu mãsu iya kãre (azãbarMu) daga gare shi.(47)} [Al-Haqah: 44-47] Imam Dan Qayyim - Allah Ya yi masa rahama - ya ce: "Allah - Madauakaki - Ya ce: (kuma da kirkirar karya a gare mu) ai: Muhammad – SAW - kuma da ya kasance kamar yadda suka raya akanmu cewa yayi qari acikin saqon ko tawaya daga cikisu ko kamar yadda wani abu daga gare shi sai ya danganta shi zuwa gare mu kuma abun da ba haka ba da munyi masa gaggawar uquba kuma saboda wannan ya ce (da mun kamashi da damarmu) sai aka ce:

﴿وَإِذْ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَى ٱبْنَ مَرْيَمَ ءَأَنتَ قُلْتَ لِلنَّاسِ ٱتَّخِذُونِي وَأُمِّيَ إِلَٰهَيْنِ مِن دُونِ ٱللَّهِ ۖ قَالَ سُبْحَٰنَكَ مَا يَكُونُ لِيٓ أَنْ أَقُولَ مَا لَيْسَ لِي بِحَقٍّ ۚ إِن كُنتُ قُلْتُهُۥ فَقَدْ عَلِمْتَهُۥ ۚ تَعْلَمُ مَا فِي نَفْسِي وَلَآ أَعْلَمُ مَا فِي نَفْسِكَ ۚ إِنَّكَ أَنتَ عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ۝١١٦ مَا قُلْتُ لَهُمْ إِلَّا مَآ أَمَرْتَنِي بِهِۦٓ أَنِ ٱعْبُدُوا۟ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبَّكُمْ ۚ وَكُنتُ عَلَيْهِمْ شَهِيدًا مَّا دُمْتُ فِيهِمْ ۖ فَلَمَّا تَوَفَّيْتَنِي كُنتَ أَنتَ ٱلرَّقِيبَ عَلَيْهِمْ ۚ وَأَنتَ عَلَىٰ كُلِّ شَيْءٍ شَهِيدٌ ۝١١٧﴾[المائدة: 116-117]

Ma'anarsa da mun munyi masa azaba da damarmu' saboda tafi tsananin kamu kuma aka ce da munkashi da damarSa, kuma Allah - Madaukaki - Ya ce {Kuma ka yuna lokacin da Allah Ya ce da Annabi Isa dan Maryam ko kaine ka ce da mutane ku riqe ni Allaoli biyu koma bayan Allah sai ya ce tsarki ya tabbata

a gareKa ba zai kasance ni fadi abunda ba gaskiya ba ne a gare ni, in nine na fada to haqiqa Ka sani kuma kasan abunda yake cikin raina kuma ni ban san abunda yake cikin ranKa ba, lallai Kai ne Masani fake, ban gaya musu ba sai abunda Ka umarce ni da shi cewa su bautawa Allah Ubangijina kuma Ubangijinku Kuma na kasance mai shaida a lokacin da nake cikin su to yayin da Ka karbi raina Kaine mai gadin su kuma Kai ne Mai shaida akan komai} [al-Maida: 116-117]. Kuma yana dagasarwarsu daga falalar Allah ga AnnabawanSa da ManzanninSa - amincin Allah a gare su- cewa Allah Zai tabbatar da su wajen isarwarsu da sakonninSa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿إِن نَّقُولُ إِلَّا ٱعْتَرَىٰكَ بَعْضُ ءَالِهَتِنَا بِسُوٓءٍۗ قَالَ إِنِّىٓ أُشْهِدُ ٱللَّهَ وَٱشْهَدُوٓاْ أَنِّى بَرِىٓءٌ مِّمَّا تُشْرِكُونَ ۝٥٤ مِن دُونِهِۦۖ فَكِيدُونِى جَمِيعًا ثُمَّ لَا تُنظِرُونِ ۝٥٥ إِنِّى تَوَكَّلْتُ عَلَى ٱللَّهِ رَبِّى وَرَبِّكُمۚ مَّا مِن دَآبَّةٍ إِلَّا هُوَ ءَاخِذٌۢ بِنَاصِيَتِهَآۚ إِنَّ رَبِّى عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ۝٥٦﴾[هود: 54-56]

{ya ce lallai ina shadawa da Allah kuma ku shaida cewa ni na barranta da abunda kuke yin Shirka (54) Koma bayansa saboda haka kuyo mun tanadi baki dayanku sannan kada ku saurara mun (55) "Haƙĩƙa, ni na dõgara ga Allah, Ubangijĩna kuma Ubangijinku. Bãbu wata dabba fãce Shi ne Mai riko ga kwarkwaɗarta. Haƙĩƙa, Ubangijĩna Yanã (kan) tafarki madaidaici} [Hud: 54-56], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَإِن كَادُواْ لَيَفْتِنُونَكَ عَنِ ٱلَّذِىٓ أَوْحَيْنَآ إِلَيْكَ لِتَفْتَرِىَ عَلَيْنَا غَيْرَهُۥۖ وَإِذًا لَّٱتَّخَذُوكَ خَلِيلًا ۝٧٣ وَلَوْلَآ أَن ثَبَّتْنَٰكَ لَقَدْ كِدتَّ تَرْكَنُ إِلَيْهِمْ شَيْـًٔا قَلِيلًا ۝٧٤ إِذًا لَّأَذَقْنَٰكَ ضِعْفَ ٱلْحَيَوٰةِ وَضِعْفَ ٱلْمَمَاتِ ثُمَّ لَا تَجِدُ لَكَ عَلَيْنَا نَصِيرًا ۝٧٥﴾[الإسراء: 73-75]

{Kuma lalle ne sun yi kusa haƙĩka, su fitinẽ ka daga abin da Muka yi wahayi zuwa gare ka, dõmin ka ƙirƙira waninsa a gare

Mu, a lõkacin, haƙĩƙa, dã sun riƙe ka masoyi.(73) Kuma bã dõmin Mun tabbatar da kai ba, lalle ne, haƙĩƙa, dã kã yi kusa ka karkata zuwa gare su ta wani abu kaɗan.(74) A lõkacin, lalle ne, dã Mun ɗanɗana maka ninkin azãbar rãyuwa da ninkin azãbar mutuwa, sa'an nan kuma bã zã ka sãmi mataimaki ba a kanMu.(75)} [al-Isa'a: 73-75] Kuma wadan nan ayoyi da wadan da suka gabace su shaida ne kuma dalili ne kan cewa Al-qur'ani saukakke ne daga Ubangijin talikai; saboda da ya kasance daga Manzo Muhammad - SAW - ne da bai tare wannan zancen da aka fuskantasa zuwa gare shi, Kuma Allah - SWT - Ya kare manzanninSa daga mutane, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞ يَـٰٓأَيُّهَا ٱلرَّسُولُ بَلِّغْ مَآ أُنزِلَ إِلَيْكَ مِن رَّبِّكَ ۖ وَإِن لَّمْ تَفْعَلْ فَمَا بَلَّغْتَ رِسَالَتَهُۥ ۚ وَٱللَّهُ يَعْصِمُكَ مِنَ ٱلنَّاسِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْكَـٰفِرِينَ ﴿٦٧﴾﴾[المائدة: 67]

{Yã kai Manzo! Ka iyar da abin da aka saukar zuwa gare ka daga Ubangijinka. Kuma idan ba ka aikata ba, to, ba ka iyar da manzancinSa ba ke nan. Kuma Allah Yanã tsare ka daga mutãne. Lalle ne, Allah bã Ya shiryar da mutãne kãfirai} [al-Ma'ida: 67] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿۞ وَٱتْلُ عَلَيْهِمْ نَبَأَ نُوحٍ إِذْ قَالَ لِقَوْمِهِۦ يَـٰقَوْمِ إِن كَانَ كَبُرَ عَلَيْكُم مَّقَامِى وَتَذْكِيرِى بِـَٔايَـٰتِ ٱللَّهِ فَعَلَى ٱللَّهِ تَوَكَّلْتُ فَأَجْمِعُوٓا۟ أَمْرَكُمْ وَشُرَكَآءَكُمْ ثُمَّ لَا يَكُنْ أَمْرُكُمْ عَلَيْكُمْ غُمَّةً ثُمَّ ٱقْضُوٓا۟ إِلَىَّ وَلَا تُنظِرُونِ ﴿٧١﴾﴾[يونس: 71]

{Kuma ka karanta musu lãbãrin Nũhu, a lõkacin da ya ce wa mutãnensa, "Ya mutãnẽna! Idan matsayĩna da tunãtarwata ameda ãyõyin Allah sun kasance sun yi nauyi a kanku, to, ga Allah na dõgara. Sai ku tãra al'amarinku, kũ da abũbuwan

shirkinku, sa'annan kuma kada al'amarinku ya kasance rufaffe a kanku, sa'an nan kuma ku kashe ni, kada ku yi mini jinkiri} [Yunus: 71], Kuma Allah Maxaukaki yana bada Labarin Annabi Musa -Amincin Allah a gare shi-

﴿قَالَا رَبَّنَآ إِنَّنَا نَخَافُ أَن يَفۡرُطَ عَلَيۡنَآ أَوۡ أَن يَطۡغَىٰ ٤٥ قَالَ لَا تَخَافَآۖ إِنَّنِي مَعَكُمَآ أَسۡمَعُ وَأَرَىٰ ٤٦﴾[طه: 45-46]

{Suka ce Ubangijinmu lallai mu muna jin tsoro kada ya yi banza da mu ko kuma yayi mana shishigi, Ya ce kada kuji tsoro lallai Ni ina tare da ku ina jio kuma ina gani} [Daha: 45-46] Sai Allah - SWT - Yayi bayanin kiyayewarsa ga ManzanninSa -amincin Allah a gare su- daga abokan gabarsu basa taba iya cimmusu da wata cuta kuma Allah - SWT - Ya bada labarin cewa shi yana kiyaye wahayinSa ba'a iya qari a cikin ko rage wani abu daga ciki, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿إِنَّا نَحۡنُ نَزَّلۡنَا ٱلذِّكۡرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ٩﴾[الحجر: 9]

{Lalle Mũ ne, Muka saukar da Ambato (Alƙur'ãni), kuma lale Mũ, haƙĩƙa, Mãsu kiyayẽwane gare shi} [al-Hijr: 9] Kuma Annabawa -amincin Allah a gare su- ma'asumai ne daga dukkan abunda ya sabawa hankali ko kyawawan halaye, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce Yana mai tsarkake su:

﴿وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٖ ٤﴾[القلم: 4]

{lalle haƙiƙa kana a kan hãlãyen kirki, manya} [al-qalam: 4] Kuma Ya ce dai:

﴿وَمَا صَاحِبُكُم بِمَجۡنُونٖ ٢٢﴾[التكوير: 22]

{Kuma abokinku ba mahaukaci ba ne} [al-Takweer: 22] Kuma wancan don su iya isar da saqon a mafi Al-kairin tsayuwa kuma Annabawa - amincin Allah a gare su- sune wadan da a dora musu nauyin isar da umarnin Allah ga bayinSa wanda basu da wani abu na daga abunda ya kevanci Allantaka ba aa su mutane ne kamar sauran mutane Allah Yana yi musu wahayi da saqonninsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قَالَتْ لَهُمْ رُسُلُهُمْ إِن نَّحْنُ إِلَّا بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ يَمُنُّ عَلَىٰ مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦ ۖ وَمَا كَانَ لَنَآ أَن نَّأْتِيَكُم بِسُلْطَٰنٍ إِلَّا بِإِذْنِ ٱللَّهِ ۚ وَعَلَى ٱللَّهِ فَلْيَتَوَكَّلِ ٱلْمُؤْمِنُونَ ﴿١١﴾﴾[إبراهيم: 11]

{Manzanninsu suka ce musu, "Bã mu zama ba fãce mutãne misã, linku, kuma amma Allah Yanã yin falala a kan wanda Yake so daga bãyinsa, kuma bã ya kasancẽwa a gare mu, mu zo muku da wani dalĩli fãce da iznin Allah. Kuma ga Allah sai mũminai su dõgara} [Ibrahim: 11], Kuma Allah - Madaukakin sarki - Ya ce Yana Mai Umartar Manzonsa Muhammad SAW kan ya cewa Mutanensa::

﴿قُلْ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰٓ إِلَيَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ ۖ فَمَن كَانَ يَرْجُوا۟ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلْيَعْمَلْ عَمَلًا صَٰلِحًا وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدًۢا ﴿١١٠﴾﴾[الكهف: 110]

{Ka ce: "Nĩ, mutum ne kawai kamarku, anã yin wahayi zuwa gare ni cewa: Lalle ne, Abin bautawarku, Abin bautawa Guda ne, sabõda haka wanda ya kasance yanã fãtan haɗuwa da Ubangijinsa, to, sai ya yi aiki na ƙwarai. Kuma kada ya haɗa kõwa ga bauta wa Ubangijinsa} [al-Kahf: 110].

**23. Kuma Musulunci yana kira zuwa ga bautar Allah Shi kadai da ginshiqan ibada manya, sune Sallah wacce ita ce tsayuwa da ruku'u da sujjada da ambaton Allah da yabonSa da kuma addu'a, kuma mutum yana sallatarta sau biyar a wuni, kuma a cikinta babu banbanci tsakanin mawadaci da talaka da shugaba da kuma talaka a sahu kwara daya a cikin sallah da kuma zakka wacce taje wani yanki ne kadan daga cikin dukiya - daidai da sharadai da kuma gwargwado wanda Allah Ya kaddara,kuma tana wajaba ne a dukiyar mawadata kuma a bada ita ga talakawa da wasunsu, kuma sau daya ce a shekara, da kuma azumi wanda shi ne kamewa ga barin ci da sha da rana a watan azumi, kuma yana koyawa mutum dauriya da haquri, da kuma hajji wanda shi ne: Nufar dakin Allah a Makka mai Alfarma sau daya a rayuwa ga mai Iko wanda zai iya, kuma a cikin wannan hajjin akwai daidaito ga kowa da kowa wajen fuskanta zuwa ga mahalicci – SWT - kuma banbance banbance da nuna wani fifiko duka ya kau a cikin sa.**

Musulunci yana kira ziwa bautar Allah da manya manyan ibadu haka da wasun su na ibadu kuma wadan nan ibadu masu girma haqiqa Allah Ya wajabta su a kan kowane Annabi da Manzanni -amincin Allah a gare su- kuma mafi girman Ibadu sune:

Na farko: Sallah Allah Ya farlantata akan musulmai kamar yadda Ya farlantata akan sauran Annabawa da Manzanni -amincin Allah a gare su- kuma Allah Ya umarci AnnabinSa Ibrahim - amincin Allah a gare shi- cewa ya tsarkake shi ga masu dawafi da masu sallah da ruku'u da sujada, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَإِذۡ جَعَلۡنَا ٱلۡبَيۡتَ مَثَابَةٗ لِّلنَّاسِ وَأَمۡنٗا وَٱتَّخِذُواْ مِن مَّقَامِ إِبۡرَٰهِـۧمَ مُصَلّٗىۖ وَعَهِدۡنَآ إِلَىٰٓ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ أَن طَهِّرَا بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡعَٰكِفِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ ١٢٥﴾[البقرة: 125]

{Kuma a lõkacin da Muka sanya dakin Allah ya zama urin zama ga mutãne, da aminci, kuma ku riƙi wurin salla daga Maƙãmu Ibrãhĩm, kuma Muka dau alƙawari daga Ibrãhĩm, da Ismã'ila da cẽwa: "Ku tsarkake dãki Na dõmin mãsu ɗawãfi da mãsu E'itikafi da mãsu rukũ'i, mãsu sujada} [al-Baqara: 125] Kuma Allah Ya wajabtatata akan Annabi Musa afarkon kiran da yayiwa Annabi Musa - amincin Allah a gare shi-, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنِّيٓ أَنَا۠ رَبُّكَ فَٱخۡلَعۡ نَعۡلَيۡكَ إِنَّكَ بِٱلۡوَادِ ٱلۡمُقَدَّسِ طُوٗى ١٢ وَأَنَا ٱخۡتَرۡتُكَ فَٱسۡتَمِعۡ لِمَا يُوحَىٰٓ ١٣ إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدۡنِي وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِذِكۡرِيٓ ١٤﴾[طه: 12-14]

{Lalle ne, Nĩ ne Ubangijnka, sai ka ɗẽbe takalmanka Lalle ne kanã a rãfin nan abin tsarkakẽwa, ¦uwa."(12) "Kuma Nĩ Nã zãɓe ka. Sai ka saurãra ga abin da ake yin wahayi."(13) "Lalle, Nĩ Ni ne Allah. Bãbu abin bautawa fãce Ni. Sai ka bauta Mini, kuma ka tsayar da salla dõmin tuna Ni(14)} [Daha: 12-14] Kuma Annabi Isa - amincin Allah a gareshi- ya bada labarin cewa Allah Ya umarce shi da sallah da zakka kamar yadda Allah - Madaukaki - Ya fada:

﴿وَجَعَلَنِي مُبَارَكًا أَيۡنَ مَا كُنتُ وَأَوۡصَٰنِي بِٱلصَّلَوٰةِ وَٱلزَّكَوٰةِ مَا دُمۡتُ حَيّٗا ٣١﴾[مريم: 31]

{Kuma Yã sanya ni mai albarka a inda duk na kasance kuma Ya umurce ni da yin salla da zakka matuƙar inã da rai} [Maryam: 31] Kuma Sallah a Musulunci ita ce tsayuwa da ruku'u da sujjada da ambaton Allah da yabonSa da kuma addu'a, mutum zai sallace ta ne sau biyar a rana, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿حَـٰفِظُواْ عَلَى ٱلصَّلَوَٰتِ وَٱلصَّلَوٰةِ ٱلۡوُسۡطَىٰ وَقُومُواْ لِلَّهِ قَٰنِتِينَ٢٣٨﴾[البقرة: 238]

{Ku tsare lõkatai a kan sallõli da salla mafificiya. Kuma ku tsayu kuna mãsu ƙanƙan da kai ga Allah} [al-Baqara: 238], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَ لِدُلُوكِ ٱلشَّمۡسِ إِلَىٰ غَسَقِ ٱلَّيۡلِ وَقُرۡءَانَ ٱلۡفَجۡرِۖ إِنَّ قُرۡءَانَ ٱلۡفَجۡرِ كَانَ مَشۡهُودٗا٧٨﴾[الإسراء: 78]

{Ka tsayar da salla a karkatar rãnã zuwa ga duhun dare da lõkacin fitar alfijir lalle ne karãtun fitar alfijir ya kasance wanda ake halarta} [al-Isra'a: 78] kuma Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Amma aruku'u to ku girmama Ubangiji a cikinsa. Ita kuma sujjada, to ku yi kokari matukar kokari wajen addu'a a cikinta, lallai ya dace a amsa muku". Sahih Muslim.

Na biyu: Zakka Allah ya farlanta ta ga musulmai kamar yadda Ya farlantata ga Annabawa da Manzanni da suka gabata - amincin Allah a gare su- kuma ita wani gwargwado ne kadan daga cikin dukiya -daidai da sharadai da kuma wani ma'auni da Allah Ya qaddara shi- kuma wajibi ce a cikin dukiyar mawadata da zasu riqa bayarwa ga talakawa da wasunsu sau daya a shekara, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿خُذۡ مِنۡ أَمۡوَٰلِهِمۡ صَدَقَةٗ تُطَهِّرُهُمۡ وَتُزَكِّيهِم بِهَا وَصَلِّ عَلَيۡهِمۡۖ إِنَّ صَلَوٰتَكَ سَكَنٞ لَّهُمۡۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ١٠٣﴾[التوبة: 103]

{Ka karɓi sadaka daga dũkiyõyinsu kana tsarkake su, kuma kana tabbatar da kirkinsu da ita. Kuma ka yi musu addu'a. Lallai addu'õ'inKa natsuwã ne a gare su. Kuma Allah ne Mai ji, Masani} [al-Taubah: 103] Kuma yayin da Annabi SAW ya aika Mu'az -Allah ya yarda da shi zuwa Yamen ya ce da shi: "wata

rana muna zaune a wajen manzon Allah - SAW - wata rana sai wani mutum ya bullo mana, mai tsananin farin kaya mai tsananin baqin gashin kai kuma ba'a ganin alamar tafiya tare da shi kuma babu wanda ya san shi daga cikin mu, har ya zauna a gaban Manzon Allah - SAW - sannan ya jingina guiwoyinsa zuwa Guiwoyinsa sannan ya dora hannayensa akan cinyoyinsa kuma ya ce: ya Muhammad bani labarin game da Musulunci sai Manzon Allah - SAW - ya ce: ka tsaida sallah ka bada zakka kuma kayi Azumin watan Ramadana da hajjatar dakin Allah idan kasamu Iko" ya ce: Kayi gaskiya ya ce: Sai muka yi mamaki yana tambayarsa kuma yana gasgatashi ya ce: to ka bani labari game da Imani ya ce: "Ka yi Imani da Allah da Mala'ikunSa da litattafanSa da ManzanninSa da ranar lahira da imani da kaddara AlkairinSa da sharrinSa" ya ce: kayi gaskiya, ya ce: to ka bani labarin kyautatawa ya ce: "ka bautawa Allah kamar kana ganinSa saboda in baka ganinSa shi yana ganinka" Tirmizi da Ahmad sun rawaito shi (625).

Na uku: Azumi Allah Ya wajabta shi kan Musulmai kamar yadda Ya farlanta shi ga Annabawa da Manzanni - amincin Allah a garesu-, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ كُتِبَ عَلَيْكُمُ ٱلصِّيَامُ كَمَا كُتِبَ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكُمْ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ ١٨٣﴾[البقرة: 183]

{Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! An wajabta azumi a kanku kamar yadda aka wajabta shi a kan waɗanda suke daga gabãninku, tsammãninku, zã ku yi taƙawa} [al-Baqara: 183] Kuma shi ne: Kamewa ga barin ci da sha a ranar watan Ramadana, kuma Azumi yana renon haquri da juriya a zuciya. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya

ce: "Allah - Madaukakin Sarki - Yana cewa: Azumi nawa ne, kuma Nine zanyi sakamako da shi saboda ya bar sha'awarsa da cinsa da shansa saboda ni kuma azumi garkuwa ne, kuma mai azumi yana da farin ciki guda biyu: Farin ciki lokacin da zai bude baki da farin ciki lokacin da zai gamu da Ubangijinsa" Sahih Al-Bukhari: 7492.

Na Hudu: Hajji, Allah Ya farlanta shi ne ga Musulmai kamar yadda yadda Allah Ya farlanta shi ga Annabawa da Manzanni da suka gabata -amincin Allah a gare su- cewa yayi kira a lokacin aikin Hajji, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَأَذِّن فِى ٱلنَّاسِ بِٱلْحَجِّ يَأْتُوكَ رِجَالًا وَعَلَىٰ كُلِّ ضَامِرٍ يَأْتِينَ مِن كُلِّ فَجٍّ عَمِيقٍ ۝٢٧﴾[الحج: 27]

{Kuma ka yi yẽkuwa ga mutãne da wajabcin Hajji su je maka suna mãsu tafiya da ƙafãfu da kuma a kan kõwane maɗankwarin rãƙumi mãsu zuwa daga kõwane rango mai zurfi} [al-Hajj: 27] Kuma Ya umarce shi da ya tsarkake dakin Allah ga alhazai sai Ya ce:

﴿وَإِذْ بَوَّأْنَا لِإِبْرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلْبَيْتِ أَن لَّا تُشْرِكْ بِى شَيْـًٔا وَطَهِّرْ بَيْتِىَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلْقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ ۝٢٦﴾[الحج: 26]

{Kuma a lõkacin da Muka iyãkance wa Ibrãhim wurin ¦akin (Muka ce masa), "Kada ka haɗa kõme da Ni ga bauta, kuma ka tsarkake ¦ãkiNa dõmin mãsu ɗawãfi da mãsu tsayuwa da mãsu ruku'u da mãsu sujada} [al-Hajj 26] Kuma Hajji shi ne fuskantar dakin Allah a Makkah mai girma ga ayyuka sanannu sau daya a rayuwa ga mai iko, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿فِيهِ ءَايَٰتٌۢ بَيِّنَٰتٌ مَّقَامُ إِبْرَٰهِيمَ ۖ وَمَن دَخَلَهُۥ كَانَ ءَامِنًا ۗ وَلِلَّهِ عَلَى ٱلنَّاسِ حِجُّ ٱلْبَيْتِ مَنِ ٱسْتَطَاعَ إِلَيْهِ سَبِيلًا ۚ وَمَن كَفَرَ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ عَنِ ٱلْعَٰلَمِينَ ۝٩٧﴾[آل عمران: 97]

{Kuma Allah ya wajabta Hajjatar dakinSa ga wanda ya samu ikon haka, kuma duk wanda ya Kafirce to lallai Allah Mawadaci ne ga barin talikai} [Aal Imran: 97] Kuma a cikin Hajji alhazai musulmai sukan taru a waje daya suna masu tsarkake ibada ga Allah Mahalicci kuma baki dayan Alhazai suna yin aikin Hajji hanya iri daya wacce take kore banbancen gari ko Ilimi ko matsayin rayuwa.

**24. kuma daga cikin mafi girman abunda ibada ta kebanta da shi a Musulunci cewa yadda ake yinta da lokutanta da sharuddanta Allah – SWT - ne Ya shar'anta ta su kuma Ya isar da ita ga Manzonsa – SAW - kuma babu wani mutum da yayi shigege a cikin su ta hanyar kari ko ragi har zuwa wannan rana, kuma baki dayan manyan ibadu baki dayan Annabwa sunyi kira zuwa gare su - amincin Allah a gare su-**

24. kuma daga cikin mafi girman abunda ibada ta kebanta da shi a Musulunci cewa yadda ake yinta da lokutanta da sharuddanta Allah - SWT - ne Ya shar'anta ta su kuma Ya isar da ita ga ManzonSa – SAW - kuma babu wani mutum da ya da yayi shigege a cikin su ta hanyar qari ko ragi har zuwa wannan rana, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿...ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ...٣﴾ [المائدة: 3]

{Yau ne na cika muku Addininku kuma na cika ni'amata a gare ku kuma na yarje muku cewa Musulunci shi ne Addini} [Al-Maa'ida: 3]. Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿فَٱسۡتَمۡسِكۡ بِٱلَّذِيٓ أُوحِيَ إِلَيۡكَۖ إِنَّكَ عَلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ٤٣﴾[الزخرف: 43]

{Sabõda haka, ka yi riƙo ga abin da aka yi wahayi da shi zuwa gaie ka. Lalle ne kai, kanã a kan hanya madaidaiciyl} [al-zukhruf: 43], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce game da Mushrikai:

﴿فَإِذَا قَضَيْتُمُ ٱلصَّلَوٰةَ فَٱذْكُرُواْ ٱللَّهَ قِيَٰمًا وَقُعُودًا وَعَلَىٰ جُنُوبِكُمْۚ فَإِذَا ٱطْمَأْنَنتُمْ فَأَقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَۚ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ كَانَتْ عَلَى ٱلْمُؤْمِنِينَ كِتَٰبًا مَّوْقُوتًا ١٠٣﴾[النساء: 103]

{Sa'an nan idan kun ƙãre salla, to ku ambaci Allah tsaye da zaune da a kan sãsanninku. Sa'an nan idan kun natsu, to, ku tsayar da Salla. Lalle ne salla tã kasance a kan mũminai, farilla mai ƙayyadaddun lõkuta} [al-Nisa'a: 103], Allah - Madaukakin sarki - Ya ce dangane da waxanda za'a bawa Zakkah:

﴿۞ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلْفُقَرَآءِ وَٱلْمَسَٰكِينِ وَٱلْعَٰمِلِينَ عَلَيْهَا وَٱلْمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمْ وَفِي ٱلرِّقَابِ وَٱلْغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبْنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةً مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ٦٠﴾[التوبة: 60]

{Abin sani kawai, dũkiyõyin sadaka na faƙĩrai ne da miskinai da mãsu aiki a kansu, da waɗanda ake lallãshin zukãtansu, kuma a cikin fansar wuyõyi, da mabarta, da a cikin hanyar Allah da ɗan hanya (matafiyi). Farilla daga Allah. Kuma Allah ne Masani, Mai hikima} [al-Taubah: 60], Allah - Ta'ala - Ya ce akan Azumi:

﴿شَهْرُ رَمَضَانَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ فِيهِ ٱلْقُرْءَانُ هُدًى لِّلنَّاسِ وَبَيِّنَٰتٍ مِّنَ ٱلْهُدَىٰ وَٱلْفُرْقَانِۚ فَمَن شَهِدَ مِنكُمُ ٱلشَّهْرَ فَلْيَصُمْهُۖ وَمَن كَانَ مَرِيضًا أَوْ عَلَىٰ سَفَرٍ فَعِدَّةٌ مِّنْ أَيَّامٍ أُخَرَۗ يُرِيدُ ٱللَّهُ بِكُمُ ٱلْيُسْرَ وَلَا يُرِيدُ بِكُمُ ٱلْعُسْرَ وَلِتُكْمِلُواْ ٱلْعِدَّةَ وَلِتُكَبِّرُواْ ٱللَّهَ عَلَىٰ مَا هَدَىٰكُمْ وَلَعَلَّكُمْ تَشْكُرُونَ ١٨٥﴾ [البقرة: 185]

{Watan Ramalãna ne wanda aka saukar da Alƙur'ãni a cikinsa yana shiriya ga mutãne da hujjõji bayyanannu daga shiriya da rarrabẽwa. To, wanda ya halarta daga gare ku a watan, sai ya azumce shi, kuma wanda ya kasance majinyaci ko kuwa a kan tafiya, sai ya biya adadi daga wasu kwanuka na dabam. Allah Yana nufin sauƙi gare ku, kuma ba Ya nufin tsanani gare ku, kuma dõmin ku cika adadin, kuma dõmin ku girmama Allah a kan Yã shiryar da ku, kuma tsammãninku, zã ku gõde} [al-Bakara, aya ta: 185]. Allah - Madaukaki - Ya ce game da Hajji:

﴿ٱلۡحَجُّ أَشۡهُرٞ مَّعۡلُومَٰتٞۚ فَمَن فَرَضَ فِيهِنَّ ٱلۡحَجَّ فَلَا رَفَثَ وَلَا فُسُوقَ وَلَا جِدَالَ فِي ٱلۡحَجِّۗ وَمَا تَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ يَعۡلَمۡهُ ٱللَّهُۗ وَتَزَوَّدُواْ فَإِنَّ خَيۡرَ ٱلزَّادِ ٱلتَّقۡوَىٰۖ وَٱتَّقُونِ يَٰٓأُوْلِي ٱلۡأَلۡبَٰبِ ١٩٧﴾ [البقرة: 197]

{Hajji watanni ne sanannu. To, wanda ya yi niyyar hajji a cikinsu to bãbu jimã'i kuma bãbu fãsiƙanci, kuma bãbu jãyayya a cikin hajji. Kuma abin da kuka aikata daga alhẽri, Allah Ya san shi. Kuma ku yi guzuri. To, mafi alhẽrin guzuri yin taƙawa. Kuma ku bi Ni da taƙawa, ya ma'abuta hankula} [al-Baqara: 197] Kuma dukkan wadan nan ibadu masu girma dukkanin Annawa sunyi kira zuwa gare su.

**25, Manzon Musulunci shi ne Muhammad Bn Abdullahi daga cikin zuriyar Annabi Isma'ila dan Annabi Ibrahim - amincin Allah a garesu- an haife shi Makka a shekara ta 571 Miladiyya, kuma yayi hijita zuwa Madina, kuma baiyi tarayya da mutanensa ba a al’amuran bautar gunki, sai dai shi ya kasance yana tarayya da su a ayyukan kirki, kuma ya kasance kan kyawawan halaye tun kafin a aiko shi, kuma mutanensa sun kasance suna kiransa amintacce, kuma Allah Ya aiko shi yayin da ya cika shekara Arba'in kuma Allah Ya karfafe shi da ayoyi (Mu'ajizozi) masu girma, kuma girmansu shi ne Al-qur'ani mai girma, kuma shi ne mafi girman ayoyin Annabawa, kuma shi ne ayoyin Annabwa har zuwa yau din nan, kuma yayin da Allah Ya cika wannan Addinin, kuma Manzon Allah - SAW - ya isar da shi matuqar isarwa sai ya yi wafati she karunsa suna sittin da uku, kuma aka binne shi a garin Madina - SAW - kuma manzon Allah Muhammad - SAW - shine cika makin Annabawa da Manzanni Allah Ya aiko shi da shiriya da Addini na gaskiya don**

**ya fitar da mutane daga duhun bautar gumaka da kafirci da jahilci zuwa hasken kadaita Allah da imani, da kuma Allah Yayi masa shida cewa shi ne ya aiko shi yana mai kira zuwa gare Shi da umarninSa**

Manzon Musulunci shi Muhammad Bn Abdullahi daga zuriyar Isma'il Bn Ibrahim - amincin Allah a gare shi- kuma an haife shi a Makkah a shekara ta 571 Miladiyya, kuma an aiko shi a cikinta kuma yayi hijira zuwa Madina kuma mutanensa suna kiransa amintacce, kuma bai taba tarayya da mutanensa ba cikin al'amuran bautar gumaka sai dai shi ya kasance yana tarayya yare da su a cikin ayyukan alkairi kuma ya kasance akan kyawawan dabi'u masu girma kafin a aiko shi kuma ya siffanta shi da manyan kyawan dabiu sai Allah - Madaukaki Ya ce game da shi:

﴿وَإِنَّكَ لَعَلَىٰ خُلُقٍ عَظِيمٍ ٤﴾[القلم: 4]

{Kuma, lalle haƙiƙa kana a kan hãlãyen kirki, manya} [al-Qalam: 4] Kuma yayin da ya cika shekara arba'in Allah Ya aiko shi kuma Ya qarfafeshi da ayoyi (Mu'ajizozi) masu girma kuma mafi girmansu shi ne Al-qur'ani mai girma Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: Babu wani Annabi daga cikin Annabawa face an bashi daga cikin ayoyi wadanda mutane zasuyi imani da shi ni kuma abinda aka bani shi ne wahayi, Allah Yana yi min wahayi ina fatan na fisu mabiya ranar tashin Alqiyama Sahih Al-Bukhari, Kuma Al-qur'ani mai girma shi wahayin Allah ne zuwa ga manzonSa - SAW -, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce game da shi:

﴿ذَٰلِكَ ٱلۡكِتَٰبُ لَا رَيۡبَۛ فِيهِۛ هُدٗى لِّلۡمُتَّقِينَ ٢﴾[البقرة: 2]

{wancan littafi ne wanda babu kokwantoa cikinsa kuma cikinsa akwai shiriya ga Masu jin tsoron Allah} [al-baqara: 2], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلْقُرْءَانَۚ وَلَوْ كَانَ مِنْ عِندِ غَيْرِ ٱللَّهِ لَوَجَدُواْ فِيهِ ٱخْتِلَٰفًا كَثِيرًا ۝٨٢﴾ [النساء: 82]

{Shin, bã su kula da Alƙur'ãni, kuma dã yã kasance daga wurin wanin Allah haƙĩƙa, dã sun sãmu, a cikinsa, sãɓã wa jũnamai yawa?} [al-Nisa'a: 82] Kuma Allah Ya qure aljannu da mutane kan su zo kwatankwacinsa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿قُل لَّئِنِ ٱجْتَمَعَتِ ٱلْإِنسُ وَٱلْجِنُّ عَلَىٰٓ أَن يَأْتُواْ بِمِثْلِ هَٰذَا ٱلْقُرْءَانِ لَا يَأْتُونَ بِمِثْلِهِۦ وَلَوْ كَانَ بَعْضُهُمْ لِبَعْضٍ ظَهِيرًا ۝٨٨﴾ [الإسراء: 88]

{Ka ce: "Lalle ne idan mutãne da aljannu sun tãru a kan su zo da misãlin wan nan Alƙur'ãni bã zã su zo da misãlinsa ba, kuma kõ dã sãshinsu yã kasance, mataimaki ga sãshi} [al-Israa: 88] Kuma Ya kure su kan su zo da surori goma kamarsa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُۖ قُلْ فَأْتُواْ بِعَشْرِ سُوَرٍ مِّثْلِهِۦ مُفْتَرَيَٰتٍ وَٱدْعُواْ مَنِ ٱسْتَطَعْتُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ۝١٣﴾ [هود: 13]

{Kõ sunã cewa: "Yã ƙirƙira shi ne."Ka ce: "Sai ku zo da sũrõri gõma misãlinsa ƙirƙirarru, kuma ku kirãyi wanda kuke iyãwa, baicin Allah, idan kun kasance mãsu gaskiya} [Hud: 13] Kuma Ya qure su kan su zo da surori goma kamarsa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَإِن كُنتُمْ فِي رَيْبٍ مِّمَّا نَزَّلْنَا عَلَىٰ عَبْدِنَا فَأْتُواْ بِسُورَةٍ مِّن مِّثْلِهِۦ وَٱدْعُواْ شُهَدَآءَكُم مِّن دُونِ ٱللَّهِ إِن كُنتُمْ صَٰدِقِينَ ۝٢٣﴾ [البقرة: 23]

{Idan kun kasance cikin kokkwanton abunda muka saukarwabawanmu to kuzo da sura kwara daya kwatankwacinta kuma ku kirawo shaidunku koma bayan Allah indai kunkasan ce masu gaskiya} [al-Baqara: 23].

Kuma Al-qur'ani mai girma shine aya kwaya daya matabbaciya daga cikin mu'ajizozin Annabawa har zuwa yau kuma yayin da Allah Ya cikawa Manzo - SAW - Addini kuma Ya isar da shi matuqar isarwa sai manzon Allah – SAW - yayi wafati kuma shekararsa tana sittin da uku, kuma ka binne shi a birnin Madina – SAW -.

Kuma Manzon Allah Muhammad - SAW - shine cika makin Annabawa da manzanni, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿مَّا كَانَ مُحَمَّدٌ أَبَآ أَحَدٍ مِّن رِّجَالِكُمۡ وَلَٰكِن رَّسُولَ ٱللَّهِ وَخَاتَمَ ٱلنَّبِيِّـۧنَۗ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمًا ٤٠﴾[الأحزاب: 40]

{Muhammadu bai kasance uban kõwa ba daga mazanku, kuma amma shĩ yã kasance Manzon Allah kuma cikon Annabãwa. Kuma Allah Ya kasance Masani ga kõme} [al-Ahzab: 40] Da hadisin Abi Huraira - Allah Ya yarda dashi - daga Manzon Allah - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Lallai ni kwatankwacina da sauran Annabawa da suka gabaceni kamar mutum ne da ya gina gida sai ya kyautatashi yai masa qawa sai wurin bulo daya a wani lungu sai mutane suka riqa kewaye shi suna mamakinsa suna cewa ina ma za'a saka wannan bulo din ? to ni ne wannan bulo din kuma ni ne cika makin Annabawa" Sahih Al-Bukhari. Kuma a cikin linjila Annabi Isa - amincin Allah a gare shi- yayi bushara da Manzon Allah - SAW - (Dutsen wanda masu gini suka qi ginawa shi ne ya isa kan zawiyyar baku karanta ba a cikin litattafai: Yasu'a ya ce

da su daga Ubangiji wannan yake kuma shi abun mamaki ne a Idanuwan mu) kuma a cikin Sifirn Al-taura wacce ake samu a yau kuma a cikinta fadin Annabi Musa - amincin Allah a gare shi: (San samar musu da Annabi a cikin su kamarka kuma na sanya magana ta a cikin bakinsa sai yayi magana da su da baki dayan abunda nayi masa wasiyya da shi) Kuma Manzon Allah Muhammad - SAW - Allah Ya aiko shi da shiriya da kuma Addinin gaskiya kuma Allah Yayi masa shaida da cewa shi yana kan gaskiya kuma cewa Shine Ya aiko shi yana mai kira zuwa gare Shi da umarninSa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿لَّٰكِنِ ٱللَّهُ يَشْهَدُ بِمَآ أَنزَلَ إِلَيْكَ أَنزَلَهُۥ بِعِلْمِهِۦ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ يَشْهَدُونَ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ١٦٦﴾[النساء: 166]

{Amma Allah Yanã shaida da abin da Ya saukar zuwa gare ka. Yã saukar da shi da saninSa. Kuma malã'iku sunã shaida. Kuma Allah Yã isa Ya zama shaida} [al-Nisa'a: 166], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدًا ٢٨﴾[الفتح: 28]

{Shĩ ne wanda Ya aiki ManzonSa da shiriya da addinin gaskiya dõmin Ya rinjãyar da shi a kan addinai dukansu. Kuma Allah Ya isa Ya zama Mai shaida} [al-Fath: 28] Allah Ya aiko shi da shiriya don ya futar da mutane daga duhun bautar gumaka da kafirci da jahilci zuwa hasken tauhidi da imani, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿يَهْدِى بِهِ ٱللَّهُ مَنِ ٱتَّبَعَ رِضْوَٰنَهُۥ سُبُلَ ٱلسَّلَٰمِ وَيُخْرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذْنِهِۦ وَيَهْدِيهِمْ إِلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ١٦﴾[المائدة: 16]

{Dashĩ, Allah Yanã shiryar da wanda ya bi yardarsa zuwa ga hanyõyin aminci, kuma Yanã fitar da su daga duffai zuwa ga haske da izninsa, kuma Yanã shiryar da su zuwa ga hanya madaidaiciya} [al-Ma'ida: 16], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿الٓرۚ كِتَٰبٌ أَنزَلۡنَٰهُ إِلَيۡكَ لِتُخۡرِجَ ٱلنَّاسَ مِنَ ٱلظُّلُمَٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ بِإِذۡنِ رَبِّهِمۡ إِلَىٰ صِرَٰطِ ٱلۡعَزِيزِ ٱلۡحَمِيدِ ١﴾[إبراهيم: 1]

{A. Ĩ.R. Littãfi ne mun saukar da shi zuwa gare ka dõmin ka fitar da mutãne daga duhunhuna zuwa ga haske, da iznin Ubangijinsu, zuwa ga tafarkin Mabuwãyi, Abin gõdẽwa} [Ibrahim: 1].

**26. Kuma shari'ar Musulunci wacce Manzon Allah Muhammad - SAW - ya zo da ita ita ce cika makin saqonnin Allah da kuma shari'ar Ubangiji; kuma ita ce shari'ar cikawa, kuma a cikinta akwai gyaruwar Addinin mutane da duniyarsu, kuma tana tsarewa a mataki na farko ga Addinin mutane da jininsu da dukiyarsu da hankulansu da zuriyarsu, kuma ta shafe kowa ce shari'a da ta gabace ta na daga shari'u, kamar yadda ta soke bangaren wasun da suka gabaceta.**

Shari'ar Musulunci wacce Manzon Allah ya zo da ita uta ce cika makin saqonnim Allah d a sharo'un Ubangiji, kuma Allah Ya cika wannan saqon Addinin kuma ni'imar ta cika ga mutane aiko Manzon Allah – SAW -, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿...ٱلۡيَوۡمَ أَكۡمَلۡتُ لَكُمۡ دِينَكُمۡ وَأَتۡمَمۡتُ عَلَيۡكُمۡ نِعۡمَتِي وَرَضِيتُ لَكُمُ ٱلۡإِسۡلَٰمَ دِينٗاۚ... ٣﴾[المائدة: 3]

{Kuma yaune muka cika muku Addininku kuma muka cika muku ni'imarku kuma muka yarje muku Musulun a Matsayin Addini} [Al-Maa'ida: 3]. Kuma Shari'ar Musulunci itace cikakkiyar

shari'a kuma a cikinta gyaruwar Addinin mutane da duniyarsu suke cikinta; saboda ita ce ta tare baki dayan shari'un da suka gabata kuma mafi cikar su, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ يَهۡدِي لِلَّتِي هِيَ أَقۡوَمُ وَيُبَشِّرُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱلَّذِينَ يَعۡمَلُونَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ أَنَّ لَهُمۡ أَجۡرٗا كَبِيرٗا ٩﴾[الإسراء: 9]

{Lalle ne wannan Alƙur'ãni yanã shiryarwa ga (hãlayen) waɗanda suke mafi daidaita kuma yanã bãyar da bushãra ga mũminai waɗanda suke aikata ayyuka na ƙwarai (cẽwa) "Lalle ne sunã da wata ijãra. mai girma} [al-Isra'a:9] Kuma Ya sanya shari'ar Musulunci daga mutane wahalhalun da suke a cikin al'umman da suka gabata, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلرَّسُولَ ٱلنَّبِيَّ ٱلۡأُمِّيَّ ٱلَّذِي يَجِدُونَهُۥ مَكۡتُوبًا عِندَهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ يَأۡمُرُهُم بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَىٰهُمۡ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡخَبَٰٓئِثَ وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ عَلَيۡهِمۡۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِهِۦ وَعَزَّرُوهُ وَنَصَرُوهُ وَٱتَّبَعُواْ ٱلنُّورَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ مَعَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ ١٥٧﴾[الأعراف: 157]

{Waɗanda suke sunã bin Manzo, Annabi, Ummiyyi wanda suke sãmun sa rubũce a wurinsu, a cikin Attaura da Linjĩla yana Umartarsu da kyawawan ayyuka kuma yana hanasu daga Mummuna kuma yana halarta musu daxaxan abubuwa kuma yana haramta aaamusu munana kuma yana sauke musu abunda ya dame su da ququmqi waxanda suke kansu saboda haka waxanda sukai Imani da shi kuma suka qarfafe shi kuma suka taimake shi kuma suka bi hasken da ya saukar tare da shi waxan nan sune masu rabauta} [al-a'araf: 157] Kuma Shari'ar musulunci ta goge dukkan Shari'un da suka gabata, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَأَنزَلۡنَآ إِلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ بِٱلۡحَقِّ مُصَدِّقٗا لِّمَا بَيۡنَ يَدَيۡهِ مِنَ ٱلۡكِتَٰبِ وَمُهَيۡمِنًا عَلَيۡهِۖ فَٱحۡكُم بَيۡنَهُم بِمَآ أَنزَلَ ٱللَّهُۖ وَلَا تَتَّبِعۡ أَهۡوَآءَهُمۡ عَمَّا جَآءَكَ مِنَ ٱلۡحَقِّۚ لِكُلّٖ جَعَلۡنَا مِنكُمۡ شِرۡعَةٗ وَمِنۡهَاجٗاۚ وَلَوۡ شَآءَ ٱللَّهُ لَجَعَلَكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَلَٰكِن لِّيَبۡلُوَكُمۡ فِي مَآ ءَاتَىٰكُمۡۖ فَٱسۡتَبِقُواْ ٱلۡخَيۡرَٰتِۚ إِلَى ٱللَّهِ مَرۡجِعُكُمۡ جَمِيعٗا فَيُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٤٨﴾[المائدة: 48]

{Kuma Mun saukar da Littãfi zuwa gare ka da gaskiya yanã mai gaskatãwa ga abin da yake a gaba gare shi daga Littãfi (Attaura da Injĩla), kuma mai halartãwa a kansa sai ka yi hukunci a tsakãninsu da abin da Allah Ya saukar kuma kada ka bĩbiyi son zũciyõyiniu daga abin da ya zo maka daga gaskiya Ga kõwanne daga gare ku Mun sanya sharĩa da hanya (ta bin ta) Kuma dã Allah Yã so, dã Yã sanya ku al'umma guda, kuma amma dõmin Ya jarraba ku a cikin abin da Ya bã ku Sai ku yi tsere ga ayyukan alheri Zuwa ga Allah makõmarku take gabã ɗaya Sa'an nan Ya bã ku lãbãri ga abin da kuka kasance kunã sãɓãwa a cikinsa} [al-Ma'ida: 48] Saboda Al-qurani ya qunshi Shari'ar abun da ya zo yana mai gasgata abunda ya gabace shi na litattafan Allah kuma yana mai hukunci akan su kuma ya shafe su.

**27. Kuma Allah - SWT - baya karbar wani Addini in ba Musulunci ba wanda shi ne wanda Annabi Muhammad - SAW - ya zo da shi, kuma duk wanda ya riqi wanin Musulunci Addini to ba za'a karba ba**

Kuma Allah - SWT - baya karbar wani Addini in ba Musulunci ba wanda shine wanda Annabi Muhammad - SAW - ya zo da shi, kuma duk wanda ya riqi wanin Musulunci Addini to ba za'a karba ba, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ ٨٥﴾ [آل عمران: 85]

{Kuma wanda ya nẽmi wanin Musulunci ya zama addini, to, bã zã a karɓa daga gare shi ba. Kuma shi a Lãhira yana daga cikin mãsu hasãra} [Aal Imran: 85] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلدِّينَ عِندَ ٱللَّهِ ٱلۡإِسۡلَٰمُۗ وَمَا ٱخۡتَلَفَ ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ إِلَّا مِنۢ بَعۡدِ مَا جَآءَهُمُ ٱلۡعِلۡمُ بَغۡيَۢا بَيۡنَهُمۡۗ وَمَن يَكۡفُرۡ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ سَرِيعُ ٱلۡحِسَابِ ١٩﴾[آل عمران: 19]

{Lalle ne, addini a wurin Allah, Shi ne Musulunci. Kuma waɗanda aka bai wa Littafi ba su sãɓã ba, fãce a bãyan ilmi ya je musu, bisa zãlunci a tsakãninsu. Kuma wanda ya kãfirta da ãyõyin Allah, to, lalle ne Allah Mai gaugãwar sakamako ne} [Aal Imran: 19], Kuma wannan Musuluncin shi ne tafarkin Anabi Ibrahim - amincin Allah a gare shi-, Allah - Madaukakin Sarki -Ya ce:

﴿وَمَن يَرۡغَبُ عَن مِّلَّةِ إِبۡرَٰهِـۧمَ إِلَّا مَن سَفِهَ نَفۡسَهُۥۚ وَلَقَدِ ٱصۡطَفَيۡنَٰهُ فِي ٱلدُّنۡيَاۖ وَإِنَّهُۥ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ لَمِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ ١٣٠﴾[البقرة: 130]

{Kuma wãne ne yake gudu daga aƙĩdar Ibrãhĩm, fãce wanda ya jãhilta ga ransa? Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun zãɓe shi, a cikin dũniya, kuma lalle ne shi, a cikin Lãhira, haƙĩƙa, yana daga sãlihai} [Al-Baqara: 130], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَنۡ أَحۡسَنُ دِينٗا مِّمَّنۡ أَسۡلَمَ وَجۡهَهُۥ لِلَّهِ وَهُوَ مُحۡسِنٞ وَٱتَّبَعَ مِلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۗ وَٱتَّخَذَ ٱللَّهُ إِبۡرَٰهِيمَ خَلِيلٗا ١٢٥﴾[النساء: 125]

{Kuma wãne ne ya fi kyau ga addini daga wanda ya sallama fuskarsa ga Allah, alhãli kuwa yanã mai kyautatawa kuma ya bi aƙidar Ibrãhĩm, Yanã mai karkata zuwa ga gaskiya? Allah Yã riƙi Ibrãhĩm badãɗayi} [al-Nisa'a: 125] Kuma Allah - Madaukakin sarki - Yana umarci ManzonSa Muhammad - SAW - kan ya cewa:

﴿قُلۡ إِنَّنِي هَدَىٰنِي رَبِّيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ دِينٗا قِيَمٗا مِّلَّةَ إِبۡرَٰهِيمَ حَنِيفٗاۚ وَمَا كَانَ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١٦١﴾[الأنعام: 161]

{ Kace: Lalle nĩ, Ubangijina Yã shiryar da ni zuwa ga tafarki madaidaici, addĩni, ƙĩmantãwa (ga abũbuwa), mai aƙĩdar Ibrãhĩm, mai karkata zuwa ga gaskiya, kuma bai kasance daga mãsu shirki ba} [al-An'am: 161].

**28. Al-qu'ani mai girma shi ne littafin da Allah Yayi wahayinSa ga Manzo Muhammad - SAW - kuma shi ne zancen Ubangijin talikaia aikowa Manzon Allah - SAW - kuma shi ne zancen Ubangijin talikai wanda Allah Ya qure mutum da aljann kan su zo da kwatankwacin sa, ko sura kwatankawcinsa, kuma har yau qurewa bata qare ba, kuma Al-qurani yana bada amsa muhimmai masu yawa da miliyoyin mutane suka gaza, kuma Al-qurani mai girma abun kiyayewa ne har zuwa yau din nan da yaren larabci da ya sauka da shi, kuma ba'a rage ko harafi daya ba, kuma yana nan a buge ana yada shi, kuma littafi ne mai girma mai gajiyarwa wanda ya dace da a karanta shi ko a karanta fassararsa, kamar yadda Sunnar manzon Allah - SAW - da koyarwarsa da tarihinsa ababan kiyayewa ne kuma ababan rawaito ne daidai da tsanin jerin masu riwaya da aka yarda da su, kuma an buga su da larabci wanda Manzon Allah - SAW - yayi magana da shi, kuma an fassara su da yaruka da yawa, kuma Al-qur'ani da Sunnar Manzon Allah su ne tushe qwara daya na hukunce-hukuncen Musulunci da shari'unsa, saboda Musulunci, saboda ba'a daukar Musulunci daga aiyukan daidaikun mutane da suke danganta kansu da Musulunci; kawai ana dauka ne daga wahayin Allah a Al-qur'ani mai girma da Sunnar Annabi**

Al-qur'ani maigirma shi ne littafin da Allah Yayi wahayinsa zuwa ga Manzo Balarabe Muhammad – SAW - da yaren Larabci

kuma shi ne zancen Ubangijin talikai, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَإِنَّهُۥ لَتَنزِيلُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٩٢ نَزَلَ بِهِ ٱلرُّوحُ ٱلۡأَمِينُ ١٩٣ عَلَىٰ قَلۡبِكَ لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ١٩٤ بِلِسَانٍ عَرَبِيّٖ مُّبِينٖ ١٩٥﴾[الشعراء: 192-195]

{Kuma lalle shi (Alƙur'ãni), haƙĩƙa, saukarwar Ubangijinhalittu ne.(192) Rũhi amintacce ne ya sauka da shi.(193) A zũciyarka, dõmin ka kasance daga mãsu gargaɗi.(194) Da harshe na Larabci mai bayãni.(195)} [al-Shu'araa: 192-195], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَإِنَّكَ لَتُلَقَّى ٱلۡقُرۡءَانَ مِن لَّدُنۡ حَكِيمٍ عَلِيمٍ ٦﴾[النمل: 6]

{Kuma lalle ne haƙĩka, anã haɗa ka da Alƙur'ãni daga gun Mai hikima, Masani} [al-Naml: 6] Kuma wannan Al-qur'ani saukakke ne daga Allah kuma mai gasgatawa ne da abunda ya gabace shi na litattafan Allah, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَمَا كَانَ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانُ أَن يُفۡتَرَىٰ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَٰكِن تَصۡدِيقَ ٱلَّذِي بَيۡنَ يَدَيۡهِ وَتَفۡصِيلَ ٱلۡكِتَٰبِ لَا رَيۡبَ فِيهِ مِن رَّبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٣٧﴾[يونس: 37]

{Kuma wannan Alƙur'ãni bai kasance ga a ƙirƙira shi ba daga wanin Allah, kuma amma shi gaskatawar wannan ne da yake a gabãninsa da bayãnin hukuncin littãffan Allah, Bãbu shakka a cikinsa, daga Ubangijin halittu yake} [Yunus: 37] Kuma Al-qur'ani mai girma ya fayyace mafi yawan mas'alolin da Yahudu da Nasara sukai Sabani akansu a cikin Addinansu, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ يَقُصُّ عَلَىٰ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ أَكۡثَرَ ٱلَّذِي هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَ ٧٦﴾[النمل: 76]

{Lalle ne wannan Alƙur'ãni yanã gaya wa Banĩ Isrãĩla mafi yawan abin da sũ suke sãɓa wa jũnansu a ciki} [al-Naml: 76]

Kuma Al-qurani mai girma ya qunshi dalilai da hujjoji da zasu iya tsayawa hujja a kan mutane baki daya wajen sanin haqiqanu da suke da alaqa da Allah – SWT- da AddinSa da sakamakonSa, Allah - Madaukakin sarki - Ya ce:

﴿وَلَقَدۡ ضَرَبۡنَا لِلنَّاسِ فِي هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانِ مِن كُلِّ مَثَلٖ لَّعَلَّهُمۡ يَتَذَكَّرُونَ٢٧﴾[الزمر: 27]

{Kuma lalle ne haƙĩƙa Mun buga wa mutãne a, cikin wannan Alƙur'ãni, daga kõwane misãli, ɗammãninsu su yi tunãni} [al-Zumar: 27], kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿... وَنَزَّلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡكِتَٰبَ تِبۡيَٰنٗا لِّكُلِّ شَيۡءٖ وَهُدٗى وَرَحۡمَةٗ وَبُشۡرَىٰ لِلۡمُسۡلِمِينَ٨٩﴾[النحل: 89]

{Kuma mun saukar maka da Littafin mai bayani ga komai kuma shiriya ne da rahama ga Musulmai} [al-Nahl 89], Kuma Al-qurani mai girma yana amsa tambayoyi masu yawa da suka kidimar da miliyoyin mutane saboda Al-qur'ani mai girma yana bayani yadda Allah Ya halicci sammai da da kasa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿أَوَلَمۡ يَرَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ أَنَّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ كَانَتَا رَتۡقٗا فَفَتَقۡنَٰهُمَاۖ وَجَعَلۡنَا مِنَ ٱلۡمَآءِ كُلَّ شَيۡءٍ حَيٍّۚ أَفَلَا يُؤۡمِنُونَ٣٠﴾[الأنبياء: 30]

{Shin kuma waɗanda suka kãfirta ba, su gani da cẽwa lalle sammai da ƙasa sun kasance ɗinke, sai Muka bũɗe su, kuma Muka sanya dukan kome mai rai daga ruwa? Shin, bã zã su yi ĩmãni ba?} [al-Anbiyaa: 30] Da kuma yadda Allah Ya halicci mutum, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِن كُنتُمۡ فِي رَيۡبٖ مِّنَ ٱلۡبَعۡثِ فَإِنَّا خَلَقۡنَٰكُم مِّن تُرَابٖ ثُمَّ مِن نُّطۡفَةٖ ثُمَّ مِنۡ عَلَقَةٖ ثُمَّ مِن مُّضۡغَةٖ مُّخَلَّقَةٖ وَغَيۡرِ مُخَلَّقَةٖ لِّنُبَيِّنَ لَكُمۡۚ وَنُقِرُّ فِي ٱلۡأَرۡحَامِ مَا نَشَآءُ إِلَىٰٓ

أَجَلٖ مُّسَمّٗى ثُمَّ نُخۡرِجُكُمۡ طِفۡلٗا ثُمَّ لِتَبۡلُغُوٓاْ أَشُدَّكُمۡۖ وَمِنكُم مَّن يُتَوَفَّىٰ وَمِنكُم مَّن يُرَدُّ إِلَىٰٓ أَرۡذَلِ ٱلۡعُمُرِ لِكَيۡلَا يَعۡلَمَ مِنۢ بَعۡدِ عِلۡمٖ شَيۡـٔٗاۚ وَتَرَى ٱلۡأَرۡضَ هَامِدَةٗ فَإِذَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡهَا ٱلۡمَآءَ ٱهۡتَزَّتۡ وَرَبَتۡ وَأَنۢبَتَتۡ مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ٥﴾ [الحج: 5]

{Ya ku mutãne! Idan kun kasance a cikin shakka a Tãshin ¡iyãma, to, lalle ne Mũ, Man halittaku daga turɓaya, sa'an nan kuma daga gudãjin jini, sa'an nan kuma daga taõka wadda ake halittãwa da wadda ba a halittawa dõmin, Mu bayyana muku. Kuma Munã tab batar da abin da Muke so a cikin mahaifa zuwa ga wani ajali ambatacce, sa'an nan kuma Munã fitar da ku kunã jãrĩri, sa'an nan kuma dõmin ku kai ga cikar ƙarfinku. Kuma daga cikin ku akwai wanda ke mutuwa, kuma daga gare ku akwai wanda ake mayarwa zuwa ga mafi ƙasƙancin rãyuwa dõmin kada ya san kõme a bãyan ya sani. Kuma kanã ganin ƙasa shiru, sa'an nan idan Muka saukar da ruwa a kanta, sai ta girgiza kuma ta kumbura, kuma ta tsirar da tsirrai daga kõwane nau'i mai ban sha'awa} [Al-hajji: 5] kuma ina ne makomarsa kuma maye sakamakon wanda ya kyautata da wanda ya munana a wannan rayuwar kuma bayanin dalilan akan wannan mas'alar ya gabata a sakin layi na (20) kuma shin wadan nan halittun sun samu ne haka kawai ko an samar da su saboda wata manufa babba? Allah Madaukakin Sarki Ya ce:

﴿أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ١٨٥﴾[الأعراف: 185]

{Shin, ba su yi dũbi ba a cikin mulkin sammai da ƙasa, da kuma abin da Allah Ya halitta daga kõme, kuma akwai tsammãni kasancewar ajalinsu, haƙĩƙa, ya kusanta? To, da

wane lãbãri a bãyansa suke yin ĩmãni?} [al-A'araf: 185], kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿أَفَحَسِبْتُمْ أَنَّمَا خَلَقْنَٰكُمْ عَبَثًا وَأَنَّكُمْ إِلَيْنَا لَا تُرْجَعُونَ ١١٥﴾[المؤمنون: 115]

{Shin, to, kun yi zaton cẽwa Mun halitta ku ne da wãsa kuma lalle ku, zuwa gare Mu, bã zã ku kõmo ba?} [al-Mua'Munun: 115] Kuma Al-qur;ani mai girma kiyayye ne har zuwa yau da yaren larabci wanda ya sauka da shi, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّا نَحْنُ نَزَّلْنَا ٱلذِّكْرَ وَإِنَّا لَهُۥ لَحَٰفِظُونَ ٩﴾[الحجر: 9]

{Lalle Mũ ne, Muka saukar da Ambato (Alƙur'ãni), kuma lale Mũ, haƙĩƙa, Mãsu kiyayẽwane gare shi} [al-Hijr: 9] Ba'a tauye wani harafi daga cikinsa ba, kuma ya tsarkaka daga kwangaba kwan baya ya faru a cikinsa ko kuma tawaya ko canji, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلْقُرْءَانَ ۚ وَلَوْ كَانَ مِنْ عِندِ غَيْرِ ٱللَّهِ لَوَجَدُوا۟ فِيهِ ٱخْتِلَٰفًا كَثِيرًا ٨٢﴾

{Shin, bã su kula da Alƙur'ãni, kuma dã yã kasance daga wurin wanin Allah haƙĩƙa, dã sun sãmu, a cikinsa, sãɓã wa jũnamai yawa?} [al-Nisa'a: 82] Kuma shi yana nan a buge kuma a ko ina kuma shi littafi ne mai girma mai Mu'ujiza, wanda kuma ya dace da a karanta shi ko a sauarare shi ko kuma a fassara ma'anoninsa kamar yadda cewa sunnar Manzon Allah – SAW - take da koyarwarsa da tarihinsa a kiyaye suke kuma an rawaito su daidai da jerin masu riwaya wadanda aka amince da su kuma yana nan a buge da yaren larabci wanda Manzon Allah - SAW - yayi magana da shi kuma an fassara shi a yaruka da yawa, kuma Al-qur'ani da Sunnar mazon Allah – SAW - sune tushe kwara daya na hukunce-hukuncen Musulunci da shari'arsa saboda Musulunci ba'a koyarsa ta hanyar ayyukan wasu daidaiku

waxanda suke danganta kansu da Musuluncin; Kuma kadai ana samun sa ne ta hanyar wahayi daga Allah wanda Yake kiyayye, su ne Al-qur'ani mai girma da Sunnar Annabi, Allah - Madaukakin Ya ce a game da sha'anin Al-qur'ani:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِٱلذِّكۡرِ لَمَّا جَآءَهُمۡۖ وَإِنَّهُۥ لَكِتَٰبٌ عَزِيزٞ ٤١ لَّا يَأۡتِيهِ ٱلۡبَٰطِلُ مِنۢ بَيۡنِ يَدَيۡهِ وَلَا مِنۡ خَلۡفِهِۦۖ تَنزِيلٞ مِّنۡ حَكِيمٍ حَمِيدٖ ٤٢﴾[فصلت: 41-42]

{Kuma lallai wadanda suka kafirta da ambato yayin da ya zo musu kuma cewa shi littafi ne cewa shi littafi ne Mabuwayi, kuma barna bata shiga cikinsa ta gaba ne ko ta baya ne kuma saukakke ne daga Mai Hikima kuma abun godewa} [Fussilat: 41-42] Kuma Allah - Madaukaki - Ya ce game da sha'anin Sunnanr Manzon Allah kuma cewa ita ma wahayi ce daga Allah:

﴿...وَمَآ ءَاتَىٰكُمُ ٱلرَّسُولُ فَخُذُوهُ وَمَا نَهَىٰكُمۡ عَنۡهُ فَٱنتَهُواْۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٧﴾[الحشر: 7]

{Kuma abunda Manzo ya zo muku da sho to ku karbe shi kuma abunda ya haneku to ku hanu kuji tsoron Allah lallai Allah Mai tsananin Uquba ne} [al'Hashr 7].

**29. Kuma Musulunci yana umarni da kyautatawa iyaye, koda kuwa sun kasance ba musulmai ba ne, kuma ya na wasiyya da 'ya'ya.**

Musulunci yana umarni da a kyautatawa iyaye, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿۞ وَقَضَىٰ رَبُّكَ أَلَّا تَعۡبُدُوٓاْ إِلَّآ إِيَّاهُ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنًاۚ إِمَّا يَبۡلُغَنَّ عِندَكَ ٱلۡكِبَرَ أَحَدُهُمَآ أَوۡ كِلَاهُمَا فَلَا تَقُل لَّهُمَآ أُفّٖ وَلَا تَنۡهَرۡهُمَا وَقُل لَّهُمَا قَوۡلٗا كَرِيمٗا ٢٣﴾[الإسراء: 23]

{Kuma Ubangijinka Ya hukunta kada ku bauta wa kõwa fãce Shi, kum game da mahaifa biyu ku kyautata kyautatawa, ko dai

ɗayansu ya kai ga tsũfa a wurinka ko dukansu biyu, to, kada ka ce musu 'tir' kuma kada ka tsãwace su kuma ka faɗa musu magana mai karimci} [al-Isra'a: 23], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيۡهِ حَمَلَتۡهُ أُمُّهُۥ وَهۡنًا عَلَىٰ وَهۡنٖ وَفِصَٰلُهُۥ فِي عَامَيۡنِ أَنِ ٱشۡكُرۡ لِي وَلِوَٰلِدَيۡكَ إِلَيَّ ٱلۡمَصِيرُ ١٤﴾[لقمان: 14]

{Kuma Mun yi wasiyya ga mutum game da mahaifansa biyu; uwarsa tã ɗauke shi a cikin rauni a kan wani rauni, kuma yãyensa a cikin shekaru biyu (Muka ce masa) "Ka gõde Mini da kuma mahaifanka biyu. Makõma zuwa gare Ni kawai take} [Luqman:14] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيۡهِ إِحۡسَٰنًاۖ حَمَلَتۡهُ أُمُّهُۥ كُرۡهٗا وَوَضَعَتۡهُ كُرۡهٗاۖ وَحَمۡلُهُۥ وَفِصَٰلُهُۥ ثَلَٰثُونَ شَهۡرًاۚ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَبَلَغَ أَرۡبَعِينَ سَنَةٗ قَالَ رَبِّ أَوۡزِعۡنِيٓ أَنۡ أَشۡكُرَ نِعۡمَتَكَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتَ عَلَيَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَيَّ وَأَنۡ أَعۡمَلَ صَٰلِحٗا تَرۡضَىٰهُ وَأَصۡلِحۡ لِي فِي ذُرِّيَّتِيٓۖ إِنِّي تُبۡتُ إِلَيۡكَ وَإِنِّي مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ١٥﴾[الأحقاف: 15]

{Kuma Mun yi wasiyya ga mutum game da mahaifansa biyu da kyautatãwa, uwarsa tã yi cikinsa wahala, kuma ta haife shi wahala. cikinsa da yãyensa watã talãtin. Har a lõkacin da ya kai ga mafi ƙarfinsa, kuma ya kai shẽkara arba'in, ya ce: "Ya Ubangijĩna! Ka kange nidõmin in gõde wa ni'imarKa, wadda Ka ni'imta a kaina da kuma a kan mahaifãna biyu, kuma dõmin in aikata aikin ƙwarai wanda Kake yarda da shi, kuma Ka kyautata mini a cikin zuriyata. Lalle nĩ, nã tũba zuwa gare Ka, kuma lalle ni, inã daga mãsu sallamãwa (ga umurninKa)} [al-Ahqaf: 15] Kuma an rawaito daga Abu Huraira -Allah Ya yarda da shi- ya ce: Wani Mutum ya zo wajen Manzon Allah - SAW - sai ya ce:

Ya Manzon Allah waye mafi cancantar mutane da kyakkyawar kusantata? sai yace: "Mahaifiyarka" sai ya ce: sannan kuma wa? sai ya ce: "Mahaifiyarka" sai ya ce: sannan kuma wa? sai ya ce: "Mahaifiyarka" sai ya ce: sannan kuma wa? sai ya ce: "Mahaifinka" Sahih Muslim Kuma wannan umarni da wasiyya ga iyaye dai dai ne musulmai ne ko ba musulmai ba ne. An rawaito daga Asmaa Bint Abubakar ta ce: "Mahaifiya ta ta zo kuma ita mushirika ce a lokacin kuraishawa sunyiwa Annabi - SAW - alqawari tare da danta sai na tambayi Manzon Allah - SAW - sai na ce: Lallai mahaifiyata ta zo tana son ganina, ko na iya zuwan mata? sai ya ce: "Eh, kina iya zuwa ga mahaifiyarki" Sahih Al-Bukhari. Kai ba haka ba da za'a ce mahaifa zasu yi qoqari cikin su juyar da yaro daga Musulunci zuwa kafurci saboda Musulci ya na yana Umarninsa -Kuma hali a wannan lokacin- cewa shi ba zai bi su ba, kuma ya zauna a matsayin mai imani da Allah kuma ya kayutata musu, kuma ya zauna da su lafiya, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَإِن جَٰهَدَاكَ عَلَىٰٓ أَن تُشۡرِكَ بِي مَا لَيۡسَ لَكَ بِهِۦ عِلۡمٞ فَلَا تُطِعۡهُمَاۖ وَصَاحِبۡهُمَا فِي ٱلدُّنۡيَا مَعۡرُوفٗاۖ وَٱتَّبِعۡ سَبِيلَ مَنۡ أَنَابَ إِلَيَّۚ ثُمَّ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأُنَبِّئُكُم بِمَا كُنتُمۡ تَعۡمَلُونَ ١٥﴾ [لقمان: 15]

{Kuma idan mahaifanka suka tsananta maka ga ka yi shirki game da Ni, ga abin da bã ka da ilmi gare shi, to, kada ka yi musu ɗã'a. Kuma ka abũce su a cikin dũniya gwargwadon sharĩ'a, kuma ka bi hanyar wanda ya mayar da al'amari zuwa gare Ni, sa'an nan zuwa gare Ni makõmarku take sa'an nan In bã ku lãbãri game da abin da kuka kasance kunã aikatãwa} [Luqman: 15] Kuma Musulunci baya hana musulmi ya

kyautatawa makusantansa mushirikai ko wasun makusantansa indai basu zamanto abokan fada ba a gare shi, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿لَّا يَنْهَىٰكُمُ ٱللَّهُ عَنِ ٱلَّذِينَ لَمْ يُقَٰتِلُوكُمْ فِى ٱلدِّينِ وَلَمْ يُخْرِجُوكُم مِّن دِيَٰرِكُمْ أَن تَبَرُّوهُمْ وَتُقْسِطُوٓا۟ إِلَيْهِمْ ۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلْمُقْسِطِينَ ﴿٨﴾﴾[الممتحنة: 8]

{Allah bã Ya hana ku, daga waɗanda ba su yãƙe ku ba sabõda addini kuma ba su fitar da ku ba daga gidãjenku, ga ku kyautata musu kuma ku yi musu ãdalci. Lalle Allah Yanã son mãsu ãdalci}. [al-Mumtahina: 8]. Kuma Musulunci yana umarni da wasiyya ga 'ya'yansa, mafi girman abunda Musulunci yayi umarni ga mahaifin ya koyar da yaransa haqqokin Ubangijinsu kamar yada Manzon Allah - SAW - ya ce ga dan Baffansa Abdullahi Bn Abbas - Allah Ya yarda da su - "Ya kai Yaro ko kai dan karamin yaro bana sanar da kai wasu kalmomi da zasu amfafeka da su? sai na ce: Eh ya Manzon Allah, sai ya ce: "Ka kiyaye Allah sai Ya kiyaye ka, ka kiyaye Allah sai ka same Shi a gabanka, ka tuna da Allah a lokacin yalwa sai Ya tuna da kai a lokacin tsanani kuma idan zakayi roqo to ka roqi Allah, kuma idan zaka nemi taimako to ka nemi taimakon Allah" Ahmad ne ya rawaito shi 4/287. Kuma Allah Yayi umarni ga iyaye su koyawa 'ya'yansu abunda zai anfanar da su a al’amuran Addininsu da duniyarsu, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ قُوٓا۟ أَنفُسَكُمْ وَأَهْلِيكُمْ نَارًا وَقُودُهَا ٱلنَّاسُ وَٱلْحِجَارَةُ عَلَيْهَا مَلَٰٓئِكَةٌ غِلَاظٌ شِدَادٌ لَّا يَعْصُونَ ٱللَّهَ مَآ أَمَرَهُمْ وَيَفْعَلُونَ مَا يُؤْمَرُونَ ﴿٦﴾﴾[التحريم: 6]

{Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku kãre wa kanku (da iyãlinku wata wuta makãmashinta mutãne da duwãtsu ne. A kanta akwai waɗansu malã'iku mãsu kauri, mãsu ƙarfi. Bã su sãbã wa

Allah ga abin da Ya umurce su, kuma sunã aikata abin da ake umunin su} [al-Tahrim: 6] Kuma daga Ali -Allah Ya yarda da shi- game da fadin Allah – Madaukaki -: "Ku tsare kanku da iyalanku daga wuta" ya ce: "Ku ladabtar da su kuma ku sanar da su" Kuma Annabi - SAW - yayi umarni ga iyaye su koyawa yaran su Sallah; don su tashi akan ta sai Manzon Allah - SAW - ya ce: "Ku umarci 'ya'yanku da Sallah suna 'yan Shekara bakwai" Abu Daud ya Rawaito shi kuma Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Dukkanku masu Kiwo ne kuma dukkanku sai an tambayeku abunda kuke kiwo, shugaba mai gadi akan talakawansa, mutum mai kiwo ne akan iyalansa kuma shi abun tambaya ne akan abunda aka bashi kiwon, kuma mace ma mai kiwo ce a cikin gidan mijinta kuma abar tambaya ce akan abunda aka bata kiwon, kuma dan aiki mai gadi akan dukiyar mai gidansa kuma za'a tambaye shi kan abunda aka bashi kuma baki dayanku masu gadi ne kuma baki dayanku masu kiwo ne kuma za'a tambaye ku kan abunda aka baku kiwonsa" Sahihin Ibn Hibban: 4490. Kuma Musulunci ya umarci mahaifi da ciyar da 'ya'yansa da kuma mutanen gidansa, kuma bayanin wani abu daga cikin wancan a sakin layi mai lamba (18) kuma Annabi - SAW - yayi bayani falalar ciyarwa akan 'ya'ya sai ya ce: "Mafificin dinare da mutum zai ciyar shi wanda ya ciyar da iyalansa da kuma dinaren da mutum ya ciyar da dabbarsa a tafarkin Allah da kuma dinaren da ya ciyar ga abokansa a tafarkin Allah" Abu Qilaba ya ce: "sai ya fara da iyali, sannan Abu Qilaba ya ce: Kuma wane mutum ne ya fi girman lada kamar mutumin da ya ciyar da iyali qanana don ya rufa musu asiri, kuma Allah Ya anfanar da su da shi kuma ya wadata su" Sahih Muslim: 994.

## 30. Musulunci yana umarni da adalci a cikin magana da kuma aiki koda kuwa tare da abokan gaba ne

Allah - SWT - Ya sifantu da adalci a cikin ayyukanSa da gudanarwarSa a tsakanin bayinSa, kuma Shi ne akan tafarki madaidaici a cikin abunda Yayi umarni da shi da kuma abunda Ya hana a abunda yake cikin halittarSa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلۡعِلۡمِ قَآئِمَۢا بِٱلۡقِسۡطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾ [آل عمران: 18]

{Allah Ya shaida cẽwa: Lalle ne bãbu abin bautãwa fãce Shi kuma malãiku da ma'abũta ilmi sun shaida, yana tsaye da ãdalci, bãbu abin bautãwa face Shi, Mabuwãyi, Mai hikima} [Aal Imran: 18], Kuma Allah Yana umarni da adalci, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قُلۡ أَمَرَ رَبِّي بِٱلۡقِسۡطِۖ...﴾ [الأعراف: 29]

{Ka ce Ubangiji na ya yi umarni da Adalci} [al-A'araf: 29] Kuma baki dayan Manzanni da Annabawa - amincin Allah a gare su - sun zo da adalci, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿لَقَدۡ أَرۡسَلۡنَا رُسُلَنَا بِٱلۡبَيِّنَٰتِ وَأَنزَلۡنَا مَعَهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡمِيزَانَ لِيَقُومَ ٱلنَّاسُ بِٱلۡقِسۡطِۖ...﴾ [الحديد: 25]

{Haƙĩƙa, lalle Mun aiko ManzanninMu da hujjõji bayyanannu, kuma Muka saukar da Littãfi da sikeli tãre da su dõmin mutãne su tsayu da ãdalci} [al-Hadid: 25] Kuma ma'auni shi ne adalci a cikin maganganu da ayyuka, kuma Musulunci yana umarni da adalci a cikin magana da aiki har a wajen abokan gaba, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ بِٱلْقِسْطِ شُهَدَآءَ لِلَّهِ وَلَوْ عَلَىٰٓ أَنفُسِكُمْ أَوِ ٱلْوَٰلِدَيْنِ وَٱلْأَقْرَبِينَۚ إِن يَكُنْ غَنِيًّا أَوْ فَقِيرًا فَٱللَّهُ أَوْلَىٰ بِهِمَاۖ فَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلْهَوَىٰٓ أَن تَعْدِلُواْۚ وَإِن تَلْوُۥٓاْ أَوْ تُعْرِضُواْ فَإِنَّ ٱللَّهَ كَانَ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًا ١٣٥﴾[النساء: 135]

{Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku kasance mãsu tsayuwa da ãdalci, mãsu shaida sabõda Allah, kuma kõ dã a kanku ne kõ kuwa, mahaifa da mafi kusantar zumunta, ko (wanda ake yi wa shaida kõ a kansa) ya kasance mawadãci kõ matalauci, to, Allah ne Mafi cancanta da al'amarinsu. Sabõda haka, kada ku bĩbiyi son zũciya, har ku karkata. Kuma idan kuka karkatar da magana, kõ kuwa kuka kau da kai, to lalle ne Allah Yã kasance Masani ga abubuwan da kuke aikatãwa} [al-Nisa: 135] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿... وَلَا يَجْرِمَنَّكُمْ شَنَـَٔانُ قَوْمٍ أَن صَدُّوكُمْ عَنِ ٱلْمَسْجِدِ ٱلْحَرَامِ أَن تَعْتَدُواْۘ وَتَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلْبِرِّ وَٱلتَّقْوَىٰۖ وَلَا تَعَاوَنُواْ عَلَى ٱلْإِثْمِ وَٱلْعُدْوَٰنِۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۖ إِنَّ ٱللَّهَ شَدِيدُ ٱلْعِقَابِ ٢﴾[المائدة: 2]

{Kuma kada kyamar wasu mutane don sun hanaku zuwa dakin Allah Ya sanya ku cewa kuyi ta'addanci, kuyi taimakekeniya kan biyayya da tsoron Allah kuma kada kuyi taimakekeniya kan sabo da ta'addanci, kuji tsoron Allah, lallai Allah Mai tsananin uquba ne} [al-Ma'[da: 2] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ كُونُواْ قَوَّٰمِينَ لِلَّهِ شُهَدَآءَ بِٱلْقِسْطِۖ وَلَا يَجْرِمَنَّكُمْ شَنَـَٔانُ قَوْمٍ عَلَىٰٓ أَلَّا تَعْدِلُواْۚ ٱعْدِلُواْ هُوَ أَقْرَبُ لِلتَّقْوَىٰۖ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ خَبِيرُۢ بِمَا تَعْمَلُونَ ٨﴾[المائدة: 8]

{Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku kasance mãsu tsayin daka dõmin Allah mãsu shaida da ãdalci. Kuma kada ƙiyayya da wasu mutane ta ɗauke ku a kan bã zã ku yi ãdalci ba. Ku yi ãdalci Shĩ ne mafi kusa ga taƙawa. Kuma ku bi Allah da taƙawa. Lalle Allah Masani ne ga abin da kuke aikatãwa} [al-Ma'da:8] Shin ka taba samu a cikin dokokin wasu al'ummai a yau ko a cikin Addinan mutane kwatankwacin wannan al'amari ? na shaidar gaskiya da fadin gaskiya har da kuwa ko akan ka ne ko iyayenka ko makusantanka da kuma umarni da adalci har ga abokan gaba da aboki, Annabi -tsira da amincin Allah- ya yi umarni da adalci a tsakanin 'ya'ya. An rawaito daga Amir ya ce: Naji Al-nu'aman Bn Bashir -Allah Ya yarda da su- kuma shi yana kan munbari yana cewa: baba na ya bani kyauta, sai Amrah Bint Rawahah ta ce: Ni ba zan yarda ba har sai Manzon Allah ya shaida, sai taje wajen Manzon Allah - SAW - sai ya ce: Ni na bawa dana da Amrah Bint Rawaha ta haifa kyauta sai ta umarce ne cewa in shaidar da kai ya Manzon Allah sai ya ce: "Ka bawa sauran 'ya'yanka irinta?" ya ce: A'a sai ya ce: "To kuji tsoron Allah kuma ku daidaita tsakanin 'ya'yanku" sai ya ce: sai na dawo sai ya mayar da kyautarsa" Sahih Al-Bukhari: 2587.

Wancan cewa shi al'amarin mutane ba zai daidaita ba haka ma na kasashe, kuma mutane ba zasu aminta ba akan Addinansu da jinanensu da zuriyarsu da mutuncin su da dukiyoyin su da kasashen su sai da adalci kuma saboda wannan ne muke samun cewa Annabi - SAW - yayin da kafiran Makkah suka matsantawa musulmai a Makkah sai ya umarce su - SAW - cewa da su yi hijira zuwa Habasha; kuma ya dogara kan haka da cewa a can akwai wani sarki mai adalci ba'a zaluntar kowa a garinsa.

**31, Kuma Musulunci yana umarnini da a kyautatawa halitta baki daya, kuma yana kira zuwa kyawawan halaye, da kuma kyawawan ayyuka**

Musulunci yana umarni da a kyautatawa iyaye, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُ بِٱلۡعَدۡلِ وَٱلۡإِحۡسَٰنِ وَإِيتَآيِٕ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ...﴾[النحل: 90]

{Lallai Allah yana Umarni da Adalci da kyautatawa da kuma bawa Ma'aboda kusanci} [al-Nahl: 90] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ فِي ٱلسَّرَّآءِ وَٱلضَّرَّآءِ وَٱلۡكَٰظِمِينَ ٱلۡغَيۡظَ وَٱلۡعَافِينَ عَنِ ٱلنَّاسِۗ وَٱللَّهُ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ﴾[آل عمران: 134]

{Waɗanda suke ciyarwa a cikin sauƙi da tsanani kuma suke mãsu haɗiyẽwar fushi, kuma mãsu yãfe wa mutãne laifi. Kuma Allah Yana son mãsu kyautatãwa} [Aal Imran: 134] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: Lallai cewa Allah ya rubuta kyautaye akan kowane abu, to idan zakuyi kisa to ku kyautata kisan kuma idan zakuyi yanka to ku kyautata yankan kuma dayaku ya wasa wukar tasa, kuma don ya hutar da abin yankansa" Sahih Muslim: 1955. Kuma Musulunci yana kira zuwa ga kyawawan halaye, Allah - Madaukaki Sarki - Ya ce a cikin siffar Manzon Allah Muhammad – SAW - a cikin litattafan da suka gabata:

﴿ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلرَّسُولَ ٱلنَّبِيَّ ٱلۡأُمِّيَّ ٱلَّذِي يَجِدُونَهُۥ مَكۡتُوبًا عِندَهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ يَأۡمُرُهُم بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَىٰهُمۡ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡخَبَٰٓئِثَ وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ عَلَيۡهِمۡۚ فَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِهِۦ وَعَزَّرُوهُ وَنَصَرُوهُ وَٱتَّبَعُواْ ٱلنُّورَ ٱلَّذِيٓ أُنزِلَ مَعَهُۥٓ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُفۡلِحُونَ﴾[الأعراف: 157]

{Waɗanda suke sunã bin Manzo, Annabi, Ummiyyi wanda suke sãmun sa rubũce a wurinsu, a cikin Attaura da Linjĩla yana

Umartarsu da kyawawan ayyuka kuma yana hanasu daga Mummuna kuma yana halarta musu daxaxan abubuwa kuma yana haramta aaamusu munana kuma yana sauke musu abunda ya dame su da ququmqi wadanda suke kansu saboda haka wadanda sukai imani da shi kuma suka qarfafe shi kuma suka taimake shi kuma suka bi hasken da ya saukar tare da shi wadan nan sune masu rabauta} [al-A'araf: 157]: Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Ya ke Aisha lallai Allah Mai tausasawa ne kuma yana bayarwa kan tausasawa abunda bai bayar ba akan tsanantawa, kuma da abunda bai bayar ba ga waninsa" Sahih Muslim: 2593. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Lallai Allah Ya haramta muku sabata iyaye mata da binne 'ya'ya matakuma ya hana take haqqi kuma ya hanaku qila wa qala da yawan tambaya da kuma tozarta dukiya" Sahih Al-Bukhari 2408. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Ba zaku shiga Al-janna ba har sai kunyi Imani kuma ba zaku yi imani ba har sai kunso juna kuma ba na nuna muku wani abu ba wanda in kuka aikatashi zaku so junanku? ku yada sallama a tsakaninku" Sahih Muslim: 54.

**32. Kuma Musulunci yana umarni da kyawawan halaye kamar gaskiya da sauke amana da kuma kamewa da kunya da gwarzanta da karamci da taimakawa mabuqaci da kai gudun mawa ga wanda yake cikin wani hali, da ciyar da mai jin yinwa, da kyautata makwabtaka, da sadar da zumunci, da tausasawa dabbobi**

Musulunci yana umarni da kyawawan dabi'u Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: "Ni an aiko ni ne kawai don in cika kyawawan halaye" Sahihu Al-adab Al-mufrad: 207 Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: Lallai mafi soyuwar ku a wajena, kuma mafi kusancinku a wajen zama a ranar al-qiyama shi mafi kyawunku

halaye, kuma lallai cewa mafi haushinku a wajena kuma mafi nisantarku zama kusa ni a ranar Al-qiyama su ne masu yawan surutu, da masu tsanantawa, da masu Jiji da kai, sai suka ce munsan masu Masu yawan magana da masu tsanantawa kai, to su waye masu Jiji da kai? Sai ya ce: Masu girman kai" Al-silsila Al-Sahiha: 791. An rawaito daga Abdullahi Bn Amr Bn Al--Aas -Allah Ya yarda da su- daga Annabi: Annabi bai kasance mai alfasha ba ko mai yada alfasha ba, kuma ya kasance yana cewa: "Lallai zababbu daga cikinku mafi kyawunku halaye" Sahih Al-Bukhari: 3559. Zuwa wanin haka na ayoyi da hadisai wadanda suke nuna cewa Musulunci yana kwadaitarwa akan kyawawan halaye da kyawawan ayyuka baki daya Musulunci yana umarni da kyawawan dabi'u Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: "Na hore ku da gaskiya saboda gaskiya tana shiryarwa zuwa biyayya, kuma lallai biyayya tana shiryarwa zuwa aljanna, kuma mutum ba zai gushe ba yana yin gaskiya kuma yana kirdadonta har sai Allah Ya rubuta shi a wajenSa cikin masu gaskiya". Sahih Muslim: 2607. Kuma daga cikin abunda Muslunci yayi umarni da shi bayarda amana, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞ إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُكُمۡ أَن تُؤَدُّواْ ٱلۡأَمَٰنَٰتِ إِلَىٰٓ أَهۡلِهَا...٥٨﴾[النساء: 58]

{Lallai Allah yana yana Umartarku da ku Mayar da Amanoni ga Masu su} [al-Nisa: 58] Musulunci yana umarni da kamewa Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: "Mutane guda uku wajibi ne akan Allah Ya taimake su, sai ya fada daga cikinsu mai aure don kame kansa" Sunan al-Tirmizi: 1655. Kuma ya kasance a cikin addu'arsa - SAW - cewa shi yana cewa: "Ya Ubangiji ina rokonka shiriya da tsoron Allah da watadar zuci da wadata" Sahih Muslim: 2721. Kuma Musulunci yana umarni da kunya Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: "kunya bata zuwa sai

da Alkairi" Sahih Al-Bukhari: 6117. Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Kowane Addini yana da kyawawan halaye kuma kyawawan halayen Musulunci sune kunya" Baihaqi ne ya rawaito shi a cikin Rassan Imani 6/2619. Kuma daga cikin abunda Musulunci yake umarni da shi sadaukantaka saboda an rawaito daga Anas -Allah Ya yarda da shi- ya ce: "Manzon Allah - SAW - ya kasance shi ne mafi kyawun mutane kuma mafi sadaukantakarsu kuma mafi kyautarsu kuma haqiqa mutanen Madina sun furgita saboda haka sai Manzon Allah ya riga kowa zuwa wurin a kan doki" Sahih Al-Bukhari: 2820. Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi-ya kasance yana neman tsari daga tsoro saboda haka ya ke cewa Ya Ubangiji ina neman tsarinka daga shaidanu maza da shaidanu mata". Sahih Al-Bukhari: 6374. Kuma daga cikin abunda Muslunci yayi umarni da shi shi kyauta da karamci, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿مَّثَلُ ٱلَّذِينَ يُنفِقُونَ أَمۡوَٰلَهُمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ كَمَثَلِ حَبَّةٍ أَنۢبَتَتۡ سَبۡعَ سَنَابِلَ فِي كُلِّ سُنۢبُلَةٖ مِّاْئَةُ حَبَّةٖۗ وَٱللَّهُ يُضَٰعِفُ لِمَن يَشَآءُۚ وَٱللَّهُ وَٰسِعٌ عَلِيمٌ ٢٦١﴾[البقرة: 261]

{Siffar waɗanda suke ciyar da dũkiyõyinsu a cikin hanyar Allah, kamar sifar ƙwãyã ce wadda ta tsirar da zangarniya bakwai, a cikin kõwace zangarniya akwai ƙwãya ɗari. Kuma Allah Yana riɓinyawa ga wanda Ya so. Kuma Allah Mawadãci ne, Masani} [al-Baqara: 261] Kuma Manzon Allah - SAW - ya kasance daga cikin halayansa akwai karamci saboda an rawaito daga Ibn Abbas -Allah Ya yarda da shi- ya ce: "Manzon Allah - SAW - ya kasance mafi kyautar mutane da Alkairi, kuma lokacin da yafi kowanne kyauta shine lokacin Azumin Ramadana lokacin da Mala'ika Jibril - amincin Allah a gare shi - ya ke

zuwan masa kowane dare a cikin watan Azumi har sai ya wuce yana gabatar masa da Al-qur'ani saboda idan Jibril ya gamu da shi -amincin Allah a gareshi- ya kasance mafi kyauta da alkairi daga sakakkiyar Iska" Sahih Al-Bukhari: 1902. Kuma daga cikin abunda Musulunci y akwadaitar taimakon mabukaci da agazawa wanda ya matsu da ciyar da mai jin yunwa da kuma kyautata maqwaftaka da sadar da zumunci da tausayawa dabbobi" Daga Abdullahi Bin Amr -Allah ya yarda da shi- Cewa wani mutum ya tambayi Manzon Allah -tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi -: Wane aiki ne yafi a Musulunci? ya ce ka ciyar da abinci kuma kayi sallama ga wanda ka sani da wanda baka sani ba" Sahih Al-Bukhari: 12 Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Wata rana wani mutum yana tafiya a hanya sai qishirwa da kama shi sai ya samu wata rijiya sai ya shiga ciki yasha ruwa sannan ya futo sai ga wani kare yana lallagi yana cin yashi saboda kishi sai mutumin ya ce: Lallai wannan karen irin abunda ya kamo ni ne ya kamo shi sai ya shiga rijiyar ya ciko huffinsa sannan ya kama bakinsa ya bashi ruwan sai Allah Ya gode masa kuma Ya gafarta masa" suka ce ya manzon Allah shin zamu samu ladan ciyar da dabbobi, sai ya ce: Eh, a cikin kowace hanta akwai lada" Sahihin Ibn Hibban: 544. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Mai kai kawo ga wacce mijinta ya mutu ko miskini kamar mai jihadi ne a tafarkin Allah ko mai tsayuwar dare kuma mai azumi da rana" Sahih Al-Bukhari: 5353. Kuma Musulunci yana qarfafa kan haqqoqin makusanta kuma yana wajabta sadar da zumunci makusanta, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿ٱلنَّبِيُّ أَوۡلَىٰ بِٱلۡمُؤۡمِنِينَ مِنۡ أَنفُسِهِمۡۖ وَأَزۡوَٰجُهُۥٓ أُمَّهَٰتُهُمۡۗ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُهَٰجِرِينَ إِلَّآ أَن تَفۡعَلُوٓاْ إِلَىٰٓ أَوۡلِيَآئِكُم مَّعۡرُوفٗاۚ كَانَ ذَٰلِكَ فِي ٱلۡكِتَٰبِ مَسۡطُورٗا٦﴾[الأحزاب: 6]

{Annabi ne mafi cancanta ga mũminai bisa ga su kansu, kuma mãtansa uwãyensu ne. Kuma ma'abuta zumunta waɗansunsu sun fi waɗansu a cikin Littãfin Allah bisa ga mũminai da Muhãjirai, fãce fa idan kun aikata wani alhẽri zuwa ga majiɓintanku. Wancan yã kasance a cikin Littafi, rubũtacce} [al-Ahzab: 6], kuma ya tsawatar daga yanke zumunci kuma ya gwamata da barna a bayan kasa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿فَهَلۡ عَسَيۡتُمۡ إِن تَوَلَّيۡتُمۡ أَن تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَتُقَطِّعُوٓاْ أَرۡحَامَكُمۡ٢٢ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ ٱللَّهُ فَأَصَمَّهُمۡ وَأَعۡمَىٰٓ أَبۡصَٰرَهُمۡ٢٣﴾[محمد: 22-23]

{To, shin, kunã fãtan idan kun jũya (daga umurnin) zã ku yi ɓarna a cikin ƙasã, kuma ku yan yanke zumuntarku?(22) Waɗannan sũ ne waɗanda Allah Ya la'anẽ su, sa'an nan Ya kurumtar da su, kuma Ya makantar da ganinsu} [Muhammad: 22-23]. Kuma Manzon Allah - SAW - ya ce: "Ba zai taba shiga aljanna ba wanda ya yanke zumunci" Sahih Muslim: 2556. Kuma makusantar da sadar da zumuncinsu: Iyaye da 'yan Uwa maza da 'yan uwa mata da kawunnai da goggoye da yakumbobi da yadikkoki, kuma Musulunci yana qarfafa haqqin makwaftaka har ko da kuwa ya kasance Kafiri ne, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞وَٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَلَا تُشۡرِكُواْ بِهِۦ شَيۡـٔٗاۖ وَبِٱلۡوَٰلِدَيۡنِ إِحۡسَٰنٗا وَبِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱلۡجَارِ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡجَارِ ٱلۡجُنُبِ وَٱلصَّاحِبِ بِٱلۡجَنۢبِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ وَمَا مَلَكَتۡ أَيۡمَٰنُكُمۡۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ مَن كَانَ مُخۡتَالٗا فَخُورًا٣٦﴾[النساء: 36]

{Kuma ku bauta wa Allah kuma kada ku haɗa wani da Shi, kuma ga mahaifa ku yi kyautatãwa, kuma ga ma'abũcin zumunta da marãyu da matalauta, da maƙwabci ma'abũcin kusanta, da maƙwabci manĩsanci, da abõki a gẽfe da ɗan hanya, da abin da hannuwanku na dãma suka mallaka. Lalle ne Allah bã Ya son wanda ya kasance mai tãƙama, mai yawan alfahari} [al-nisa: 36] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Mala'ika bai gushe ba yana yi mun wasiyya da makwabci har sai da na zaci cewa shi zai gaje shi" Sahihu Abu daud: 5152.

## 33. Musulunci ya halatta abubuwa masu dadi na abun ci da sha, kuma yayi umarni da tsarkin zuciya da jiki saboda haka ya halatta aure, Kamar yadda ya umarci Annabawa -Amincin Allah a gare su- da hakan, saboda su suna umarni ne da dukkan abu mai kyau

Musulunci yana umarni da kyawawan dabi'u Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: Daga Abu Huraira daga Annabi ya ce: "Lallai Allah Mai tsarki ne kuma baya karba sai mai tsarki, kuma Ya umarci muminai da duk abinda Ya umarci manzanninsa da shi, sai ya ce:{Ya ku Manzanni kuci daga dadadan abubuwa kuma kuyi aiki nagari,lallai Ni ina sane da abinda kuke aikatawa} [51] kuma Ya ce:

{Ya ku Masu Imani kuci daga dadadan abinda muka aazurtaku} [Bakara:172] sannan Annabi ya fadi tsawatarwa ga al'ummarsa daga haram; sabida ya ambaci wani mutum da yake yawaita tafiya, kuma acikin ayyukan alheri kamar hajji da Jihadi da kuma neman abinci, gashi budubudu yake gashinsa yayi kura sabida tsawon tafiyarsa a cikin bin Allah, kuma yana daga hannunsa sama da addua yana rokon Allah da kuma kaskantar da kansa

izuwa ga Allah, kuma tare da hakan an nisanta amsa masa wannan adduar tasa, saboda munin abinda yayi, ta yadda abincinsa ya kasance haram ne abun shansa haram ne. Sahih Muslim: 1015. Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce: Ka ce:

﴿قُلۡ مَنۡ حَرَّمَ زِينَةَ ٱللَّهِ ٱلَّتِيٓ أَخۡرَجَ لِعِبَادِهِۦ وَٱلطَّيِّبَٰتِ مِنَ ٱلرِّزۡقِۚ قُلۡ هِيَ لِلَّذِينَ ءَامَنُواْ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا خَالِصَةٗ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِۗ كَذَٰلِكَ نُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ٣٢﴾[الأعراف: 32]

{Wãne ne ya haramta ƙawar Allah, wadda Ya fitar sabõda bãyinSa, da mãsu dãɗi daga abinci?" Ka ce: "Sũ, dõmin waɗanda suka yi ĩmani suke a cikin rãyuwar dũniya, suna keɓantattu a Rãnar Kiyãma. "Kamar wannan ne Muke bayyana ãyõyi, daki-daki, ga mutãnen da suke sani} [al-A'araf: 32 Kuma Musulmi yayi umarni da tsarkin zuciya da kuma jiki da gida saboda wancan ya halatta aure kamar yadda Ya umarci Annabawa da manzanni da wancan batu, sabo sune suke umarni da dukkan abunda yake kyakkyawa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَٱللَّهُ جَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَنفُسِكُمۡ أَزۡوَٰجٗا وَجَعَلَ لَكُم مِّنۡ أَزۡوَٰجِكُم بَنِينَ وَحَفَدَةٗ وَرَزَقَكُم مِّنَ ٱلطَّيِّبَٰتِۚ أَفَبِٱلۡبَٰطِلِ يُؤۡمِنُونَ وَبِنِعۡمَتِ ٱللَّهِ هُمۡ يَكۡفُرُونَ ٧٢﴾[النحل: 72]

{Kuma Allah Yã sanya muku mãtan aure daga kãwunanku, kuma Ya sanya muku daga mãtan aurenku ɗiyã da jĩkõki, kuma Ya arzũta ku daga abũbuwa mãsu dãɗi. Shin fa, da ƙarya suke yin ĩmãni, kuma da ni'imar Allah sũ, suke kãfirta?} [al-Nahl: 72] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَثِيَابَكَ فَطَهِّرۡ ٤ وَٱلرُّجۡزَ فَٱهۡجُرۡ ٥﴾[المدثر: 4-5]

{Kuma tufafinka to ka tasarlaleta" (4) Kuma Gumaka ka kaurace musu (5)} [al-Mudathir: 4-5] Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Babu wanda zai shiga aljanna wanda yakasance a cikin zuciyarsa akwai girman kai

gwargwadon qwayar zarra a zuciyarsa, sai wani mutum ya ce: Lallai mutum yana son ya kasance tufafinsa suyi fesfes kuma takalmasa ma fesfes sai ya ce: Lallai Allah ai Mai kyau ne kuma yana son kyau, girman kai shi ne take gaskiya da kuma raina mutane" Sahih Muslim: 91.

**34. Musulunci ya haramta dukkan tushen dukkan haramun kamar shirka da bautar gumaka, da shaci fadi ga Allah bada Ilimi ba, da kashe 'ya'ya da kashe ran da Allah ya haramta, da barna a bayan kasa, da sihiri da alfasha ta fili da ta boye da zina da Liwadi, kuma ya haramta riba, da cin mushe, da abunda aka yanka ga gumaka da dodanni, da kuma cin naman alade, da sauran najasa da kazanta, kuma ya haramta cin dukiyar maraya da tauye mudu da ma'auni, kuma ya haramta yanke zumunci kuma Annabawa -Amincin Allah a gare su- baki dayansu sun hadu kan haramcin wadan nan abubuwan**

Musulunci ya haramta tushen haramun, kamar shirka da Allah da kafirci da bautar gumaka da fadi ga Allah ba tare da ilimi ba da kashe "ya'ya, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قُلْ تَعَالَوْاْ أَتْلُ مَا حَرَّمَ رَبُّكُمْ عَلَيْكُمْۖ أَلَّا تُشْرِكُواْ بِهِۦ شَيْـًٔاۖ وَبِٱلْوَٰلِدَيْنِ إِحْسَٰنًاۖ وَلَا تَقْتُلُوٓاْ أَوْلَٰدَكُم مِّنْ إِمْلَٰقٖ نَّحْنُ نَرْزُقُكُمْ وَإِيَّاهُمْۖ وَلَا تَقْرَبُواْ ٱلْفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنْهَا وَمَا بَطَنَۖ وَلَا تَقْتُلُواْ ٱلنَّفْسَ ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلْحَقِّۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَعْقِلُونَ ١٥١ وَلَا تَقْرَبُواْ مَالَ ٱلْيَتِيمِ إِلَّا بِٱلَّتِي هِيَ أَحْسَنُ حَتَّىٰ يَبْلُغَ أَشُدَّهُۥۚ وَأَوْفُواْ ٱلْكَيْلَ وَٱلْمِيزَانَ بِٱلْقِسْطِۖ لَا نُكَلِّفُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَاۖ وَإِذَا قُلْتُمْ فَٱعْدِلُواْ وَلَوْ كَانَ ذَا قُرْبَىٰۖ وَبِعَهْدِ ٱللَّهِ أَوْفُواْۚ ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَذَكَّرُونَ ١٥٢﴾[الأنعام: 151-152]

{Ka ce: "Ku zo, in karanta abin da Ubangijinku Ya haramta." wãjibi ne a kanku kada ku yi shirkin kõme da Shi, kuma ga

mahaifa biyu (ku kyautata) kyautatãwa, kuma kada ku kashe ɗiyanku sabõda talauci, Mũ ne Muke azurta ku, kũ da su, kuma kada ku kusanci abũbuwa alfãsha, abin da ya bayyana daga gare ta da abin da ya ɓõyu, kada ku kashe rai wanda Allah Ya haramta, fãce da hakki. Wannan ne (Allah) Ya yi muku wasiyya da Shi: Tsammãninku, kunã hankalta. Kada ku kusanci dũkiyar marãya fãce da wadda take ita ce mafi kyau, har ya kai ga ƙarfinsa. Kuma ku cika mũdu da sikẽli da ãdalci, bã Mu kallafã wa rai fãce iyãwarsa. Kuma idan kun faɗi magana, to, ku yi ãdalci, kuma ko dã yã kasance ma'abũcin zumunta ne. Kuma da alkawarin Allah ku cika. wannan ne Ya yi muku wasiyya da shi: Tsammãninku, kunã tunãwa} [al-An'am: 151-152], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿قُلۡ إِنَّمَا حَرَّمَ رَبِّيَ ٱلۡفَوَٰحِشَ مَا ظَهَرَ مِنۡهَا وَمَا بَطَنَ وَٱلۡإِثۡمَ وَٱلۡبَغۡيَ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَأَن تُشۡرِكُواْ بِٱللَّهِ مَا لَمۡ يُنَزِّلۡ بِهِۦ سُلۡطَٰنٗا وَأَن تَقُولُواْ عَلَى ٱللَّهِ مَا لَا تَعۡلَمُونَ ٣٣﴾[الأعراف: 33]

{Ka ce: "Abin sani kawai, Ubangijina Yã hana abũbuwanalfãsha; abin da ya bayyana daga gare su da abin da ya ɓõyu, da zunubi da rarraba jama'a, bã da wani hakki ba, kuma da ku yi shirki da Allah ga abin da bai saukar da wani dalĩli ba gare shi, kuma da ku faɗi abin da ba ku sani ba, ga Allah} [al-A'araf: 33], kuma Musulunci ya haramta kashe rai da baiyi laifin komai ba, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَلَا تَقۡتُلُواْ ٱلنَّفۡسَ ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلۡحَقِّۗ وَمَن قُتِلَ مَظۡلُومٗا فَقَدۡ جَعَلۡنَا لِوَلِيِّهِۦ سُلۡطَٰنٗا فَلَا يُسۡرِف فِّي ٱلۡقَتۡلِۖ إِنَّهُۥ كَانَ مَنصُورٗا ٣٣﴾[الإسراء: 33]

{Kuma kada ku kashe rai wanda Allah Ya haramta fãce da haƙƙi, kuma wanda aka kashe, yanã wanda aka zãlunta to,

haƙĩƙa Mun sanya hujja ga waliyyinsa, sai dai kada ya ƙẽtare haddi a cikin kashẽwar. Lalle shĩ ya kasance wanda ake taimako} [al-Israa: 33] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ لَا يَدۡعُونَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ وَلَا يَقۡتُلُونَ ٱلنَّفۡسَ ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَلَا يَزۡنُونَۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ يَلۡقَ أَثَامًا ٦٨﴾[الفرقان: 68]

{Kuma waɗanda bã su kiran wani ubangiji tãre da Allah, kuma bã su kashe rai wanda Allah Ya haramta fãce da hakki kuma bã su yin zina. Kuma wanda ya aikata wancan, zai gamu da laifuffuka} [al-Furqan: 68], kuma Musulunci ya haramta barna a bayan kasa, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَلَا تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ بَعۡدَ إِصۡلَٰحِهَا... ٥٦﴾ [الأعراف: 56]

{Kuma kada kuyi barna a bayan Qasa bayan ai gyara ta} [al-A'araf: 58] Kuma Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce game da Annabi Shu'abu -Amincin Allah a gare shi- cewa ya ce da mutanen sa:

﴿وَإِلَىٰ مَدۡيَنَ أَخَاهُمۡ شُعَيۡبٗاۚ قَالَ يَٰقَوۡمِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مَا لَكُم مِّنۡ إِلَٰهٍ غَيۡرُهُۥۖ قَدۡ جَآءَتۡكُم بَيِّنَةٞ مِّن رَّبِّكُمۡۖ فَأَوۡفُواْ ٱلۡكَيۡلَ وَٱلۡمِيزَانَ وَلَا تَبۡخَسُواْ ٱلنَّاسَ أَشۡيَآءَهُمۡ وَلَا تُفۡسِدُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ بَعۡدَ إِصۡلَٰحِهَاۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ٨٥﴾[الأعراف: 85]

{Ya mutãnena! Ku bauta wa Allah; bã ku da wani abin bauta wa waninSa. Lalle ne, wata hujja bayyananniya daga Ubangijinku tã zõ muku! Sai ku cika mũdu da sikeli kumakada ku nakasa wa mutãne kãyansu, kuma kada ku yi fasãdi a cikin ƙasa a bãyan gyaranta. Wannan ne mafi alhẽri a gare ku, idan kun kasance mũminai} [al-a'araf: 85]. Kuma Allah Ya haramta sihiri, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَأَلْقِ مَا فِي يَمِينِكَ تَلْقَفْ مَا صَنَعُوٓاْۖ إِنَّمَا صَنَعُواْ كَيْدُ سَٰحِرٍۖ وَلَا يُفْلِحُ ٱلسَّاحِرُ حَيْثُ أَتَىٰ ٦٩﴾[طه: 69]

{Kuma ka jẽfa abin da ke a cikin hannun dãmanka, ta cafe abin da suka aikata. Lalle ne abin da suka aikata mãkircin masihirci ne kuma masihirci bã ya cin nasara a duk inda ya je} [Daha: 69]. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: Ku guji abubuwa bakwai masu halakarwa suka ce ya Ma'aikin Allah! wadanne ne su? ya ce: Yin shirka da Allah, da sihiri, da kashe rai wacce Allah Ya haramta face da gaskiya, da cin riba, da cin dukiyar maraya, da juyawa ranar yaki, da kuma yiwa katangaggiya marafkaniya mumina kazafi". Sahih Al-Bukhari: 6583. Kuma Musulunci ya haramta alfasha ta fili da boye da zina da luwadi kuma ya gabata a cikin farkon wannan lokaci ya fadi dalilai akan hakan kuma Musulun ya haramta riba, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَذَرُواْ مَا بَقِيَ مِنَ ٱلرِّبَوٰٓاْ إِن كُنتُم مُّؤْمِنِينَ ٢٧٨ فَإِن لَّمْ تَفْعَلُواْ فَأْذَنُواْ بِحَرْبٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦۖ وَإِن تُبْتُمْ فَلَكُمْ رُءُوسُ أَمْوَٰلِكُمْ لَا تَظْلِمُونَ وَلَا تُظْلَمُونَ ٢٧٩﴾[البقرة: 278-279]

{Yã ku waɗanda suka yi ĩmãni! Ku bi Allah da taƙawa kuma ku bar abin da ya rage daga riba, idan kun kasance mãsu ĩmãni.(278) To, idan ba ku aikata ba to, ku sani fa da akwai yãƙi daga Allah da ManzonSa. Kuma idan kun tũba to kuna da asalin dũkiyõyinku, bã ku zãlunta, kuma bã a zãluntar ku(279)} [al-Baqara: 278-279]. Kuma Allah bai tsawatar da mai sabo ba da yaqi kamar yadda ya tsawatar da ma'abocin riba; saboda a cikin riba akawai ruguza Addinai da kasashe da dukiyoyi da kawuna, kuma Musulunci ya haramta cin mushe da abunda aka

yanka ga gumaka da dodanni kuma ya haramta naman alade, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿حُرِّمَتۡ عَلَيۡكُمُ ٱلۡمَيۡتَةُ وَٱلدَّمُ وَلَحۡمُ ٱلۡخِنزِيرِ وَمَآ أُهِلَّ لِغَيۡرِ ٱللَّهِ بِهِۦ وَٱلۡمُنۡخَنِقَةُ وَٱلۡمَوۡقُوذَةُ وَٱلۡمُتَرَدِّيَةُ وَٱلنَّطِيحَةُ وَمَآ أَكَلَ ٱلسَّبُعُ إِلَّا مَا ذَكَّيۡتُمۡ وَمَا ذُبِحَ عَلَى ٱلنُّصُبِ وَأَن تَسۡتَقۡسِمُواْ بِٱلۡأَزۡلَٰمِۚ ذَٰلِكُمۡ فِسۡقٌۗ...٣﴾[المائدة: 3]

{An haramta muku mũshe da jini da nãman alade da abin da aka ambaci sũnan wanin Allah a gare shi, da mãƙararriya da jefaffiya da mai gangarõwa da sõkakkiya, da abin da mãsu dãgi suka ci, fãce abin da kuka yanka}. [Al-Maa'ida: 3]. Kuma Musulunci Ya haramta shan giya da sauran najasosi da munanan abubuwa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡخَمۡرُ وَٱلۡمَيۡسِرُ وَٱلۡأَنصَابُ وَٱلۡأَزۡلَٰمُ رِجۡسٞ مِّنۡ عَمَلِ ٱلشَّيۡطَٰنِ فَٱجۡتَنِبُوهُ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٩٠ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَن يُوقِعَ بَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةَ وَٱلۡبَغۡضَآءَ فِي ٱلۡخَمۡرِ وَٱلۡمَيۡسِرِ وَيَصُدَّكُمۡ عَن ذِكۡرِ ٱللَّهِ وَعَنِ ٱلصَّلَوٰةِۖ فَهَلۡ أَنتُم مُّنتَهُونَ ٩١﴾[المائدة: 90-91]

{Ya ku waɗanda suka yi ĩmãni! Abin sani kawai, giya da cãca da refu da kiban ƙuri'a, ƙazanta ne daga aikin shaiɗan, sai ku nĩsance shi, wa la'alla ku ci nasara.(90) Abin sani kawaĩ Shaiɗan yanã nufin ya aukar da adãwa da ƙeta a tsakãninku, a cikin giya da cãca, kuma ya kange ku daga ambaton Allah, kuma daga sallah. To, shin, ku mãsu hanuwa ne?(91)} [al-Ma'ida: 90-91], kuma ya gabata a cikin sakin layi mai lamba ta (31) bayanin labarin Allah - SWT - cewa daga cikin siffofin Manzon Allah - SAW - a cikin Al-taura cewa shi Ya haramta munanan abubuwa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ يَتَّبِعُونَ ٱلرَّسُولَ ٱلنَّبِيَّ ٱلۡأُمِّيَّ ٱلَّذِي يَجِدُونَهُۥ مَكۡتُوبًا عِندَهُمۡ فِي ٱلتَّوۡرَىٰةِ وَٱلۡإِنجِيلِ يَأۡمُرُهُم بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَىٰهُمۡ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ وَيُحِلُّ لَهُمُ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَيُحَرِّمُ عَلَيۡهِمُ ٱلۡخَبَٰٓئِثَ وَيَضَعُ عَنۡهُمۡ إِصۡرَهُمۡ وَٱلۡأَغۡلَٰلَ ٱلَّتِي كَانَتۡ عَلَيۡهِمۡۚ...١٥٧﴾[الأعراف: 157]

{Waɗanda suke sunã bin Manzo, Annabi, Ummiyyi wanda suke sãmun sa rubũce a wurinsu, a cikin Attaura da Linjĩla.yanã umurnin su da alhẽri, kuma yana hana su daga barin abin da bã a so; kuma yana halatta musu abũ- buwa masu dadi, kuma yana haramtarwar mũnana a kansu. Kuma yanã kãyar da nauyinsu daga barinsu, da ƙuƙummai waɗannan da suka kasance a kansu} [al-A'araf: 157] kuma Musulunci ya haramta cinye dukiyar maraya, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَءَاتُواْ ٱلۡيَتَٰمَىٰٓ أَمۡوَٰلَهُمۡۖ وَلَا تَتَبَدَّلُواْ ٱلۡخَبِيثَ بِٱلطَّيِّبِۖ وَلَا تَأۡكُلُوٓاْ أَمۡوَٰلَهُمۡ إِلَىٰٓ أَمۡوَٰلِكُمۡۚ إِنَّهُۥ كَانَ حُوبٗا كَبِيرٗا٢﴾[النساء: 2]

{Kuma ku bai wa marãyu dũkiyõyinsu, kuma kada ku musanya mummuna da mai kyau. Kuma kada ku ci dũkiyõyinsu zuwa ga dũkiyõyinku. Lalle shi, yã kasance zunubi ne mai girma} [al-Nisa'a: 2] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَأۡكُلُونَ أَمۡوَٰلَ ٱلۡيَتَٰمَىٰ ظُلۡمًا إِنَّمَا يَأۡكُلُونَ فِي بُطُونِهِمۡ نَارٗاۖ وَسَيَصۡلَوۡنَ سَعِيرٗا١٠﴾[النساء: 10]

{Lalle ne, waɗanda suke cĩn dũkiyar marãyu da zãlunci, to, wuta kawai suke ci a cikin cikkunansu, kuma za su shiga cikin wata wuta mai tsanani} [al-Nisa'a: 10] kuma Musulunci ya haramta tauye mudu, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَيۡلٞ لِّلۡمُطَفِّفِينَ١ ٱلَّذِينَ إِذَا ٱكۡتَالُواْ عَلَى ٱلنَّاسِ يَسۡتَوۡفُونَ٢ وَإِذَا كَالُوهُمۡ أَو وَّزَنُوهُمۡ يُخۡسِرُونَ٣ أَلَا يَظُنُّ أُوْلَٰٓئِكَ أَنَّهُم مَّبۡعُوثُونَ٤﴾[المطففين: 1-4]

{Bone ya tabbata ga Masu tauye Mudu (1) Waɗanda suke idan suka auna daga mutãne suna cika mũdu.(2) Kuma idan sun auna musu da zakka ko da sikẽli, suna ragẽwa(3) Ashe! Waɗancan bã su tabbata cẽwa lalle sũ, ana tãyar da su ba?(4)} [al-Muxaffifin: 1-4]

kuma Musulunci Ya haramta yanke zumunci kuma ya gabata a sakin layi mai lamba (31) fadin ayoyi da hadisai wadan da suke nuni kan hakan, Kuma baki dayan Annabawa da Manzanni -Amincin Allah a garesu- baki dayan su sun hadu kan haramcin wadan nan haramtattun abubuwan.

**35. Musulunci ya hana munanan halaye kamar karya da ha'inci da yaudara da ha'inci da danfara, da hassada da mummunan kaidi da sata da zalunci, kuma ya na hana dukkan wani mummunan hali**

Musulunci ya na hana munanan ayyuka baki daya, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَلَا تُصَعِّرْ خَدَّكَ لِلنَّاسِ وَلَا تَمْشِ فِي ٱلْأَرْضِ مَرَحًاۖ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ كُلَّ مُخْتَالٖ فَخُورٖ ١٨﴾[لقمان: 18]

{Kada ka karkatar da kundukukinka ga mutãne, kada ka yi tafiya a cikin ƙasã kanã mai nũna fãɗin rai. Lalle, Allah bã Ya son dukan mai tãƙama, mai alfahari} [Luqman:18] Manzon Allah - tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce "Lallai wanda ya fiku soyuwa a gare ni kuma mafi kusancinku mazauni a ranar Al-kiyama mafi kyawunku halayya, kuma mafi qinku a gare ni, kuma mafi nisanku dani a wajen zama a ranar Al-qiyama masu surutu da masu tsanantawa da masu girman kai, suka ce ya Manzon Allah haqiqa munsan masu surutu da masu tsanantawa to su waye masujiji da kai ya ce: Masu

girman kai" Al-silsila Al-Sahiha: 791 Musulunci yana hani daga karya, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿... إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ مُسۡرِفٞ كَذَّابٞ ٢٨﴾[غافر: 28]

{Lallai Allah baya shiryar da wanda yake mai barna kuma mai yawan karya} [Ghafir: 28] Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Na hane ku da bari qarya saboda qarya tana shiryarwa zuwa fajirci, kuma lallai fajirci yana shiryarwa zuwa wuta kuma mutum ba zai gushe ba yana yin karya kuma yana kirdadonta har sai Allah Ya rubuta shi a wajensa maqaryaci" Sahih Muslim: 2607. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Alamomin munafuki uku ne: Idan yai zance sai yayi karya, kuma idan yayi alkawari sai ya saba, kuma idan aka amince masa sai yayi ha'inci" Sahih Al-Bukhari: 6095. Musulunci yana hana algus" Kuma ya zo a cikin Hadisi cewa Manzon Allah - SAW - ya wuce a wata shinfidar abinci sai ya shigar da hannunsa a cikinta sai ya ji danshi sai ya ce: "Maye haka ya kai mai wannan abinci?" sai ya ce: Ruwan sama ne ya same shi ya Manzon Allah sai ya ce: To ba sai kasanya shi ba a saman abincin don mutane su gani to duk wanda ya ha'ince mu to baya tare da ni" Sahih Muslim: 102. Musulunci yana hani daga yaudara da ha'inci, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَخُونُواْ ٱللَّهَ وَٱلرَّسُولَ وَتَخُونُوٓاْ أَمَٰنَٰتِكُمۡ وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ ٢٧﴾

{Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Kada ku yaudari Allah da ManzonSa, kuma ku yaudari amãnõninku, alhãli kuwa kunã sane} [al-Anfal: 27] kuma Allah - Madaukaki - Ya ce

﴿ٱلَّذِينَ يُوفُونَ بِعَهۡدِ ٱللَّهِ وَلَا يَنقُضُونَ ٱلۡمِيثَٰقَ ٢٠﴾[الرعد: 20]

{Sũ ne waɗanda suke cikãwa da alkawarin Allah, kuma bã su warware alkawari} [al-Ra'ad: 20] "Manzon Allah -tsira da amincin Allah- ya kasance yana cewa da rundunarsa idan suka futo: "Kuyi yaqi kada kuyi azarbabi kuma kuyi yaudara kada kuyi musla kuma kada ku kashe yaro" Sahih Muslim: 1731. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Abubuwa guda hudu duk wanda ya kasance a cikinsu ya zamano munafuki tsantsa kuma duk wanda yake yana da wani hali daga cikinsu to ya kasance yana da wani abu daga cikin munafunci har sai ya barshi idan aka amince masa sai yayi ha'inci kuma idan yayi zance sai yayi karya, kuma idan yayi alkawari sai sai yayi yaudara, kuma idan aka yi fada da shi sai yayi fajirci" Sahih Al-Bukhari: 34. Musulunci yana hani daga hassada, Allah - Madauakaki - Ya ce:

﴿أَمۡ يَحۡسُدُونَ ٱلنَّاسَ عَلَىٰ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦۖ فَقَدۡ ءَاتَيۡنَآ ءَالَ إِبۡرَٰهِيمَ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَءَاتَيۡنَٰهُم مُّلۡكًا عَظِيمٗا ٥٤﴾[النساء: 54]

{Ko suna hãsadar mutãne ne a kan abin da Allah Ya bã su daga falalarSa? To, lalle ne, Mun bai wa gidan Ibrãhĩm Littãfida hikima kuma Mun bã su mulki mai girma} [al-Nisa'a: 54] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَدَّ كَثِيرٞ مِّنۡ أَهۡلِ ٱلۡكِتَٰبِ لَوۡ يَرُدُّونَكُم مِّنۢ بَعۡدِ إِيمَٰنِكُمۡ كُفَّارًا حَسَدٗا مِّنۡ عِندِ أَنفُسِهِم مِّنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلۡحَقُّۖ فَٱعۡفُواْ وَٱصۡفَحُواْ حَتَّىٰ يَأۡتِيَ ٱللَّهُ بِأَمۡرِهِۦٓۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ١٠٩﴾[البقرة: 109]

{Mãsu yawa daga Ma'abuta Littãfi sunã gũrin dã sun mayar da ku, daga bãyan ĩmãninku, kãfirai, sabõda hãsada daga wurin rãyukansu, daga bayãn gaskiya tã bayyana a gare su. To, ku yãfe, kuma ku kau da kai, sai Allah Yã zo da umurninSa. Lalle ne

Allah a kan dukkan kõme Mai ĩkon yi ne} [al-Baqara: 109]. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Cutar al’umman da suka gabace ku ya shigo ku hassada da keta ita ce mai askewa ba ina nufin mai aske gashin kai ba, sai dai tana aske Addni, na rantse da wanda raina yake hannunSa ba zaku taba shiga aljanna ba har sai kunyi imani kuma ba zaku tava yin imani ba har sai kun so junanku kuma bana baku labarin abunda zai tabbatar muku da wancan din ba? to ku yada Sallama a tsakaninku" Sunan al-Tirmizi: 2510. Musulunci yana hani daga mummunan kulli, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَكَذَٰلِكَ جَعَلۡنَا فِي كُلِّ قَرۡيَةٍ أَكَٰبِرَ مُجۡرِمِيهَا لِيَمۡكُرُواْ فِيهَاۖ وَمَا يَمۡكُرُونَ إِلَّا بِأَنفُسِهِمۡ وَمَا يَشۡعُرُونَ ١٢٣﴾[الأنعام: 123]

{Kuma kamar wancan ne Mun sanya a cikin kõwace alƙarya, shugabanni sũ ne mãsu laifinta dõmin su yi mãkirci a cikinta, alhãli kuwa ba su yin makirci fãce ga rayukansu, kuma ba su sansancẽwa} [al-An'am: 123] Kuma Allah Ya bada labarin cewa Yahudawa sunyi niyyar kashe Annabi Isa -Amincin Allah a gare shi- kuma sunyi makirci sai dai Allah Ya mayar musu da makircinsu kuma Allah Ya bayyana cewa mummunan makirci baya fadawa ko ina sai ga mai shi, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞ فَلَمَّآ أَحَسَّ عِيسَىٰ مِنۡهُمُ ٱلۡكُفۡرَ قَالَ مَنۡ أَنصَارِيٓ إِلَى ٱللَّهِۖ قَالَ ٱلۡحَوَارِيُّونَ نَحۡنُ أَنصَارُ ٱللَّهِ ءَامَنَّا بِٱللَّهِ وَٱشۡهَدۡ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ٥٢ رَبَّنَآ ءَامَنَّا بِمَآ أَنزَلۡتَ وَٱتَّبَعۡنَا ٱلرَّسُولَ فَٱكۡتُبۡنَا مَعَ ٱلشَّٰهِدِينَ ٥٣ وَمَكَرُواْ وَمَكَرَ ٱللَّهُۖ وَٱللَّهُ خَيۡرُ ٱلۡمَٰكِرِينَ ٥٤ إِذۡ قَالَ ٱللَّهُ يَٰعِيسَىٰٓ إِنِّي مُتَوَفِّيكَ وَرَافِعُكَ إِلَيَّ وَمُطَهِّرُكَ مِنَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَجَاعِلُ ٱلَّذِينَ ٱتَّبَعُوكَ فَوۡقَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِلَىٰ يَوۡمِ ٱلۡقِيَٰمَةِۖ ثُمَّ إِلَيَّ مَرۡجِعُكُمۡ فَأَحۡكُمُ بَيۡنَكُمۡ فِيمَا كُنتُمۡ فِيهِ تَخۡتَلِفُونَ ٥٥﴾[آل عمران: 52-55]

{To, a lõkacin da Ĩsa ya gane kãfirci daga gare su, sai ya ce: "Su wãne ne mataimakãna zuwa ga Allah?" Hawãriyãwa suka ce: "Mu ne mataimakan Allah. Mun yi ĩmani da Allah. Kuma ka shaida cẽwa lalle ne mu, mãsu sallamãwa ne.(52) "Yã Ubangijinmu! Mun yi imãni da abin da Ka saukar, kuma mun bi ManzonKa, sai Ka rubũta mu tãre da mãsu shaida.(53) Kuma (Kãfirai) suka yi mãkirci, Allah kuma Ya yi musu (sakamakon) makircin, kuma Allah ne Mafi alhẽrin mãsu sãka wamãkirci (34) A lõkacin da Ubangiji Ya ce: "Ya Ĩsa! Lalle NĨ Mai karɓar ranka ne, kuma Mai ɗauke ka ne zuwa gare Ni, kuma Mai tsarkake ka daga waɗanda suka kãfirta, kuma Mai sanya waɗanda suka bĩ ka a bisa waɗanda suka kãfirta har Rãnar ¡iyãma. Sa'an nan kuma zuwa gare Ni makõmarku take, sa'an nan in yi hukunci a tsakãninku, a cikin abin da kuka kasance kuna sãɓã wa jũna(55)} [Ali Imran: 52-56] Kuma Allah - Madaukaki - Ya bada labarin cewa mutanen Annabi Salih -Amincin Allah a gare shi- sunyi nufin kashe shi da makirci sai sukai mugun shiri sai Allah Ya mayar musu da makircinsu, kuma ya ruguzasu da mutanensu baki daya, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قَالُواْ تَقَاسَمُواْ بِٱللَّهِ لَنُبَيِّتَنَّهُۥ وَأَهۡلَهُۥ ثُمَّ لَنَقُولَنَّ لِوَلِيِّهِۦ مَا شَهِدۡنَا مَهۡلِكَ أَهۡلِهِۦ وَإِنَّا لَصَٰدِقُونَ ٤٩ وَمَكَرُواْ مَكۡرٗا وَمَكَرۡنَا مَكۡرٗا وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٥٠ فَٱنظُرۡ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ مَكۡرِهِمۡ أَنَّا دَمَّرۡنَٰهُمۡ وَقَوۡمَهُمۡ أَجۡمَعِينَ ٥١﴾ [النمل: 49-51]

{Kuma suka ƙulla mãkirci, kuma Muka ƙulla sakamakon mãkirci, alhãli sũ ba su sani ba.(49) Ka dũba yadda ãƙibar mãkircinsu ta kasance lalle Mũ Mun darkãke su da mutãnensu, gabã ɗaya.(50) Waɗancan, gidãjensu ne, wõfintattu sabõda zãluncin da suka yi, lalle ne a wancan akwai ãyã ga mutãne

waɗanda suke sani(51)} [al-Naml: 49-51] Musulunci yana hani daga sata, Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: "Mai zina ba zai taba yin zina ba a halin yana mumini, haka barawo bazai sata ba lokacin da yake sata yana mumini, kuma mashayin giya ba zai sha ba a halin yana mumini, kuma tuba yana nan dai" Sahih Al-Bukhari: 6810 Musulunci yana hani daga zalunci, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿۞إِنَّ ٱللَّهَ يَأۡمُرُ بِٱلۡعَدۡلِ وَٱلۡإِحۡسَٰنِ وَإِيتَآيِٕ ذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَيَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِ وَٱلۡبَغۡيِۚ يَعِظُكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَذَكَّرُونَ ٩٠﴾[النحل: 90]

{Lalle Allah nã yin umurni da ãdalci da kyautatãwa, da bai wa ma'abũcin zumunta, kuma yanã hani ga alfãsha da abin da aka ƙi da rarrabe jama'a. Yanã yi muku gargaɗi, ɗammãnin ku, kunã tunãwa} [al-Nahl: 90] Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: Lallai Allah - Madaukakin Sarki - Yayi min wahayi cewa ku kaskantar da kanku, ha yadda babu wani da zai yi alunci kan wani, kuma kada daya ya yi fariya akan wani" Sahihu Abu daud: 4895. Musulunci yana hani daga zalunci, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿...وَٱللَّهُ لَا يُحِبُّ ٱلظَّٰلِمِينَ ٥٧﴾[آل عمران: 57]

{Kuma Allah baya son azzalumai} [Aal Imran: 57] kuma Allah - Madaukaki - Ya ce

﴿...إِنَّهُۥ لَا يُفۡلِحُ ٱلظَّٰلِمُونَ ٢١﴾[الأنعام: 21]

{Lallai Al-zalumai basa rabauta} [al-An'am: 21] kuma Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿... وَٱلظَّٰلِمِينَ أَعَدَّ لَهُمۡ عَذَابًا أَلِيمَۢا ٣١﴾[الإنسان: 31]

{Kuma Al-zalumai ya tanadar musu azaba mai radadi} [al-Insan: 31], Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a

gare shi - ya ce: "Mutane uku ba'a mayar da Adddu'arsu: Shugaba adali da mai Azumi har sai ya sha ruwa da Addu'ar wanda aka zalunta ka dorata akan girgije kuma a bude mata kofofin sammai kuma yace Ya Ubangiji na rantse da girmana zan taimakeka koda kuwa bayan zamani ne" Muslim ne ya rawaito shi (2749) a takaice da dan sabani kadan, da kuma Tirmizi (2526) da dan sabani kadan, kuma Ahmad (8043) kuma lafazin nasa ne, Kuma yayin da Manzo - SAW - ya tura Mu'az zuwa Yeman ya na mai kira zuwa Musulunci sai ya ce da shi: "Kaji tsoron Addu'ar wanda aka zalunta saboda cewa ita babu wani hijabi tsakaninta da Allah" Sahih Al-Bukhari: 1496. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "ku saurara duk wanda ya zalunci kafirin amana ko ya wulaqanta shi ko ya dora masa abunda yafi qarfinsa ko ya karbi wani abu da da yardar sa ba to nine zan tsaya in yi jayayya da shi a Ranar al-qiyama" Sunan Abi Daud 3052. Saboda Musulunci kamar yadda ka gani yana hana kowace irin mummunan hali ko mu'amala ta zalunci ko ta cuta.

**36. Musulunci ya hana muna nan mua'amalolin kudi waxanda cikinsu akwai riba ko cutarwa ko kuma garari ko zalunci ko algus, ko kuma yana kaiwa zuwa ga masifu, ko cutarwa da zata game baki dayan kasashe da kuma mutane da daidaiku**

Musulunci ya hana muna nan mua'amalolin kudi wadanda cikinsu akwai riba ko cutarwa ko kuma garari ko zalunci ko algus, ko kuma yana kaiwa zuwa ga masifu, ko cutarwa da zata game baki dayan kasashe da kuma mutane da daidaiku, kuma ya gabata a cikin farkon sakin layi da aka fadi ayoyi da hadisan da aka haramta riba ko zalunci ko ha'inci ko barna a bayan kasa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ بِغَيۡرِ مَا ٱكۡتَسَبُواْ فَقَدِ ٱحۡتَمَلُواْ بُهۡتَٰنٗا وَإِثۡمٗا مُّبِينٗا ٥٨﴾ [الأحزاب: 58]

{Kuma waɗanda suke cũtar mũminai maza dã muminai mãtã, bã da wani abu da suka aikata ba to, lalle sun ɗauki ƙiren ƙarya da zunubi bayyananne} [al-Ahzab: 58] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿مَّنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا فَلِنَفۡسِهِۦۖ وَمَنۡ أَسَآءَ فَعَلَيۡهَاۗ وَمَا رَبُّكَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ٤٦﴾[فصلت: 46]

{Wanda ya aikata aiki na ƙwarai to sabõda kansa ne, kuma wanda ya mũnanã, to, yanã akansa. Kuma Ubangiwinka, bã Mai zãlunci ga bãyinSa ne ba} [Fussilat: 46] Kuma ya zo a cikin Sunna: "Cewa Manzon Allah - SAW - yayi hukunci cewa babu cuta babu cutarwa" Sunan Abi Daud, Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: Duk wanda yai imani da Allah da ranar lahira to ya fadi alkairi ko yayi shiru, kuma duk wanda yayi imani da Allah da ranar lahira to ta girmama makwabcinsa, kuma duk wanda yayi imani da Allah da ranar lahira to ta girmama to ya girmama bakonsa Sahih Muslim: 47. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Anyiwa wata mata azaba saboda mage da ta kulle har ta mutu saboda ita aka saka ta a cikin wuta ita bata bata abinci ba ko ruwa ita kuma bata barta ba ta tafi taci kwarin bayan kasa" Sahih Al-Bukhari: 3482. Wannan fa ga wanda ya cutar da mage ne to mai kake zaton wanda yake cutar da mutane, saboda an rawaito daga dan Umar ya ce: Manzon Allah - SAW - ya hau munbari sai yai kira da murya mai qarfi kuma ya ce: " Ya ku jama'ar da suka Musulunta da harshen su kuma imani bai shiga zuciyarsu ba kada ku cutar da Musulmai kuma kada ku aibatasu

kuma kada ku bibiyi al’aurarsu saboda duk wanda yabi al’aurar wani dan uwansa musulmi to Allah zai bibiyi al’aurarsa, kuma duk wanda Allah Ya bi al’aurarsa sai ya kunyata, ko da kuma yana cikin mutanensa ne, ya ce: Kuma Ibn Umar wata rana ya kalli dakin Allah ko zuwa Ka'aba sai ya ce: Mai yafiki girma da alfarma kuma mumini shi ne mafi girmanki alfarma a wajen Allah" Tirmizi ne ya rawaito shi (2032), da Ibn Hibban (5763). Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: Duk wanda yai imani da Allah da ranar lahira to ya fadi alkairi ko yayi shiru, kuma duk wanda yayi imani da Allah da ranar lahira to ta girmama makwabcinsa, kuma duk wanda yayi imani da Allah da ranar lahira to ta girmama to ya girmama bakonsa” Sahih Al-Bukhari: 6018. An karbo daga Abu Huraira daga manzon Allah - SAW - ya ce: "Shin kunsan wane ne tozartacce? Suka ce Tozartacce a cikin mu shi ne wanda bashi ko kwabo kuma bashi da kaya, sai ya ce: "Lallai tozartacce daga cikin al’umma ta wanda ya zo a ranar Al-qiyama da azumi da sallah da zakka kuma yazo ahalin ya zagi wancan yayiwa wancan qazafi kuma yaci kudin wancan sai a zaunar da shi sai a dauka daga kyawawan ayyukansa idan suka qare kafin abiya abunda yake kansa sai a debo zunubansu sai lafta masa sannan a jefa shi cikin Wuta" Muslim ne ya rawaito shi (2581), da kuma Tirmi zi (2418), da Ahmad (8029) kuma lafazin nasa ne. Manzon Allah ya ce: "Ya kasance akan hanya akwai wani reshe da yake cutar da mutane sai ya kawar da shi sai Allah Ya sa shi a aljanna" Bukhari ne ya rawaito shi (652) da ma'anarsa, da Muslim (1914) kwatankwacinsa, da Ibn Majah (3682), da Ahmad (10432) kuma Lafazin nasu ne, saboda kawar da cuta

akan hanya yana sa a shiga aljanna to yaya kuma wanda yake cutar da mutane kuma yake bata rayuwarsu?

**37. Musulunci ya zo da kiyaye hankula da haramta dukkan abunda zai bata shi kamar shan giya, kuma Musulunci ya daga darajar hankali kuma ya sanya shi doron dora nauyi, kuma ya 'yantashi daga dabaibayin taysuniyoyo da bautar gumaka kuma a Musulunci babu wasu boyayyun abubuwa ko hukunce hukunce da suka kebanci wasu mutane koma bayan wasu, kuma baki dayan hukunce-hukuncen sa da shari'unsa sunyi daidai da hankula ingantattu, kuma ita ce daidai da adalci da hikima**

Musulunci ya zo da kiyaye hankali kuma ya daga darajarsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿... إِنَّ ٱلسَّمۡعَ وَٱلۡبَصَرَ وَٱلۡفُؤَادَ كُلُّ أُوْلَٰٓئِكَ كَانَ عَنۡهُ مَسۡـُٔولٗا ٣٦﴾[الإسراء: 36]

{Lallai ji da gani da zuciya dukkan wadancan sun kasance ababan tambaya} [al-Isra'a: 36] to ya wajaba akan mutum ya kiyaye hankalinsa saboda haka Musulunci ya haramta giya da ababan maye, kuma an fadi haramcin giya a sakin layi na (34) da kuma ayoyin Al-qur'ani masu yawa wacce ta qare da fadinSa – Madaukaki -:

﴿...لَعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ٢٤٢﴾[البقرة: 242]

{Ko kwayi hankali} [al-Baqara: 242] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَآ إِلَّا لَعِبٞ وَلَهۡوٞۖ وَلَلدَّارُ ٱلۡأٓخِرَةُ خَيۡرٞ لِّلَّذِينَ يَتَّقُونَۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ٣٢﴾

[الأنعام: 32]

{Kuma rãyuwar dũniya ba ta zama ba, fãce wãsa da shagala, kuma lalle ne, Lãhira ce mafi alhẽri ga waɗanda suka yi taƙawa.

Shin, ba za ku yi hankali ba?} [al-An'am: 32], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿إِنَّآ أَنزَلۡنَٰهُ قُرۡءَٰنًا عَرَبِيّٗا لَّعَلَّكُمۡ تَعۡقِلُونَ ٢﴾[يوسف: 2]

{Lalle ne Mũ, Mun saukar da shi, yanã abin karantãwa na Lãrabci; tsammãninkũ, kunã hankalta} [Yusuf: 2] Kuma Allah - Madaukaki Yayi bayanin cewa shiriya da hikima ba'a anfanuwa da su sai ga ma'abota hankali su ne ma'abota hankali, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يُؤۡتِي ٱلۡحِكۡمَةَ مَن يَشَآءُۚ وَمَن يُؤۡتَ ٱلۡحِكۡمَةَ فَقَدۡ أُوتِيَ خَيۡرٗا كَثِيرٗاۗ وَمَا يَذَّكَّرُ إِلَّآ أُوْلُواْ ٱلۡأَلۡبَٰبِ ٢٦٩﴾[البقرة: 269]

{Yana bãyar da hikima (ga fahimtar gaskiyar abubuwa) ga wanda Yake so. Kuma wanda aka bai wa hikima to lalle ne an bã shi alhẽri mai yawa. Kuma bãbu mai tunãni fãce ma'abuta hankula} [al-Baqara:269] Saboda haka Musulunci ya sanya hankali ma'aunin dora doka Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-ya ce: "An dauke Al-qalami ga mutum Uku: Mai bacci har sai ya farka da yaro har sai ya balaga, da kuma mahaukaci har sai ya warke" Bukhari ne ya rawaito shi a matsayin Mua'allaqi da sigar yankewa kafin Hadisi na (5269) da makamancinsa kuma Abu Daud ya futar da shi a Mausuli (4402) kuma lafazin nasa ne, da Tirmizi (1423) da nasa'i a cikin (Al-sunan Alkubra) (7346), da Ahmad (956) da sabani kadan, da Ibn Majah (2042) a taqaice. Kuma ya 'yantasu daga sasarin tatsunuyoyi da gumaka, Allah - Madaukaki - Ya ce yana bada labarin halin wasu al’ummai wajen riqonsu da tastuniyoyi da kuma mayarwarsu da gaskioya wacce ta zo musu daga Allah:

﴿وَكَذَٰلِكَ مَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ فِي قَرۡيَةٖ مِّن نَّذِيرٍ إِلَّا قَالَ مُتۡرَفُوهَآ إِنَّا وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا عَلَىٰٓ أُمَّةٖ وَإِنَّا عَلَىٰٓ ءَاثَٰرِهِم مُّقۡتَدُونَ ٢٣﴾[الزخرف: 23]

{ kuma kamar haka, bamu aika wani mai gargaɗi ba a gabãninka, a cikin wata alƙarya, fãce mani'imtanta sun ce,Lalle mũ, mun sãmi ubanninmu a kan wani addini kuma lalle mũ, mãsu kõyi ne a kan gurãbunsu} [al-Zukhruf: 23] Kuma Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce game da Annabi Ibrahim - amincin Allah a gare shi- cewa ya ce da mutanensa:

﴿إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦ مَا هَٰذِهِ ٱلتَّمَاثِيلُ ٱلَّتِيٓ أَنتُمۡ لَهَا عَٰكِفُونَ ٥٢ قَالُواْ وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا لَهَا عَٰبِدِينَ ٥٣﴾[الأنبياء: 52-53]

{Wadan nan wadanne gumaka ne da kuke sunkuyawa" (52) Suka ce: "Mun sãmi Ubanninmu mãsu lazimta a kansu."(53)} [al-Anbiya: 52-53] Sai Musulunci ya zo kuma ya umarci mutane da barin bautar gumaka da barin tatsuniyoyi wadanda suka gada daga iyayensu da kakanni da bin hanyar Manzanni - amincin Allah a gare su- kuma babu wasu sirruka a Musulunci ko hukunce-hukunce da suka kebanci wasu mutane banda wasu, an tamabyi Ali Bn Abi Dalib -Allah Ya yarda da shi- kuma shi ne baffan manzon Allah - SAW - kuma Mijin diyarsa: ko Manzon Allah ya kebance ku da wani abu? sai ya ce: "Manzon Allah - SAW - bai kevance mu da komai ba da bai game mutane da shi ba baki daya sai abunda yakasance a cikin kuben takobina wannan, ya ce: Sai ya futo da wata takarda a rubuce a cikinta: Allah Ya tsinewa duk wanda yayi yanka ga wanin Allah kuma Allah Ya tsinewa marar kasa, kuma Allah Ya tsinewa wanda ya la'anci iyayensa, kuma Allah Ya tsinewa duk wanda bada mafaka ga ‘yan bidi'a" Sahih Muslim: 1978. Kuma baki dayan hukun-hukuncen Musulunci da shari'unsa sunyi daidai

da lafiyayyun hankula kuma sun daidai da abinda adalci ya qunsa da hikima.

**38. kuma Addinann bata idan mabiyansu basu gamsu da abunda yake cikinsu ba na kwangaba kwanbaya, da al’amuran da hankali ba zai dauka ba sai malama mabiya Addinin sai su rudi mabiyan da cewa ai Addini sama yake da hankali.kuma cewa hankali ai dole sai da shi wajen fahimtar Addini da kuma riqeshi wanda ko Musulunci ya sanya hankali wani haske ne da yake haskawa hankali hanya; saboda ma'abota Addinan karya sunason mutum ne ya bar hankalinsa ya bi su, kuma Musulunci yana son mutum ne da ya farkar da hankalinsa, don yasan haqiqanin al’amura kamar yadda yake**

kuma Addinann bata idan mabiyansu basu gamsu da abunda yake cikinsu ba na kwangaba kwanbaya, da al’amuran da hankali ba zai dauka ba sai malaman mabiya Addinin sai su rudi mabiyan da cewa ai Addini sama yake da hankali. kuma cewa hankali ai dole sai da shi wajen fahimtar Addini da kuma riqeshi wanda ko Musulunci ya sanya hankali wani haske ne da yake haskawa hankali hanya; saboda ma'abota Addinan karya sunason mutum ne ya bar hankalinsa ya bi su, kuma Musulunci yana son mutum ne da ya farkar da hankalinsa, don yasan haqiqanin al’amura kamar yadda yake:

﴿وَكَذَٰلِكَ أَوۡحَيۡنَآ إِلَيۡكَ رُوحٗا مِّنۡ أَمۡرِنَاۚ مَا كُنتَ تَدۡرِي مَا ٱلۡكِتَٰبُ وَلَا ٱلۡإِيمَٰنُ وَلَٰكِن جَعَلۡنَٰهُ نُورٗا نَّهۡدِي بِهِۦ مَن نَّشَآءُ مِنۡ عِبَادِنَاۚ وَإِنَّكَ لَتَهۡدِيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ ۝٥٢﴾[الشورى: 52]

{ kuma kamar wancan mun aika wani rũhi (rai mai haɗa jama'a) zuwa gare ka, daga gare Mu Ba ka kasance kã san abin da yake littãfi ba, kõ abin da Yake ĩmãni, kuma amma Mun sanya shi (rũhin, watau Alƙur'ãni) wani haske ne, Munã shiryar da wanda Muke so daga cikin bãyĩnMu game da shi. Kuma Lalle

kai, haƙĩƙa, kanã shiryarwa zuwa ga hanya, madaidaiciya} [al-Shura: 52] to wahayi Allah ya qunshi hujjoji da dalilai abunda zai shiryar da lafiayyayun hankula zuwa haqiqai wadan da kake son saninsu da Imani da su, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ قَدْ جَآءَكُم بُرْهَـٰنٌ مِّن رَّبِّكُمْ وَأَنزَلْنَآ إِلَيْكُمْ نُورًا مُّبِينًا ﴿١٧٤﴾﴾ [النساء: 174]

{Yã kũ mutãne! Haƙĩƙa wani dalĩli daga Ubangijinku yã je muku kuma Mun saukar da wani haske, bayyananne zuwa gare ku} [al-Nisa: 174] Allah - SWT - Yana son mutum ya rayu cikin hasken shiriya da kuma Ilimi da haqiqa, su kuwa shaidanu da dagutai suna son mutum ya wanzu cikin duhhan kafirci da jahilci da kuma bata, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿ٱللَّهُ وَلِيُّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ يُخْرِجُهُم مِّنَ ٱلظُّلُمَـٰتِ إِلَى ٱلنُّورِ ۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُوٓا۟ أَوْلِيَآؤُهُمُ ٱلطَّـٰغُوتُ يُخْرِجُونَهُم مِّنَ ٱلنُّورِ إِلَى ٱلظُّلُمَـٰتِ ۗ...﴿٢٥٧﴾﴾ [البقرة: 257]

{Allah Shine masoyin wadanda suka yi imani, Yana fitar da su daga duffai zuwa ga haske, kuma wadanda suka kafirta, masoyansu dagutu ne, suna fitar da su daga haske zuwa ga duffai...} [al-Baqara: 257].

**39. Musulunci yana girmama ingantaccen ilimi, kuma yana kwadaitarwa kan binciken ilimi wanda yake babu son rai a cikinsa, kuma yana kira zuwa nazari da tunani cikin kawunanmu da kuma halittu da suke kewaye da mu, da kuma sakamakon ilimi ingantacce don ilimi wadanda basa cin karo da Musulunci.**

Musulunci yana yana girmama ingantaccen ilimi, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿...يَرْفَعِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مِنكُمْ وَٱلَّذِينَ أُوتُوا۟ ٱلْعِلْمَ دَرَجَـٰتٍ ۚ وَٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرٌ ﴿١١﴾﴾ [المجادلة: 11]

{Allah Yana daga darajar wadanda sukai Imani daga cikin ku kuma wadanda aka bawa ilimi suna da darajjojo, kuma Allah Ya na baku labarin abunda kuke aikatawa} [al-mujadalah 11). Kuma Ya hada shaidar malamai da shaidarSa da kuma shaidar Mala'iku kan mafi girman abun shaidawa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلۡعِلۡمِ قَآئِمَۢا بِٱلۡقِسۡطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ ١٨﴾ [آل عمران: 18]

{ Allah Ya shaida cẽwa Lalle ne bãbu abin bautãwa fãce Shi kuma malãiku da ma'abũta ilmi sun shaida, yana tsaye da ãdalci, bãbu abin bautãwa face Shi, Mabuwãyi, Mai hikima} [Aal Imran: 18] Kuma wannan yana nuna matsayin ma'abota Ilimi a cikin musulunci da kuma abun da Alah ya umarci annabinsa Muhammad - SAW - da neman qari daga wani abu na ilaimi, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿... وَقُل رَّبِّ زِدۡنِي عِلۡمٗا ١١٤﴾[طه: 114]

{Kuma ka ce Ya Ubangiji Ka karar da ni ilimi} [Daha:114] Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Duk wanna ya kama wata turba yana neman ilimi a cikin ta to Allah Zai sawwake masa da ita hanyar zuwa aljanna" kuma lallai cewa mala'iku suna shinfida fukafukansu don yarda da mai neman Ilimi kuma lallai dalibin ilimi suna nema masa gafara duk wadanda suke cikin sama da kasa har kifaye a cikin ruwa, kuma lallai cewa falalar malami kan mai Ibada kamar falalar wata a kan sauran taurari, lallai malamai su ne magada Annabwa kuma lallai cewa Annabawa basu gadar da dinare ba ko dirhami kawai sun gadar da Ilimi ne to duk wanda yai riqo da shi to yayi riqo da rabo

mai yawa" Abu Daud ne ya futar da shi (3641), da Tirmizi (2682), da Ibn Maja (223) kuma lafazin nasa ne, da Ahmad (21715). Kuma Musulunci yana kwadaitarwa kan ilimi tsantsa wanda babu son rai a cikinsa kuma yana kira zuwa nazari da tunani a cikin kawunanmu da kuma cikin halittun da suke gefenmu, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿سَنُرِيهِمۡ ءَايَٰتِنَا فِي ٱلۡأٓفَاقِ وَفِيٓ أَنفُسِهِمۡ حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَهُمۡ أَنَّهُ ٱلۡحَقُّۗ أَوَلَمۡ يَكۡفِ بِرَبِّكَ أَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ شَهِيدٌ ٥٣﴾[فصلت: 53]

{Zã Mu nũna musu ãyõyinMu a cikin sãsanni da kuma cikin rãyukansu, har ya bayyana a gare su cẽwã lalle (Alƙur'ãni), shi ne gaskiya. Ashe, kuma Ubangijinka bai isa ba, ga cẽwa lalle Shĩ halartacce ne a kan kowane abu ne?} [Fussilat: 53], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ١٨٥﴾[الأعراف: 185]

{Shin, ba su yi dũbi ba a cikin mulkin sammai da ƙasa, da kuma abin da Allah Ya halitta daga kõme, kuma akwai tsammãni kasancewar ajalinsu, haƙĩƙa, ya kusanta? To, da wane lãbãri a bãyansa suke yin ĩmãni?} [al-A'araf: 185], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أَوَلَمۡ يَسِيرُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ فَيَنظُرُواْ كَيۡفَ كَانَ عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنۡهُمۡ قُوَّةٗ وَأَثَارُواْ ٱلۡأَرۡضَ وَعَمَرُوهَآ أَكۡثَرَ مِمَّا عَمَرُوهَا وَجَآءَتۡهُمۡ رُسُلُهُم بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٩﴾ [الروم: 9]

{Shin, kuma ba su yi tafiya ba, a cikin ƙasã dõmin su gani yadda aƙibar waɗanda ke a gabãninsu ta kasance? Sun kasance

mafiya ƙarfi daga gare su kuma suka nõmi ƙasa suka rãya ta fiye da yadda suka raya ta, kuma manzanninsu suka je musu da hujjoji bayyanannu. Sabo da haka Allah ba Ya yiwuwa Ya zãlunce su, amma kansu suka kasance sunã zãlunta} [Rum: 9] Kuma sakamakon ilimi ingantaccen ilimi baya cin karo da Musulunci kuma zamu fadi wani misali kwaya daya wanda Al-qur'ani ya fadi bayanin cikakke dangane da sha'aninsa tun kafin sama da shekara dubu daya da dari kuma ilimin zamani a qarshe ya sanar da shi; sakamakon daidaituwar abunda yake cikin Al-qur'ani mai girma kuma shi ne halittar dan tayi a cikin mahaifiyarsa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ مِن سُلَٰلَةٖ مِّن طِينٖ ١٢ ثُمَّ جَعَلۡنَٰهُ نُطۡفَةٗ فِي قَرَارٖ مَّكِينٖ ١٣ ثُمَّ خَلَقۡنَا ٱلنُّطۡفَةَ عَلَقَةٗ فَخَلَقۡنَا ٱلۡعَلَقَةَ مُضۡغَةٗ فَخَلَقۡنَا ٱلۡمُضۡغَةَ عِظَٰمٗا فَكَسَوۡنَا ٱلۡعِظَٰمَ لَحۡمٗا ثُمَّ أَنشَأۡنَٰهُ خَلۡقًا ءَاخَرَۚ فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ أَحۡسَنُ ٱلۡخَٰلِقِينَ ١٤﴾[المؤمنون: 12-14]

{Kuma lalle ne, haƙĩƙa, Mun halitta mutum daga wani tsantsa daga lãka.(12) Sa'an nan kuma Muka sanya shi, ɗigon maniyyi a cikin matabbata natsattsiya.(13) Sa'an nan kuma Muka halitta shi gudan jini, sa'an nan Muka halitta gudan jinin tsõka, sa'an nan Muka halitta tsõkar ta zama ƙasũsuwa, sa'an nan Muka tufãtar da ƙasũsuwan da wani nãma sa'an nan kuma Muka ƙãga shi wata halitta dabam. Sabõda haka albarkun Allah sun bayyana, Shi ne Mafi kyaun mãsu halittawa.(14)} [al-Mu'aminun: 12-14].

**40. kuma Allah baya karbar aiki ko ya bada lada akansa a lahira sai daga wadanda sukai imani da Allah kuma suka gasgata Manzanninsa -Amincin Allah a gare su- kuma Allah baYa karbar ibadu sai da abunda Ya shar'anta, saboda mai zai sa mutum ya kafircewa Allah kuma ya kaunaci ladansa? kuma Allah baYa karbar imani wani mutum sai idan yayi imani da Annabawa -Amincin Allah a gare su baki daya- Kuma yayi imani da saqon Annabi Muhammad – SAW -.**

Kuma Allah baYa karbar aikin kuma baya bada lada akansa a lahira sai daga wanda yayi imani da Allah, kuma ya bishi kuma ya gasgata ManzonSa - amincin Allah a gare shi-, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿مَّن كَانَ يُرِيدُ ٱلۡعَاجِلَةَ عَجَّلۡنَا لَهُۥ فِيهَا مَا نَشَآءُ لِمَن نُّرِيدُ ثُمَّ جَعَلۡنَا لَهُۥ جَهَنَّمَ يَصۡلَىٰهَا مَذۡمُومٗا مَّدۡحُورٗا ١٨ وَمَنۡ أَرَادَ ٱلۡأٓخِرَةَ وَسَعَىٰ لَهَا سَعۡيَهَا وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَأُوْلَٰٓئِكَ كَانَ سَعۡيُهُم مَّشۡكُورٗا ١٩﴾ [الإسراء: 18-19]

{Wanda ya kasance yanã nufin mai gaggãwa, sai Mu gaggauta masa a cikinta, abin da Muke so ga wanda Muke nufi, sa'an nan kuma Mu sanya masa Jahannama, ya ƙõnu da ita, yanã abin zargi kuma abin tunkuɗewa.(18) Kuma wanda ya nufi Lãhira, kuma ya yi aiki sabõda ita irin aikinta alhãli kuwa yanã mũmĩni, to, waɗannan aikinsu ya kasance gõdadde.(19)} [al-Israa: 18-19] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿فَمَن يَعۡمَلۡ مِنَ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَا كُفۡرَانَ لِسَعۡيِهِۦ وَإِنَّا لَهُۥ كَٰتِبُونَ ٩٤﴾[الأنبياء: 94]

{Dõmin wanda ya aikata daga ayyukan kwarai alhãli kuwa yanã mai ĩmãni, to, bãbu musu ga aikinsa, kuma Mu Mãsu rubũtãwa gare shi ne} [al-Anbiya: 94].

﴿... فَمَن كَانَ يَرۡجُواْ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلۡيَعۡمَلۡ عَمَلٗا صَٰلِحٗا وَلَا يُشۡرِكۡ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدَۢا ١١٠﴾ [الكهف: 110]

{Kuma Allah baYa karbar ibadu sai wadanda Ya shar'anta, Allah - Madaukaki - Ya ce: Saboda haka wanda ya kasance yana fatan haduwa da Ubangijinsa,to, sai ya yi aiki na kwarai. Kuma kada ya hada kowa ga bauta wa Ubangijinsa} [al-Kahf: 110]. Saboda haka Yayi bayani cewa aiki baya kasancewa nagartacce sai in ya kasance yana daga cikin abunda Allah Ya shar'anta kuma ya kasance ya tsakake shi saboda Allah a cikin aikinsa, kuma yana mai imani da Allah yana mai kuma yana mai gasgatawa da Annabawansa da Manzanninsa - amincin Allah a gare su- amman wanda ya kasance aikinsa wanin hakan ne to haqiqa Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَقَدِمۡنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُواْ مِنۡ عَمَلٖ فَجَعَلۡنَٰهُ هَبَآءٗ مَّنثُورًا ٢٣﴾[الفرقان: 23]

{Kuma Muka gabãta zuwa ga abin da suka aikata daga aiki, sai Muka sanya shi ƙũra wãtsattsiya} [al-furqan: 23], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وُجُوهٞ يَوۡمَئِذٍ خَٰشِعَةٌ ٢ عَامِلَةٞ نَّاصِبَةٞ ٣ تَصۡلَىٰ نَارًا حَامِيَةٗ ٤﴾[الغاشية: 2-4]

{Wasu huskõki a rãnar nan ƙasƙantattu ne.(2) Mai aiki tana shan Wuya (3) Zata shiga Wiuta Mai kuna (4)} [al-gashiya: 2-4]. To wadan nan fuskoki masu shan wahalar aiki sai dai su sun kasance suna aiki ne ba tare shiriya daga Allah ba, Allah sai Ya sanya makomarta zuwa wuta; saboda batai aiki da da abunda Allah Ya shar'anta ba a'a tayi aiki ne da ibadu batattu kuma ta bi shugabannin bata wadan da suka qirqirar musu Addinan bata saboda aiki nagari karbabbe a wajen Allah shi wanda yayi daidai da abunda Manzon Allah - SAW - ya zo da shi to ta yaya

mutum zai kafirta da Allah kuma ya zo kuma ya saka masa?? Kuma Allah baYa karbar imanin wani daga cikin mutane sai idan yai imani da Annabawa - amincin Allah a gare su- baki dayan su, kuma yayi imani da saqon Manzon Allah - SAW - ya gabata cewa an fadi wasu dalilai akan hakan a sakin layi na (20) Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيۡهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيۡنَ أَحَدٖ مِّن رُّسُلِهِۦۚ وَقَالُواْ سَمِعۡنَا وَأَطَعۡنَاۖ غُفۡرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيۡكَ ٱلۡمَصِيرُ ٢٨٥﴾[البقرة: 285]

{ {Manzon Allah yã yi ĩmãni da abin da aka saukar zuwa gare shi daga Ubangijinsa, da mũminai. Kõwanensu yã yi ĩmãni da Allah, da mala'ikunSa, da littattafanSa, da manzanninSa. Bã mu rarrabẽwa a tsakãnin daya daga manzanninSa. Kuma (mũminai) suka ce Mun ji kuma mun yi dã'a; (Muna nẽman) gãfararKa, yã Ubangijinmu, kuma zuwa a gare Ka makõma take} [al-Baqara: 285], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِي نَزَّلَ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِن قَبۡلُۚ وَمَن يَكۡفُرۡ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ فَقَدۡ ضَلَّ ضَلَٰلَۢا بَعِيدًا ١٣٦﴾[النساء: 136]

{Yã kũ waɗanda suka yi ĩmãni! Ku yi ĩmãni da Allah da Manzonsa, da Littãfin da Ya sassaukar ga ManzonSa da Littãfin nan wanda Ya saukar daga gabãni. To, wanda ya kãfirta da Allah da malã'ikunSa, da LittattafanSa, da ManzanninSa, da Rãnar Lãhira, to, lalle ne yã ɓace, ɓata mai nĩsa} [al-Nisa'a: 136], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَإِذۡ أَخَذَ ٱللَّهُ مِيثَٰقَ ٱلنَّبِيِّـۧنَ لَمَآ ءَاتَيۡتُكُم مِّن كِتَٰبٖ وَحِكۡمَةٖ ثُمَّ جَآءَكُمۡ رَسُولٞ مُّصَدِّقٞ لِّمَا مَعَكُمۡ لَتُؤۡمِنُنَّ بِهِۦ وَلَتَنصُرُنَّهُۥۚ قَالَ ءَأَقۡرَرۡتُمۡ وَأَخَذۡتُمۡ عَلَىٰ ذَٰلِكُمۡ إِصۡرِيۖ قَالُوٓاْ أَقۡرَرۡنَاۚ قَالَ فَٱشۡهَدُواْ وَأَنَا۠ مَعَكُم مِّنَ ٱلشَّٰهِدِينَ٨١﴾[آل عمران: 81]

{Kuma a lõkacin da Allah Ya riƙi alkawarin Annabãwa: "Lalle ne ban bã ku wani abu ba daga Littãfi da hikima, sa'an nan kuma wani manzo ya je muku, mai gaskatãwa ga abin da yake tãre da ku; lalle ne zã ku gaskata Shi, kuma lalle ne zã ku taimake shi." Ya ce: "Shin, kun tabbatar kuma kun riƙi alkawarĩNa a kan wannan a gare ku?" suka ce: "Mun tabbatar." Ya ce: "To, ku yi shaida, kuma Nĩ a tãre da ku Inã daga mãsu shaida} [Aal Imran: 81].

**41.Lallai manufar sakonnin Allah baki dayansu shi ne: cewa lallai Addinin gaskiya ya daukaka dan Adam, saboda ya kasance tsantsar bawan Allah Ubangijin talikai, kuma ya 'yanta shi daga bautar mutane ko kuma wani abun duniya ko kuma tatsunuyoyi, saboda Musulunci -kamar yadda kake ganinsa- baya tsarkake mutane ya dagasu sama da matsayinsu, kuma baya sanya su Alloli ababan bauta**

Lallai manufar baki dayan sakonnin Allah shi ne: cewa addinin gaskiya ya zamo ya daukaka dan Adam sama da komai sai bawa ya kasance mai tsantsanr tsarkake ibada ga Allah Ubangijin talikai kuma Musulunci ya 'yanta mutum daga bautar kudi ko tatsuniyoyi Manzon Allah - SAW - ya ce" "Bawan kwabo da dari ya wahala da bawan riga da sutura idan aka bashi sai ya yarda idan kuma ba'a bashi ba sai yaqi yarda" Sahih Al-Bukhari: 6435. Saboda mutumin da yake daidai ba zai zamanto ya risina ba sai ga Allah babu wata dukiya da zata bautar da shi ko wani

girma ko matsayi ko kabila kuma a cikin wannan kissar akwai abunda zai budewa mai karatu abunda mutane suke kanasa kafin zuwan Manzanni kuma yaya suka zama a bayan sa" yayin da musulman farko suka yi hijira zuwa Habasha, sai sarkin Habasha na wannan lokacin -Najjashi- ya ce da su: "Wane Addini ne wanda ya raba ku da mutanenku a cikinsa, kuma baku shiga Addini na ba ko Addinin wani daga cikin wadan nan al'ummai? Sai Ja'afar Bn Abi Dalib ya ce: Ya kai wannan sarki mun samu kanmu a Jahiliyya muna bautawa gumaka, kuma muna cin mushe, kuma muna aikata alfasha, kuma muna yanke zumunci, Kuma muna munana makwabtaka, mai karfi a cikin mu yana cinye kayan mai rauni, to dukkanmu muna kan hakan sai Allah Ya aiko mana wani Manzo munsan nasabarsa, da gaskiyarsa da amanarsa, da kamewarsa, sai ya kirawo mu zuwa bautar Allah don mu kadaita shi kuma mu bauta masa kuma mu yakice abunda muke bautawa mu da iyayenmu na koma bayan Allah na duwatsu da gumaka kuma ya umarce nu da mu bautawa Allah Shi kadai kada kuma muyi masa shirka da komai kuma ya umarce mu sallah da zakka da Azumi ya ce: sai al'amuran Musulunci suka yawaita a gareshi sai muka gasgata shi kuma mukai imani da shi kuma muka bishi akan abunda ya zo da shi sai muka bautawa Allah shi kadai bama shirka da shi da komai kuma ya haramta mana abunda ya hamta mana kuma ya halatta mana abunda ya halatta mana". Ahmad ne ya rawaito shi (1740) da sabani kadan, da kuma Abu Nu'aim a cikin ((Hilyat Al-auliyaa)) (1/115) a takaice. Saboda Musulunci kamar yadda kake gani baya tsarkake wasu mutane kuma ya daga darajarsu sama da matsayin su kuma ya sanya su zu zaman to Alloli ko abun bauta, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce Ka ce:

﴿قُلۡ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ كَلِمَةٖ سَوَآءِۭ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمۡ أَلَّا نَعۡبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشۡرِكَ بِهِۦ شَيۡـٔٗا وَلَا يَتَّخِذَ بَعۡضُنَا بَعۡضًا أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِۚ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُولُواْ ٱشۡهَدُواْ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ ٦٤﴾[آل عمران: 64]

{{Yã ku Mutãnen Littãfi! Ku tafo zuwa ga kalma mai daidaitãwa a tsakã ninmu da ku; kada mu bauta wa kõwa fã ce Allah. Kuma kada mu haɗa kõme da Shi, kuma kada sãshenmu ya riƙi sãshe Ubangiji, baicin Allah." To, idan sun jũya bã ya sai ku ce:ku yi shaida cẽwa, lalle ne mu masu sallamã wa ne} [Aal Imran: 64], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَلَا يَأۡمُرَكُمۡ أَن تَتَّخِذُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ أَرۡبَابًاۗ أَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡكُفۡرِ بَعۡدَ إِذۡ أَنتُم مُّسۡلِمُونَ ٨٠﴾ [آل عمران: 80]

{Kuma ba ya umurnin ku da ku riƙi malã'iku da annabãwa Iyãyengiji. Shin, zai umurce ku da kãfirci ne a bãyan kun riga kun zama mãsu sallamãwa (Musulmi)?} [Aal Imran: 80]. Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Kada ku wuce gona da iri wajen yabona yadda Nasara suka maida Dan Maryam, ni kawai bawa ne, to kuce bawan Allah ne kuma ManzonSa" Sahih Al-Bukhari: 3445.

**42.Allah Ya shar'anta tuba a Musulunci wanda shi ne maida komai da komai din dan Adam zuwa ga Ubangijinsa, da barin zunubai, kuma Musulunci yana rushe abunda yake kafinsa na zunubai, kuma tuba yana wanke abunda ya gabace shi na zunubai, saboda haka babu wata buqata mutum ace sai ya bayyana laifukansa ga mutane**

Alllah Ya shar'anta Tuba a cikin Musulunci kuma Shine mutum ya maida komai nasa zuwa ga Ubangijinsa, kuma ya bar zunubai, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿...وَتُوبُوٓاْ إِلَى ٱللَّهِ جَمِيعًا أَيُّهَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ لَعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٣١﴾[النور: 31]

{Kuma ku tuba zuwa ga Allah ya ku Muminai baki xayanku ko kwa rabauta} [al-Nur: 31], Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ هُوَ يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَأۡخُذُ ٱلصَّدَقَٰتِ وَأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٤﴾[التوبة: 104]

{Shin, ba su sani ba cẽwa lallai Allah, ne Yake karɓar tũbã daga bãyinSa, kuma Yanã karɓar sadakõkinsu, kuma lalle Allah ne Mai karɓar tũba, Mai jin ƙai?} [al-Tauba: 104] Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَهُوَ ٱلَّذِي يَقۡبَلُ ٱلتَّوۡبَةَ عَنۡ عِبَادِهِۦ وَيَعۡفُواْ عَنِ ٱلسَّيِّـَٔاتِ وَيَعۡلَمُ مَا تَفۡعَلُونَ ٢٥﴾[الشورى: 25]

{Kuma Shi ne ke karɓar tũba daga bãyinSa, kuma Yanã Yafe ƙananan laifuffuka, alhãli kuwa Yanã sanin abin da kuke aikatãwa} [al-Shura: 25] Annabi - tsira da amincin Allah su qara tabbata a gare shi - ya ce: "Lallai Allah Yafi tsananinin farin ciki da tuban bawanSa mumini daga mutumin da yake cikin wata kasa ya samu kansa cikin wata qasa sai guguwa ta taso tare da shi abun hawansa akanta abincinsa da abun shansa sai ya yi bacci sannan ya farka kuma haqiqa ta tafi ya neme ta har sai da qishirwa ta kama shi sannan ya ce: bari in koma wajena wanda nake a cikinsa sai inyi bacci har mutuwa ta same ni sai ya sanya kansa kan dantsensa don ya mutu sai kawai ya farka sai ga dabbarsa a gabansa kuma akanta guzurinsa da abincinsa da abun shansa to Allah Ya fi shi farin ciki da tuban bawansa mumini daga mai wannan dabba da guzirin nasa" Sahih Muslim: 2744. Kuma Musulunci yana rushe dukan abunda ya

gabace shi na kuma tuba yana wanke abunda ya gabace shi na zunubai, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قُل لِّلَّذِينَ كَفَرُوٓاْ إِن يَنتَهُواْ يُغۡفَرۡ لَهُم مَّا قَدۡ سَلَفَ وَإِن يَعُودُواْ فَقَدۡ مَضَتۡ سُنَّتُ ٱلۡأَوَّلِينَ ٣٨﴾[الأنفال: 38]

{Ka ce wa waɗanda suka kãfirta, idan sun hanu, zã a gãfarta musu abin da ya riga ya shige, kuma idan sun kõma, to, hanyar kãfiran farko, haƙĩƙa, ta shũɗe} [al-Anfal: 38] Kuma Allah Ya kirawo Nasara da su tuba sai Allah - sha'aninSa ya daukaka - Ya ce:

﴿أَفَلَا يَتُوبُونَ إِلَى ٱللَّهِ وَيَسۡتَغۡفِرُونَهُۥۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧٤﴾[المائدة: 74]

{shin fã, bã su tuba zuwa ga Allah, kuma su neme Shi gãfara, alhãli kuwa Allah Mai gãfara ne, Mai jin ƙai?} [al-Ma'ida: 74] Kuma ya kwadaitar da baki dayan masu sabo da masu zunubai da su tuba sai Allah - Madaukaki - Ya ce::

﴿۞قُلۡ يَٰعِبَادِيَ ٱلَّذِينَ أَسۡرَفُواْ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِمۡ لَا تَقۡنَطُواْ مِن رَّحۡمَةِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ يَغۡفِرُ ٱلذُّنُوبَ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٥٣﴾[الزمر: 53]

{ Ka ce: (Allah Ya ce) Yã bãyĩNa waɗanda suka yi barna a kan rãyukansu! Kada ku yanke ƙauna daga rahamar Allah. Lalle Allah na gãfarta zunubai gabã ɗaya. Lalle Shĩ, Shĩ ne Mai gãfara, Mai jin ƙai} [al-Zumar: 53] Kuma yayin da Amr Bn Al-as ya Musulunta sai yaji tsoron ko ba za'a gafarta masa zunubansa ba wadanda ya aikata kafin Musulunci sai Amr yana mai rawaito wannan lokacin ya ce: "Yayin da Allah ya jefa Musulunci a cikin zuciyata ya ce nazo wajen Manzon Allah - SAW - don inyi masa mubaya'a sai ya shinfida hanannayensa gare ni sai na ce: Ba zan yi maka mubaya'a ba ya manzon Allah har sai ka gafarta mun abunda ya gabata daga zunubai na ya ce: sai Manzon Allah - SAW - ya ce ya kai Amru baka san cewa

hijira tna shafe abunda ya gabaceta ba na zunubai ya kai Amru baka sani ba cewa Musulunci ya shafe abunda ya gabace na zunubai". Muslim ne ya rawaito shi (121) mai tasawo kamarsa, da kuma Ahmad (17827) kuma wannan lafazin ma nasa ne.

**43.Saboda a cikin Musulunci dangantaka tsakanin mutum da Allah kai tsaye ta ke, saboda haka baka buqatar wani mutum da zai kasance tsani tsakaninka da Allah, saboda Musulunci ya hana mu sanya mutane su zamanto Alloli ko kuma suna tarayya da Allah cikin AllantakarSa da BautarSa**

A cikin Musulunci babu wata buqatar yin furuci da laifukan mutum a gaban wani Mutum saboda a cikin Musulunci Alaqa a tsakanin Mutum da Allah kai tsaye saboda ba'a buqatar zuwa wani daya, saboda ya kasance a tsakaninka da tsakanin Allah kamar yadda ya wuce a sakin layi mai lamba (36) cewa Allah – Madaukaki - ya kira baki dayan mutane zuwa tuba da kuma komawa zuwa gare shi to shi kamar haka ya hana mutane kan su riqi Annabawa ko Mala'iku tsani tsakaninsa da tsakanin bayinSa, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَلَا يَأۡمُرَكُمۡ أَن تَتَّخِذُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ وَٱلنَّبِيِّـۧنَ أَرۡبَابًاۗ أَيَأۡمُرُكُم بِٱلۡكُفۡرِ بَعۡدَ إِذۡ أَنتُم مُّسۡلِمُونَ ٨٠﴾ [آل عمران: 80]

{Kuma ba ya umurnin ku da ku riƙi malã'iku da annabãwa Iyãyengiji. Shin, zai umurce ku da kãfirci ne a bãyan kun riga kun zama mãsu sallamãwa (Musulmi)?} [Aal Imran: 80] Saboda Musulunci -kamar yadda kake gani- ya na hana mu sanya mutum a matsayin Ubangiji ko yai tarayya da Allah a cikin Allantaka ko kuma bauta kuma Allah Ya ce game da Nasara:

﴿ٱتَّخَذُوٓاْ أَحۡبَارَهُمۡ وَرُهۡبَٰنَهُمۡ أَرۡبَابًا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ مَرۡيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُوٓاْ إِلَٰهًا وَٰحِدًاۖ لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ سُبۡحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٣١﴾[التوبة: 31]

{Sun riƙi mãlamansu (Yahũdu) da ruhubãnãwansu (Nasãra) Ubannangiji, baicin Allah, kuma sun riƙi Masĩhu ɗan Maryama (haka). Kuma ba a umurce su ba fãce da su bautã wa Ubangiji Guda. Bãbu abin bautãwa fãce Shi. TsarkinSa ya tabbata daga barin abin da suke yin shirki da shi} [al-Taubah: 31] Kuma Allah Ya musantawa kafiran da suka riqi wasu tsanuka tsakaninsu da Shi, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿أَلَا لِلَّهِ ٱلدِّينُ ٱلۡخَالِصُۚ وَٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ مِن دُونِهِۦٓ أَوۡلِيَآءَ مَا نَعۡبُدُهُمۡ إِلَّا لِيُقَرِّبُونَآ إِلَى ٱللَّهِ زُلۡفَىٰٓ إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ بَيۡنَهُمۡ فِي مَا هُمۡ فِيهِ يَخۡتَلِفُونَۗ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهۡدِي مَنۡ هُوَ كَٰذِبٞ كَفَّارٞ ٣﴾[الزمر: 3]

{To, addini tsarkakakke na Allah ne, kuma waɗanda suka riƙi waɗansu majibinta, bã Shi ba, (sunã cẽwa) "Ba mu bauta musu ba fãce dõmin su kusantar da mu zuwa ga Allah, kusantar daraja." Lalle Allah nã yin hukunci a tsakãninsu ga abin da suka zama sunã sãɓãwa a cikinsa. Lalle Allah ba Ya shiryar da wanda yake mai ƙarya, mai kãfirci} [al-Zumar: 3] Kuma Allah Yayi bayanin cewa masu bautar gumaka -mutanen Jahiliyya- sun kasance suna riqi wasu tsanuka tsakaninsu da Allah cewa su ne masu kusanta su zuwa ga Allah. Kuma idan Allah Ya hana mutane su riqi Annabawa ko Mal'iku wasu tsani tsakaninSa da bayainSa; to wasun su sun fi dacewa da a bari kuma ta yaya Annabawa da manzanni – amincin Allah a gare su- suna gaggawa a cikin kusanci zuwa ga Allah, Allah - Madaukaki - Ya ce Yana mai bada labarin halin annabawa da Manzanni - amincin Allah a gare su- lalle ne su,

﴿... إِنَّهُمۡ كَانُواْ يُسَٰرِعُونَ فِي ٱلۡخَيۡرَٰتِ وَيَدۡعُونَنَا رَغَبٗا وَرَهَبٗاۖ وَكَانُواْ لَنَا خَٰشِعِينَ ٩٠﴾
[الأنبياء: 90]

{... sun kasance suna gudun tsere zuwa ga ayyukan alheri, Kuma suna kiranmu a kan kwadayi da fargaba Kuma sun kasance masu saunar (aikata sabo) gare Mu. Al-anbiya'a: 90 Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿أُولَٰئِكَ الَّذِينَ يَدْعُونَ يَبْتَغُونَ إِلَىٰ رَبِّهِمُ الْوَسِيلَةَ أَيُّهُمْ أَقْرَبُ وَيَرْجُونَ رَحْمَتَهُ وَيَخَافُونَ عَذَابَهُ...﴾ [الإسراء: 57]

{Waɗancan, waɗanda suke kiran, sunã nẽman tsãni zuwa ga Ubangijinsu. Waɗanne ne suke mafĩfĩta a kusanta? Kuma sunã fãtan sãmun rahamarSa, kuma sunã tsõron azãbarSa. Lalle ne azãbar Ubangijinka ta kasance abar tsõro ce} [al-Isra'a: 57], ai lallai cewa wadanda suke bautar wanin Allah -na daga annabawa da salihai- su suna neman kusantar Allah kuma suna neman rahamarSa kuma suna tsoron azabarSa; to ta yaya yaya za'a roqi wanin Allah?

**44.A karshen wannan littafin muna tunsarwa cewa mutane duk da sabanin zamaninsu da kabilunsu, da garuruwan su kai baki dayan duniyar mutane sun saba a wajen tunanisu da manufofin su, sun yi hannun riga wajen garuruwansu da ayyukan su, saboda haka suna da buqatar wani mai shiryarwa da zai dorasu kan turba, da wani tasri da hade kansu, da wani jagora da zai kare su, kuma Manzanni -Amincin Allah a gare su- sun jibinci hakan da wahayi daga Allah - Madaukaki - suna shiryar da mutane zuwa hanyar alkairi da shiriya, kuma ya hada su akan shari'ar Allah kuma suna hukunci da gaskiya a tsakaninsu, saboda al'amuransu su tafi daidai dai dai da yadda wadan nan suka amsawa Manzannin, da kuma kusancinsu da wadan nan lokutan na Saqonnin Allah, kuma Allah Ya cika saqonin Manzancin da Manzo Annabi Muhammad - SAW -**

**kuma ya hukunta mata wanzuwa, kuma ya sanyata shiriya ga mutane da kuma rahama da haske da shiriyarwa zuwa tafarki mai isarwa zuwa ga Allah – SWT -**

A qarshen wannan littafin muke tunasar da mutane duk da sabanin zamanunsu da yarukansu, da garuruwansu, kai baki dayan ma mutanen duniya sun saba a tunaninsu da manufofin su a cikin garuruwansu da ayyukansu saboda yana bukata zuwa wanda zai shige masa gaba da zai sa shi a hanya da kuma tsari da zai hade su da kuma jagora da zai kare su, kuma Mazanni masu girma - amincin Allah a gare su- sun dau wannan nauyin da wahayi daga Allah suna shiryar da mutane suwa kan tafarkin alkairi da kuma shiriya kuma su tara su akan shari'ar Allah kuma suyi musu hukunci a tsakaninsu da ita saboda abubuwan su su daidaita, gwargwadon yadda suka amsawa wadan nan Manzanni da kuma kusancin lokacin su da saqonnin Allah kuma yayin da bata ya yawaita, kuma jahilci ya game ko ina, kuma akai bautar gunki, saboda haka sai Allah Ya aiko Annabi Muhammad - SAW - da shiriya da kuma Addini na gaskiya don ya futar da mutane daga duhun kafirci da jahilci da bautar gumaka zuwa imani da shiriya.

**45.Saboda haka nake roqonka ya kai dan Adam ka tsaya ga Allah tsayuwa ta gaskiya kana mai tsiraita kanka daga kwaikwayo da al'ada, kuma kasani cewa kai bayan mutuwarka zaka koma ne zuwa ga Ubangijinka, kuma ka kalli kanka, da kuma wasu sassa da suke kewaye da kai, ka Musulunta zaka rabauta a duniyarka da lahirar ka, idan kuma kana son shiga Musulunci babu abinda zaka yi sai kawai ka shaida cewa Babu abun bauta da gaskiya sai Allah, kuma cewa Annabi Muhammad Manzon Allah ne, kuma kayi watsi da duk abinda ake bautawa**

**koma bayan Allah, kuma kayi imani cewa Allah Zai tashi wadanda suke cikin kabari kuma cewa hisabi da sakamako gaskiya ne, to idan ka shaida da wannan shaidawar to haqiqa ka zama Musulmi, saboda haka bayan haka zaka bautawa Allah da abinda Ya shar'anta na Sallah da Zakka da Azumi, da kuma Hajjatar dakin Allah idan ka samu iko yin hakan,**

To ina kira gareka ya kai mutum lallai ka tsaya ga Allah kana mai gaskiya kuma ka rabu duk wani taqalidi da al'ada kamar yadda Allah - Madaukaki - Ya fada:

﴿۞قُلْ إِنَّمَآ أَعِظُكُم بِوَٰحِدَةٍ ۖ أَن تَقُومُوا۟ لِلَّهِ مَثْنَىٰ وَفُرَٰدَىٰ ثُمَّ تَتَفَكَّرُوا۟ ۚ مَا بِصَاحِبِكُم مِّن جِنَّةٍ ۚ إِنْ هُوَ إِلَّا نَذِيرٌ لَّكُم بَيْنَ يَدَىْ عَذَابٍ شَدِيدٍ ﴿٤٦﴾﴾ [سبأ: 46]

{Kace: Ina yi muku wa'azi ne kawai da kalma guda! watau ku tsayu dõmin Allah, bibbiyu da ɗaiɗai, sa'an nan ku yi tunãni, bãbu wata hauka ga ma'abũcinku. Shĩ bai zama ba fãce mai gargaɗi ne a gare ku a gaba ga wata azãba mai tsanani} [Saba'i: 46]. Kuma kana sani cewa kai bayan mutuwarka zaka koma ga Ubangijinka, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿وَأَن لَّيْسَ لِلْإِنسَٰنِ إِلَّا مَا سَعَىٰ ﴿٣٩﴾ وَأَنَّ سَعْيَهُۥ سَوْفَ يُرَىٰ ﴿٤٠﴾ ثُمَّ يُجْزَىٰهُ ٱلْجَزَآءَ ٱلْأَوْفَىٰ ﴿٤١﴾ وَأَنَّ إِلَىٰ رَبِّكَ ٱلْمُنتَهَىٰ ﴿٤٢﴾﴾ [النجم: 39-42]

{Kuma mutum bã shi da kõme fãce abin da ya aikata.(39) Kuma llai zaiga Ayyukansa(40) Sannan sai a saka masa da cikakken Sakamako (41) Kuma lallai zuwa ga Ubangijinka Matuqa ta ke (42)} [al-Najm: 39-42], kuma lallai cewa ka kalli kanka da kuma sassa da suke kewaye da kai, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿أَوَلَمۡ يَنظُرُواْ فِي مَلَكُوتِ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا خَلَقَ ٱللَّهُ مِن شَيۡءٖ وَأَنۡ عَسَىٰٓ أَن يَكُونَ قَدِ ٱقۡتَرَبَ أَجَلُهُمۡۖ فَبِأَيِّ حَدِيثِۭ بَعۡدَهُۥ يُؤۡمِنُونَ ١٨٥﴾[الأعراف: 185]

{Shin, ba su yi dũbi ba a cikin mulkin sammai da ƙasa, da kuma abin da Allah Ya halitta daga kõme, kuma akwai tsammãni kasancewar ajalinsu, haƙĩƙa, ya kusanta? To, da wane lãbãri a bãyansa suke yin ĩmãni?} [al-A'araf: 185] to ka musulunta sai ka rabauta a duniyarka da lahirarka, kuma idan kana son shiga Musulunci babau wani da zakayi sai ka shaida cewa babu wani Ubangiji da ya cancanci a bauta maSa sai Allah kuma lallai cewa Muhammagu Manzon Allah ne, Kuma yayin da Manzo - SAW - ya tura Mu'az zuwa Yeman ya na mai kira zuwa Musulunci sai ya ce da shi: "Lallai kai zaka je wajen wasu mutane daga cikin Ahlul kitab ka kirasu zuwa shaidawa cewa babu wani Ubangiji da ya cancanci a bautawa sai Allah kuma cewa ni manzon Allah ne, to idan suka bi ka akan hakan to ka sanar da su cewa Allah Ya farlanta musu salloli biyar a cikin kowace rana da dare, to idan suka bika cikin hakan to ka sanar da su cewa Allah Ya farlanta musu sadaqa da za'a karbo daga mawadatansu sannan a mayar ga talakawansu to idan suka bika akan haka to na haneka da ka kiyayi mafi darajar dukoiyoyinsu" Sahih Muslim: 19. Kuma ka rabu da duk abinda ake bautawa koma bayan Allah shi ne Addinin Annabi Ibrahim - amincin Allah a hare shi-, Allah - Madaukaki - Ya ce:

﴿قَدۡ كَانَتۡ لَكُمۡ أُسۡوَةٌ حَسَنَةٞ فِيٓ إِبۡرَٰهِيمَ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ إِذۡ قَالُواْ لِقَوۡمِهِمۡ إِنَّا بُرَءَٰٓؤُاْ مِنكُمۡ وَمِمَّا تَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ كَفَرۡنَا بِكُمۡ وَبَدَا بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمُ ٱلۡعَدَٰوَةُ وَٱلۡبَغۡضَآءُ أَبَدًا حَتَّىٰ تُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ وَحۡدَهُۥٓ... ٤﴾[الممتحنة: 4]

{Haqiqa ya kasance kuma da abun koyi cikin rayuwar Annabi Ibrahim da wadanda suke tare da shi lokacin da suka ce da mutanen su mu babu mu babu ku da abinda kuke bautawa koma bayan Allah kuma mun kafirce muku kuma gaba ta kullu tsakaninmu da ku da kiyayya har sai kunyi imani da shi kadai} [al-Mumtahana: 4], Kuma kayi imani cewa za'a tashi wadanda suke cikin kaburbura, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلۡحَقُّ وَأَنَّهُۥ يُحۡيِ ٱلۡمَوۡتَىٰ وَأَنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٞ ٦ وَأَنَّ ٱلسَّاعَةَ ءَاتِيَةٞ لَّا رَيۡبَ فِيهَا وَأَنَّ ٱللَّهَ يَبۡعَثُ مَن فِي ٱلۡقُبُورِ ٧﴾[الحج: 6-7]

{Wancan ne dõmin lalle Allah Shi ne Gaskiya, kuma lalle ne shi Yake rãyar da matattu, kuma lalle Shi Mai ikon yi ne a kan kõme.(6) Kuma lalle ne Sa'ar Tãshin ¡iyãma mai zuwa ce, bãbu shakka a cikinta kuma lalle ne Allah Yanã tãyar da waɗanda suke a cikin ƙaburbura.(7)} [al-Hajji: 6-7]. Kuma Hisabi da sakamako gaskiya ne, Allah - Madaukakin Sarki - Ya ce:

﴿وَخَلَقَ ٱللَّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ بِٱلۡحَقِّ وَلِتُجۡزَىٰ كُلُّ نَفۡسِۭ بِمَا كَسَبَتۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ ٢٢﴾ [الجاثية: 22]

{Kuma Allah ne Ya halitta sammai da ƙasã sabõda gaskiya, Kuma dõmin a sãka wa kõwane rai da abin da ya sanã'anta, kuma su, bã zã a zãlunce su ba} [al-Jathiya: 22].

Saboda idan ka shaida da wannan shaidawar to haqiqa ka zama musulmi to ya wajaba akan ka bayan haka ka bautawa Allah da abinda Ya shar'anta na Sallah da Zakkah da Azumi da Hajji idan ka samu damar dama yi da wanin hakan.

**Kwafi a ranar 19-11-1441**

**Wanda ya rubuta shi Shi ne Farfesa Muhammad Bn Abdullahi al-Suhaim**

**Babban Malamin koyar da Aqida a bangaren koyar da darussan Musulunci (a da can)**

**Tsangayar koyo da koyarwa, na Jami'ar Sarki Su'ud**

**Riyadh, Kasar Saudi Arabia**

MUSULUNCI..............................................................3

TAQAITACCEN BAYANI GAME DA MUSULUNCI KAMAR YADDA YA ZO A CIKIN QUR'ANI DA SUNNAR MANZON ALLAH ...................................................................3

1-Musulunci shi Saqon Allah zuwa ga mutane baki dayan su shi ne saqon Allah wanzajje...................................................5

2. Kuma Musulunci ba Addinin wasu kebantattun mutane ba ne ko jinsi a'a Addinin Allah ne ga mutane baki dayansu ..........6

3-Musulunci shi ne Saqon Allah wanda ya zo don cika Saqonnin Annabawa da Manzanni wadanda suka gabata -amincin Allah ya tabbata a gare su- zuwa ga al-ummansu ........7

4. Annabawa Amincin Allah a gare su Addininsu daya ne kuma shari'unsu sun sha banban.............................................8

5,Musulunci yana kira -Kamar yadda kowane Annabi yayi: Nuhu da Ibrahim da Musa, da Sulaiman, da Daud, da Isa -amincin Allah a gare su- zuwa ga imani cewa Ubangiji kadai Shi ne Allah wanda Yayi halitta kuma Mai rayawa Mai kashewa Mai Mulki Mamallaki, kuma Shine wanda Yake gudanar da al'amura, kuma Shine Mai jin kai Mai tausasasawa ..................9

6: Allah - Madaukakin Sarki - Shi ne wanda Yayi halitta kuma Shi ne wanda Ya cancanci ibada shi kadai, kuma ba'a bautawa kowa waninsa tare da shi .......................................................15

7: Allah shi ne Mahalicci ga baki dayan halitta abunda muke iya gani da wadan da bama iya gani, kuma duk wani abu da ba shi ba to shi abun halitta ne da cikin halittunSa, kuma shi Ya halicci sammai da kasa cikin kwana shidda ............................22

8-Kuma Allah - Madaukakin sarki - baShi da abokin tarayya a cikin mulkinSa da halittunSa ko bayinSa.................................23

9. Allah - Madaukakin Sarki - bai haifa ba kuma ba'a haifeShi ba kuma baShi wani kini ko mai kamanceceniya da Shi ..........27

10. Allah - Madaukakin Sarki - baYa sauka a cikin wani abu, ko kuma Ya saje da jikin wani abu daga cikin halittunSa .........28

11-Allah - Madaukakin Sarki - Mai rangwame ne kuma Mai jin kai ga bayinSa shi Yasa ya aiko manzanni kuma Ya saukar da litattafai ....................................................................................30

12. Allah Shine Ubangiji Mai jin kai Shi kadai wanda Shine zai yi hisabi ga halittu a ranar Al-qiyama lokacin da zai tashe su baki dayansu daga kaburburansu, saboda Ya sakawa kowanne mutum da aikin da yayi na Al-kairi ko sharri, saboda duk wanda yayi aiki nagari kuma yana mai imani to yana da ni'ama matabbaciya, kuma duk wanda ya kafirta kuma yayi mummunan aiki to yana da azaba mai girma a lahira. ............32

13. Allah - Madaukakin Sarki - Ya halicci dan Adam daga turbaya, kuma Ya sanya zurriyarsa tana yaduwa bayansa, saboda mutane a asalisu daidai suke, kuma babu banbanci a tsakanin jinsi da jinsi ko kuma mutane kan mutane sai da tsoron Allah. ...............................................................................35

14. Kuma kowane yaro ana haifarsa ne akan fidra.............37

15. Kuma babu wani mutum da aka haifeshi da sabo ko ya gaji sabon waninsa ..............................................................38

16. Kuma manufa na halittar mutane ita ce bautar Allah shi kadai ....................................................................................40

17. Musilunci ya karrama mutum -maza da mata- kuma ya dauke masa baki dayan haqqoqinsa, kuma ya sanya shi abun tambaya akan baki dayan sauran zaxuxxukansa, da ayyukansa da kuma Tasarrufinsa, kuma ya dora masa nauyin kowane irin aiki da zai cutar da kansa ko ga wani akansa ..........................40

18. kuma ya Sanya namiji da mace daidai da daidai wajen daukar alhakim aikinsu da kuma sakamako da bada lada .......45

19. Musulunci ya karrama mace, kuma ya sanya mata su zamanto abokan tafiyar maza, kuma ya lazamtawa mazan ciyar da su idan ya kasance yana da iko, saboda haka ya wajaba uba ya ciyar da diyarsa, haka uwa akan danta idan ya kasance ya balaga kuma yana da Iko, haka mata akan mijinta ..................46

20. kuma mutuwa ba karewa bace ta har abada, a'a ita wata tafiya daga gidan aiki zuwa gidan sakamako, kuma mutuwa yana samun jiki da ruhi, mutuwar ruhi ita ce rabuwar ruhi daga jiki, sannan kuma ya dawo zuwa jinkin bayan tashin Al-qiyama, kuma ruhi baya tafiya zuwa wani jikin bayan mutuwa, kuma baya sake tsiruwa a wabi jikin daban ....................................48

21, kuma Musulunci yana kira ne zuwa imani da jigajigan imani manya, kuma shi ne imani da Allah da Mala'ikunsa da imani da litattafan Allah kamar Al-taura da Linjila da Zabura - kafin jirkita su- da kuma Al-qurani, da kuma imani da bai dayan Annabawa da Manzanni -Amincin Allah a gare su- kuma yayi imani da cika makin su shi Annabu Muhammadu Manzon Allah cikamakin Annabawa da Manzanni da Kuma imani da ranar Lahira kuma ya sani cewa rayuwar duniya da ita ce karshe da

kuma da halittu sun zama tsantsar wasa kuma imani da hukuncin Allah da kaddarara ................................................50

22. kuma Annabwa ma'asumai ne -amincin Allah a gare su- cikin abunda suka isar da shi daga Allah, kuma ma'asumai ne ga barin dukkanin abunda ya saba da hankali, ko kuma kyawawan halaye su kyamace shi, kuma Annabawa an dora musu isar da umarnin Allah ga bayinSa, kuma Annabawa basu da wani abu na abunda ya kebanci Allantaka; aa suma mutane kamar sauran mutane Allah Yayi musu wahayi da Manzantakarsa ...........................................................65

23. Kuma Musulunci yana kira zuwa ga bautar Allah Shi kadai da ginshiqan ibada manya, sune Sallah wacce ita ce tsayuwa da ruku'u da sujjada da ambaton Allah da yabonSa da kuma addu'a, kuma mutum yana sallatarta sau biyar a wuni, kuma a cikinta babu banbanci tsakanin mawadaci da talaka da shugaba da kuma talaka a sahu kwara daya a cikin sallah da kuma zakka wacce taje wani yanki ne kadan daga cikin dukiya -daidai da sharadai da kuma gwargwado wanda Allah Ya kaddara,kuma tana wajaba ne a dukiyar mawadata kuma a bada ita ga talakawa da wasunsu, kuma sau daya ce a shekara, da kuma azumi wanda shi ne kamewa ga barin ci da sha da rana a watan azumi, kuma yana koyawa mutum dauriya da haquri, da kuma hajji wanda shi ne: Nufar dakin Allah a Makka mai Alfarma sau daya a rayuwa ga mai Iko wanda zai iya, kuma a cikin wannan hajjin akwai daidaito ga kowa da kowa wajen fuskanta zuwa ga mahalicci – SWT - kuma banbance banbance da nuna wani fifiko duka ya kau a cikin sa. ............................72

24. kuma daga cikin mafi girman abunda ibada ta kebanta da shi a Musulunci cewa yadda ake yinta da lokutanta da sharuddanta Allah – SWT - ne Ya shar'anta ta su kuma Ya isar da ita ga Manzonsa – SAW - kuma babu wani mutum da yayi shigege a cikin su ta hanyar kari ko ragi har zuwa wannan rana, kuma baki dayan manyan ibadu baki dayan Annabwa sunyi kira zuwa gare su - amincin Allah a gare su-.................................77

25, Manzon Musulunci shi ne Muhammad Bn Abdullahi daga cikin zuriyar Annabi Isma'ila dan Annabi Ibrahim - amincin Allah a garesu- an haife shi Makka a shekara ta 571 Miladiyya, kuma yayi hijita zuwa Madina, kuma baiyi tarayya da mutanensa ba a al’amuran bautar gunki, sai dai shi ya kasance yana tarayya da su a ayyukan kirki, kuma ya kasance kan kyawawan halaye tun kafin a aiko shi, kuma mutanensa sun kasance suna kiransa amintacce, kuma Allah Ya aiko shi yayin da ya cika shekara Arba'in kuma Allah Ya karfafe shi da ayoyi (Mu'ajizozi) masu girma, kuma girmansu shi ne Al-qur'ani mai girma, kuma shi ne mafi girman ayoyin Annabawa, kuma shi ne ayoyin Annabwa har zuwa yau din nan, kuma yayin da Allah Ya cika wannan Addinin, kuma Manzon Allah - SAW - ya isar da shi matuqar isarwa sai ya yi wafati she karunsa suna sittin da uku, kuma aka binne shi a garin Madina - SAW - kuma manzon Allah Muhammad - SAW - shine cika makin Annabawa da Manzanni Allah Ya aiko shi da shiriya da Addini na gaskiya don ya fitar da mutane daga duhun bautar gumaka da kafirci da jahilci zuwa hasken kadaita Allah da imani, da kuma Allah Yayi masa shida cewa shi ne ya aiko shi yana mai kira zuwa gare Shi da umarninSa ...........................................................................79

26. Kuma shari'ar Musulunci wacce Manzon Allah Muhammad - SAW - ya zo da ita ita ce cika makin saqonnin Allah da kuma shari'ar Ubangiji; kuma ita ce shari'ar cikawa, kuma a cikinta akwai gyaruwar Addinin mutane da duniyarsu, kuma tana tsarewa a mataki na farko ga Addinin mutane da jininsu da dukiyarsu da hankulansu da zuriyarsu, kuma ta shafe kowa ce shari'a da ta gabace ta na daga shari'u, kamar yadda ta soke bangaren wasun da suka gabaceta. ............................84

27. Kuma Allah - SWT - baya karbar wani Addini in ba Musulunci ba wanda shi ne wanda Annabi Muhammad - SAW - ya zo da shi, kuma duk wanda ya riqi wanin Musulunci Addini to ba za'a karba ba........................................................................86

28. Al-qu'ani mai girma shi ne littafin da Allah Yayi wahayinSa ga Manzo Muhammad - SAW - kuma shi ne zancen Ubangijin talikaia aikowa Manzon Allah - SAW - kuma shi ne zancen Ubangijin talikai wanda Allah Ya qure mutum da aljann kan su zo da kwatankwacin sa, ko sura kwatankawcinsa, kuma har yau qurewa bata qare ba, kuma Al-qurani yana bada amsa muhimmai masu yawa da miliyoyin mutane suka gaza, kuma Al-qurani mai girma abun kiyayewa ne har zuwa yau din nan da yaren larabci da ya sauka da shi, kuma ba'a rage ko harafi daya ba, kuma yana nan a buge ana yada shi, kuma littafi ne mai girma mai gajiyarwa wanda ya dace da a karanta shi ko a karanta fassararsa, kamar yadda Sunnar manzon Allah - SAW - da koyarwarsa da tarihinsa ababan kiyayewa ne kuma ababan rawaito ne daidai da tsanin jerin masu riwaya da aka yarda da su, kuma an buga su da larabci wanda Manzon Allah - SAW - yayi magana da shi, kuma an fassara su da yaruka da yawa,

kuma Al-qur'ani da Sunnar Manzon Allah su ne tushe qwara daya na hukunce-hukuncen Musulunci da shari'unsa, saboda Musulunci, saboda ba'a daukar Musulunci daga aiyukan daidaikun mutane da suke danganta kansu da Musulunci; kawai ana dauka ne daga wahayin Allah a Al-qur'ani mai girma da Sunnar Annabi ..........................................................88

29. Kuma Musulunci yana umarni da kyautatawa iyaye, koda kuwa sun kasance ba musulmai ba ne, kuma ya na wasiyya da 'ya'ya.........................................................................93

30. Musulunci yana umarni da adalci a cikin magana da kuma aiki koda kuwa tare da abokan gaba ne........................98

31, Kuma Musulunci yana umarnini da a kyautatawa halitta baki daya, kuma yana kira zuwa kyawawan halaye, da kuma kyawawan ayyuka...........................................................101

32. Kuma Musulunci yana umarni da kyawawan halaye kamar gaskiya da sauke amana da kuma kamewa da kunya da gwarzanta da karamci da taimakawa mabuqaci da kai gudun mawa ga wanda yake cikin wani hali, da ciyar da mai jin yinwa, da kyautata makwabtaka, da sadar da zumunci, da tausasawa dabbobi ...................................................................102

33. Musulunci ya halatta abubuwa masu dadi na abun ci da sha, kuma yayi umarni da tsarkin zuciya da jiki saboda haka ya halatta aure, Kamar yadda ya umarci Annabawa -Amincin Allah a gare su- da hakan, saboda su suna umarni ne da dukkan abu mai kyau ....................................................................107

34. Musulunci ya haramta dukkan tushen dukkan haramun kamar shirka da bautar gumaka, da shaci fadi ga Allah bada

Ilimi ba, da kashe 'ya'ya da kashe ran da Allah ya haramta, da barna a bayan kasa, da sihiri da alfasha ta fili da ta boye da zina da Liwadi, kuma ya haramta riba, da cin mushe, da abunda aka yanka ga gumaka da dodanni, da kuma cin naman alade, da sauran najasa da kazanta, kuma ya haramta cin dukiyar maraya da tauye mudu da ma'auni, kuma ya haramta yanke zumunci kuma Annabawa -Amincin Allah a gare su- baki dayansu sun hadu kan haramcin wadan nan abubuwan............................109

35. Musulunci ya hana munanan halaye kamar karya da ha'inci da yaudara da ha'inci da danfara, da hassada da mummunan kaidi da sata da zalunci, kuma ya na hana dukkan wani mummunan hali.........................................................115

36. Musulunci ya hana muna nan mua'amalolin kudi waxanda cikinsu akwai riba ko cutarwa ko kuma garari ko zalunci ko algus, ko kuma yana kaiwa zuwa ga masifu, ko cutarwa da zata game baki dayan kasashe da kuma mutane da daidaiku ....................................................................................121

37. Musulunci ya zo da kiyaye hankula da haramta dukkan abunda zai bata shi kamar shan giya, kuma Musulunci ya daga darajar hankali kuma ya sanya shi doron dora nauyi, kuma ya 'yantashi daga dabaibayin taysuniyoyo da bautar gumaka kuma a Musulunci babu wasu boyayyun abubuwa ko hukunce hukunce da suka kebanci wasu mutane koma bayan wasu, kuma baki dayan hukunce-hukuncen sa da shari'unsa sunyi daidai da hankula ingantattu, kuma ita ce daidai da adalci da hikima......124

38. kuma Addinann bata idan mabiyansu basu gamsu da abunda yake cikinsu ba na kwangaba kwanbaya, da al'amuran

da hankali ba zai dauka ba sai malama mabiya Addinin sai su rudi mabiyan da cewa ai Addini sama yake da hankali.kuma cewa hankali ai dole sai da shi wajen fahimtar Addini da kuma riqeshi wanda ko Musulunci ya sanya hankali wani haske ne da yake haskawa hankali hanya; saboda ma'abota Addinan karya sunason mutum ne ya bar hankalinsa ya bi su, kuma Musulunci yana son mutum ne da ya farkar da hankalinsa, don yasan haqiqanin al’amura kamar yadda yake.................................127

39. Musulunci yana girmama ingantaccen ilimi, kuma yana kwadaitarwa kan binciken ilimi wanda yake babu son rai a cikinsa, kuma yana kira zuwa nazari da tunani cikin kawunanmu da kuma halittu da suke kewaye da mu, da kuma sakamakon ilimi ingantacce don ilimi wadanda basa cin karo da Musulunci. ...................................................................128

40. kuma Allah baya karbar aiki ko ya bada lada akansa a lahira sai daga wadanda sukai imani da Allah kuma suka gasgata Manzanninsa -Amincin Allah a gare su- kuma Allah baYa karbar ibadu sai da abunda Ya shar'anta, saboda mai zai sa mutum ya kafircewa Allah kuma ya kaunaci ladansa? kuma Allah baYa karbar imani wani mutum sai idan yayi imani da Annabawa -Amincin Allah a gare su baki daya- Kuma yayi imani da saqon Annabi Muhammad – SAW -. ................................132

41.Lallai manufar sakonnin Allah baki dayansu shi ne: cewa lallai Addinin gaskiya ya daukaka dan Adam, saboda ya kasance tsantsar bawan Allah Ubangijin talikai, kuma ya 'yanta shi daga bautar mutane ko kuma wani abun duniya ko kuma tatsunuyoyi, saboda Musulunci -kamar yadda kake ganinsa-

baya tsarkake mutane ya dagasu sama da matsayinsu, kuma baya sanya su Alloli ababan bauta........................................135

42.Allah Ya shar'anta tuba a Musulunci wanda shi ne maida komai da komai din dan Adam zuwa ga Ubangijinsa, da barin zunubai, kuma Musulunci yana rushe abunda yake kafinsa na zunubai, kuma tuba yana wanke abunda ya gabace shi na zunubai, saboda haka babu wata buqata mutum ace sai ya bayyana laifukansa ga mutane ...........................................137

43.Saboda a cikin Musulunci dangantaka tsakanin mutum da Allah kai tsaye ta ke, saboda haka baka buqatar wani mutum da zai kasance tsani tsakaninka da Allah, saboda Musulunci ya hana mu sanya mutane su zamanto Alloli ko kuma suna tarayya da Allah cikin AllantakarSa da BautarSa...................140

44.A karshen wannan littafin muna tunsarwa cewa mutane duk da sabanin zamaninsu da kabilunsu, da garuruwan su kai baki dayan duniyar mutane sun saba a wajen tunanisu da manufofin su, sun yi hannun riga wajen garuruwansu da ayyukan su, saboda haka suna da buqatar wani mai shiryarwa da zai dorasu kan turba, da wani tasri da hade kansu, da wani jagora da zai kare su, kuma Manzanni -Amincin Allah a gare su-sun jibinci hakan da wahayi daga Allah - Madaukaki - suna shiryar da mutane zuwa hanyar alkairi da shiriya, kuma ya hada su akan shari'ar Allah kuma suna hukunci da gaskiya a tsakaninsu, saboda al’amuransu su tafi daidai dai dai da yadda wadan nan suka amsawa Manzannin, da kuma kusancinsu da wadan nan lokutan na Saqonnin Allah, kuma Allah Ya cika saqonin Manzancin da Manzo Annabi Muhammad - SAW - kuma ya hukunta mata wanzuwa, kuma ya sanyata shiriya ga

mutane da kuma rahama da haske da shiriyarwa zuwa tafarki mai isarwa zuwa ga Allah – SWT -.........................................142

45.Saboda haka nake roqonka ya kai dan Adam ka tsaya ga Allah tsayuwa ta gaskiya kana mai tsiraita kanka daga kwaikwayo da al’ada, kuma kasani cewa kai bayan mutuwarka zaka koma ne zuwa ga Ubangijinka, kuma ka kalli kanka, da kuma wasu sassa da suke kewaye da kai, ka Musulunta zaka rabauta a duniyarka da lahirar ka, idan kuma kana son shiga Musulunci babu abinda zaka yi sai kawai ka shaida cewa Babu abun bauta da gaskiya sai Allah, kuma cewa Annabi Muhammad Manzon Allah ne, kuma kayi watsi da duk abinda ake bautawa koma bayan Allah, kuma kayi imani cewa Allah Zai tashi wadanda suke cikin kabari kuma cewa hisabi da sakamako gaskiya ne, to idan ka shaida da wannan shaidawar to haqiqa ka zama Musulmi, saboda haka bayan haka zaka bautawa Allah da abinda Ya shar'anta na Sallah da Zakka da Azumi, da kuma Hajjatar dakin Allah idan ka samu iko yin hakan, ..........................................................................................143

# Get to Know about Islam

## in More Than 100 Languages

موسوعة الأحاديث النبوية
HadeethEnc.com

**Encyclopedia of the Translations of the Prophetic Hadīths and their Commentaries**

ISLAM HOUSE .com
IslamHouse.com

**A Comprehensive Reference for Introducing Islam in the World's Languages**

موسوعة القرآن الكريم
QuranEnc.com

**Encyclopedia of the Translations of the Meanings and Interpretations of the Noble Qur'an**

ما لا يسع أطفال المسلمين جهله
kids.islamenc.com

**The Platform of What Muslim Children Must Know**

موسوعة المحتوى الإسلامي
IslamEnc.com

**A Selection of the Translated Islamic Content**

بيان الإسلام
byenah.com

**A Simplified Gateway for Introducing Islam and Learning its Rulings**

**Islamic Content Service Association in Languages**

**Da'wah, Guidance, and Community Awareness Association in Rabwah**



978-603-8474-06-8

Ha180